[10/10, 5:26 PM] Rahma Kabir🌺: *Kaɗaici*
12/11/2017

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 1 ~ 2_*

Ranar juma'a babban rana ce ga duk kan musulmai, da misalin ƙarfe biyun rana, Haj. Beeba wacce yaranta suke kira da Momy ce zaune a falo tana kallon tv, tana riƙe da juice mai sanyi a cup tana sha, kana ganinta kasan tana cikin nishaɗi, natsuwa tare da kwanciyar hankali.

Husna ce ta shigo falon tana raɓe-raɓe, cikin tsawa Momy ta soma magana.

"Dan ubanki zo nan, daga aike ki siyo min kati shi ne zaki je ki daɗe haka"

Husna saboda tsananin tsoro kamar zata saki fitsari a wando jikinta ya soma ɓari, idon nan nata kamar zai faɗo ƙasa dan tsoro, cikin inda-inda da sanyin murya ta ce.

"Momy kuɗin ya faɗi ne ina ta nima ban ganshi ba"

Wani irin mummunar ashar Momy ta yi.

"wallahi yau me rabani da ke sai Allah, wato na baki ɗari biyar ki siyo min kati shi ne zaki yar min, toki sani a kuɗin break ɗinki na makaranta, kuma sai na daki kuɗina ƴar iskan yarinya, kina kallo na kamar mayya"

A zabure ta miƙe ta rarimo wayar wuta ta cafkota, ta shiga zuba mata a jiki, Husna ta shi ga ihu kamar ana yankata.

"Dan Allah Momy ki yi haƙuri ba zan sake ba, wallahi ba da gan-gan na yar miki da kuɗinki ba, wayyo Allah Dady na, Momy na ki min rai na tuba"

Dukan ta take yi kamar ta samu kato, Husnah ganin dukan ya yi mata yawa sai ta falla waje a guje tana gunjin kuka, a bayan Baba mai gadi taje ta ɓuya sai sosa jikinta take yi, Momy a sittin ta biyo ta tana sirfa masifa.

"Wallahi yau sai kinci ubanki za kisan kin yar min kuɗi"

"Hajiya dan Allah ki mata haƙuri"

Cewar Baba mai gadi.

"Yi min shuru ba ruwanka, in kuma zaka biya kuɗin data yar min ne sai inji, kuma bani son shishshigi kullun ina ja maka kunne akan haka"

Baba mai gadi yaja bakinsa ya tsuke gudun karya samu matsala a aikinsa, inma da sabo ya kamata ace ya saba da irin wannan abun da Hajiya take yiwa Husna. Haka Momy ta yi masifarta iya yinta, daga bisani ta ce.

"Zaki shigo ciki ki sameni"

ta yi kwafa ta juya cike da mita zuwa falo.

******

Zaune yake cikin harabar gidansa ta wajen gate, zaune yake cikin wata ruffa mai ɗauke da fararen kujeru uku da table a tsakiya, iska yana hura shi, da ganin alama yana jin daɗin wannan yanayin da yake ciki, ihun Husna daya ji ne duk sai ya ji hankalinsa ya tashi, ransa ya dagule har wani ajiyar zuciya yake yi. Kasantuwar gidansa yana jikin gidansu Husna maƙota suke, duk abin da ke faruwa a cikin gidansu Husna yana ji in dai yana cikin gidan bai fita. Yau ma dawowarsa kenan daga masallacin juma'a sai ya ji sha'awa zama a gurin dan ɗebe masa kewar iyayensa, kasancewar shi kaɗai yake rayuwa a cikin wannan gida, tsaki yaja yana mai jinjina kansa.

"Wannan wace irin azzalumar mace ce? Haka nan kita azabtar da yaranki, tir da hali irin naki"

Ya ce a fili tare da ɗaukar ruwa ya kurɓa dan ya ji sauƙin raɗaɗin da zuciyarsa ke masa. Haka nan yake jin tausayin Husna saboda kusan kullun sai ya ji kukanta, hakan yana matuƙar ɓata masa rai da sanya shi damuwa, wata rana har a cikin barcinsa yana jin kukanta yana masa guzo. Miƙewa ya yi tsaye ya ɗauki key motarsa ya fice daga gidan a fusace, ko ƙila zai samu sauƙin raɗaɗin da zuciyarsa ke yi masa.

******

Baba mai gadi ya zaunar da Husna a gefensa ya ce cikin lallashi.

"Husna meyasa kika zubar mata da kuɗi? Kuma kinsan halin Mominki bata raga miki ko kaɗan"

"Uhum uhum um, Baba ba da gan-gan na zubar ba, wunya nake ji banci komai ba kuma ta aikeni, kaga ko uniform bata bari na cire ba, ni kuma da kyar nake tafiya saboda wunya nake ji, shi ne na tsaya na huta a wani dakali, barci ne ya fara ɗaukata daga nan kuma sai banga kuɗin ba"

Ta ce cikin sassheƙar kuma. Baba mai gadi shuru ya yi yana tunanin halin da take ciki yarinya ƙarama wacce a yanzu bata wuce shekara bakwai ba a duniya. Shekarunsa uku da fara aiki a

gidan, amma kullun a cikin  *kaɗaici* Husna take da takura, tsangwama da hantara, har yanzu abu bai chanza zani ba.

'Ya Allah ka fidda yarinyar nan daga wannan ƙangi'

Ya ce a cikin ransa cike da damuwa. Sai ya miƙe ya shiga ɗakinsa ya ɗauko mata sauran abincin da ya rage mata, dama kusan kullun duk abin da ya ci yana rage mata, saboda ba sosai Momy take bata abinci ba. Cikin sauri ta karba abincin jikinta na rawa ta soma ci, bayan ta kammala tasha ruwa, nan take gumi ya fara karyo mata alamar ta ƙoshi.

"Tashi ki je ki cire uniform ɗinki sai ki dawo in miki karatu"

Cewar Baba yana mata murmushi, cikin jin daɗi Husna ta miƙe ta wuce cikin gida. Ta samu babu kowa a falon, cikin sanɗa ta shige ɗakinta, uniform ta soma cirewa ta sanya doguwar rigar atamfa, sai ta shiga toilet ta yi fitsari sannan ta fito, kayan wankinta ne jibge a gefen gadonta, ta zauna gefen gadon ta rafka tagumi kamar wata babbar mace, hawaye ya shiga kwaranya a kuncinta, ta shiga rera kuka babu mai lallashinta, in da sabo ta saba da wannan rayuwa, saboda kullun cikin *kaɗaici* take, Momy sam bata ƙaunarta balle ta kula da ɗawainiyarta.

Tana cikin wannan yanayin ne sai ta ji an turo mata ƙofa, da sauri ta kalli ƙofar dan ganin wanda ya shigo, Momy ce tsaye tana mata kallon uku saura kwata, jikin Husna ya ɗauki rawa ta miƙe tana kama jikinta.

"Yanzu ai ga shi kin shigo hannuna ko, amma na kyale ki tunda ko banza kin daku, sai dai zan ja miki kunne in Dady ɗinki ya dawo karki kuskura in ganki a falo, dan inna ganki wallahi sai jikinki ya gaya miki. Sannan maza ki je ki min wanke-wanke gasu can na fitar miki da shi ta bayan kitchen, kuma ki wanke min su da kyau, da fatan kina ji na?"

Cewar Mamy cikin faɗa.

"Eh Momy"

Ta ce a tsorace, Momy sai ta wuce, ita kuma Husna ta biyo bayanta dan yin aikin data sanya ta.

******

Momy tana zaune a falo ita da d'anta Nura, suna kallon wani series film a tashar zee word, sallamar Dady ne ya katse musu kallon cikin farin ciki Momy ta mike.

"Barka da dawo wa Alhaji"

"Yauwa uwar gida, na same ku lafiya?"

"Lafiya lau"

Sai ya samu guri ya zauna, Nura ya yi masa sannu da zuwa, ya amsa cike da kulawa ya kara da cewa.

"Ya makaranta? Da fatan kana maida hankali"

"Eh Dady ina maidawa sosai gobe zamu fara text"

"Da kyau, masha Allah, Allah ya taimaka"

"Ameen Dady"

Dady ya kai dubansa ga Momy yana dan murmushi ya ce.

"Hajiya wai ina Husnah ta ke? Ba dai har ta yi barci ba?"

"Ai kasan ita kasa ce akwai saurin barci da ta ci abinci shi kenan"

"Ikon Allah, ita kullun bana samun had'uwa da ita, inna dawo ta yi barci lokacin fitana kuma tana barci, gaskiya bari dai yau na duba ta dan rabon da in sanyata a idona yafi sati biyu fa"

Cikin hanzari ya mike zai nufi d'akinta, da sauri Momy ta tari gabansa cike da kissa.

"Haba dear yanzu fa ka dawo ko wanka baka yi ba balle cin abinci, ka bari in ka natsa sai ka je ka ganta din"

Murmushi ya yi ya ce. "Hakane to muje inna kammala naje naga Mamana kar ta yi fushi dani"

Haka suka tafi ba tare da yaje ganin Husnan ba. Ta bangaren Husnah tana zaune a d'aki gefen gadon a takure kamar 'yar tsako, sai kalle-kalle take yi jikin nan nata cud'u-cud'u babu wanka balle ma tasan ya za ta yi Alwala da sallah, Momy ce ta shigo dakin, a zabure Husna ta mike tana kallonta cikin tsoro, motmy ta yi mata wani mugun kallo wanda ya ke kada mata hanjin ciki

"To dare ya yi me kike jira baki yi barci ba? ga Dady ya dawo maza ki kwanta, kuma yanzu zai shigo karki kuskura ya gane ba barci kike ba, in ba haka ba wallahi jikin ki zai gaya miki, kwanta in gani"

Da sauri ta koma ta kwanta ta bama Momy baya, Momy ta jawo wani bargo ta yafa mata a jiki ta kashe wutan dakin ta fice.

Dady ne sanye cikin jallabiya milk color, yana tafiya Hajiya na biye da shi a baya, har suka isa dakin Husna, ya ce.

"Hajiya kunna mana wutan dakin"

Nan take ta kunna haske ya gauraye dakin, Momy na cewa

"Ai tun dazu na leko na kashe mata dan naga ta yi nisa a barcin"

Dady ya shiga bin d'akin da kallo, ya mance yaushe rabonsa daya  shigo ciki, cikin damuwa ya kalli Hajiya.

"Lafiya naga d'akin nata a hargitse sai tashin warin datti yake yi"

Ya kai kallonsa ga inda ta jibge kayan wankinta.

"Wancen kuma kayan na meye a gun?"

"Alhaji kayan datti ne, kaga dare ya yi muje mu kwanta gobe za mu yi magana"

Cewar Hajiya cike da fad'uwar gaba, Dady ya bita da kallon da tuhuma, yana son ya karanto wasu abubuwa a tattare da ita, Hajiya dakewa ta yi kamar mai gaskiya, girgiza kai ya yi ya fice ba tare da ya ce komai ba, ita ma bin bayansa ta yi jiki a sanyaye. Suna fita Husna ta bi kofar da kallo tana mai zubda hawaye, kiri-kiri a na son rabata da mahaifinta mai sonta, a haka har barci ya yi awon gaba da ita.

****
*Da safe*

Ta farka bata san ta yi  wanka ba da brush, balle ta san ta yi alwala da sallah. Ta fita babban falon ba kowa sai Jimmai mai aikinsu da take kicin, shiga ta yi ta sameta tana had'a musu breakfast.

"Husnan Momy kin tashi?"

"Eh Mama na tashi"

Da yake haka take kiranta, ta cigaba da cewa.

"Shi ne rannan kika tafi kika barni kin dad'e baki dawo ba sai yau"

Ta ce cike da shagwaba, Jimmai dariya ta yi.

"Baba 'yar Momy shi ne kamar za ki yi kuka, ai gani na dawo, ki kwantar da hankalinki ba zan sake tafiya in dad'e haka ba kin ji"

Ta gyad'a mata kai alamar ta gamsu, sai ta fita daga kicin din tabar Jimmai. Wurin Baba mai gadi ta wuce tana dariya, ta sameshi zaune akan benci yana jin radio, tana ganinta ya washe jajayen hakoransa wanda ya dafe da goro.

"Husna yar Baba kin tashi kenan"

"Eh Baba, ka rage min kunu da kosai na?"

"Husnah kenan, kununki yana nan a d'aki shiga ki d'auko kisha da kosan"

Ya ce yana murmushi, cikin jin dad'i ta nufi d'akin Baba ta d'auko ta dawo kusa da shita zauna, ta soma ci cikin nutsuwa da santi.

Dady ne ke zagaye gidan dan shan hantsi, ya hango Husna gurin mai gadi sai hakan ya ba shi mamaki, ya shiga tambayar kansa.

'Me take yi a gurinsa da safen nan?'

Da sauri ya katse tunaninsa ya karaso kusa dasu ya ce cikin daga murya

"Husna, Husnahhh, me kike yi a gurin nan maza zo nan"

Cikin sanyin jiki ta aje kunun da take sha da kosai, ta isa gurin Dady ta tsaya tana kallonsa, shima binta da kallo ya yi duk ta fita hayyacinta, gaba d'aya ta bushe ta rame sai hasken wahala ta kara, ya kai kallonta ga kanta wanda yake ba d'an kwali, gashinta ya dankare da datti ko layin kitson ba a gani saboda daud'a, mamaki ne ya cika shi, sai ya kiran mai gadi, cikin sassarfa ya zo ya ce

"Barka da safiya yallabai ya kwanan Iyalin?"

Dady bai amsa masa ba sai ma murtike fuska da ya yi.

"Karna sake gani cewa ka bama Husna abu tana ci, ban yarda ba kuma ban amince ba, da fatan ka jini"

Jiki na rawa ya ce.

"Insha Allah yallabai zan kiyaye"

"Tashi ka tafi"

Jikinsa ba kwari ya mike ya tafi.

"Je kuma mu je ciki"

Dady ya yi maganar yana kallon husna, sai tabi bayansa tanakama jikinta. Momy ce zaune a falo tana waya, da alama magana take yi daa kawarta.

"Hajiya Uwani dan Allah ki bani mafita, wallahi tunda Alhaji yaga d'akin Yarinyar nan yake tuhumata na rasa me zance masa, ina tsoron ya kuma tambayata dan banda amsa"

Haj. Uwani ta kwashe da dariya.

"Haba Haj. habee karki bani kunya mana, sai kaceba uwar makirci,I ba, akan karamar alhaki kin tada hankalinki"

"To ya zanyi Hajiya kin san fa Alhaji na mugun son ta dole in tashi tsaye fa"

"To ki kwantar da hankalinki kar kiji komai, ina ga ma ba sai kin yi asarar kudi zuwa wurin boka ba, ki yi amfani da kissar ki da makirci kawai"

"To Hajiya me kike ganin zanyi ba tare dana samu matsala ba"

"Me zaki mata wanda ya wuce ki daura mata cutar Hauka"

"Hauka fa Hajiya? taya hakan zai yuwu?"

"Hahaha Haj. Habee kina bani mamaki kinbi kin damu kanki, dan Allah karki bani kunya mana"

Nan ta cigaba da jero mata yanda zata yi makirci cikin dubara da mugunta, har sai da Momy ta gamsu. Sun cigaba da tattaunawa, sai ga Dady ya shigo Husna na biye da shi a baya, fuskar shi ba annuri a murtuke, da sauri Momy ta katse wayar gabanta na fad'uwa, ta ce a zuciyarta..

'Allah yasa mai gadi bai min katsalan dan ya gayawa Alhaji abin da nakewa Husna'

Yanda taga yanayin Alhaji shi ne ya kara birkita mata ciki, duk iya makirci da asirin da take takama dasu tana mugun shakkar Dady, saboda baya yi mata da wasa, binsu ta yi da kallo har suka zauna.

Dady ya ce "...

*Rahma ce*
[10/12, 3:15 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 3 ~ 4_*

Dady ya ce.
"Hajiya jiya na tambaye ki akan Husna amma kin min shuru, wai me yake faruwa ne? ji jikin yarinya yadda duk ta lalace, ta zama kamar wacce ba tada galihu, ji kanta kamar kitson da ya yi shekara, anya Hajiya kin kasance mai amana kuwa?"

A kid'ime Momy ta ce

"Haba Alhaji me kake nufi dani ne? duk irin ƙoƙarin da nake yi da Husna, yarinyar da..."

"Dakata! bance ki gaya min shirme ba, gaskiyar magana nake son ji"

Hajiya ta fara kukan kissa.

"Alhaji baka yarda dani ba kenan, wallahi in kaga yadda nake fama da Husna sai ka yi mamaki, kayan wankinta da kaina nake wanke mata amma yarinyar nan ta ce bata so, kitso kuwa da dambe ake mata, in na bata abinci sai ta zubar ta ce baza ta ci ba, wanka ko har cizona take yi wai bata so.

Alhaji ni ce Husna take zagi, kuma ban isa in sata abu ba sai taƙi yi, ba zan yiwa mata sharri ba ran nan cewa ta yi ai bani ce uwarta ba, dan haka karna sake yi mata wanka, na rasa ta ina tasan bani ce na haifeta ba"

Ta ƙarasa maganar tana kuka. Husna dai na zaune tana jin ƙarairayin da Momy ke yi akanta, wanda wasu ma bata iya gane su ba, Alhaji jikinsa ya yi sanyi.

"Yanzu Habeeba duk wannan abu yana faruwa shi ne zaki yi shuru ba zaki sanar min ba, gaskiya baki kyauta min ba, haka zaki zuba mata ido ba tare da d'aukar mataki ba"

Wani farin ciki ne Momy taji ya lullub'eta amma sai ta b'oye hakan, ta ce.

"Alhaji abin da yasa ban gaya maka, ina ganin ai Husna yarinya ce zata daina nan gaba, kuma wasu lokutan ina mamaki yanda take yin wasu abubuwa, zama shuru-shuru, kullun ita kad'ai a d'aki, yawan surutai ita kad'ai, hakanan kaga tana soshe-soshe kamar wacce take da taɓin hankali, hakan yasa nake ganin bai kamata na ɗauki hukunci ba, ba tare da tabbatacin sanin halin da take ciki ba, dan mutum mai lafiya ba zai yi haka ba"

Ta ƙara maganar cike da damuwa a fuskarta, Dady ya shiga itashin hankali.

"Amma shi ne baki taɓa sanar min ba?"

"To Alhaji banda tabbacin hakan shiyasa ban gaya maka ba, na jira ne naga in abun ya fara yawa in sanar maka sai mu tafi asibiti"

"Ikon Allah, to ai yanzu ba shuru zamu yi ba, dole mu tafi asibiti dan a duba lafiyar kwakwalwarta, ba za mu bari abun ya cigaba da tafiya ba, kar yazo ya sha k'arfin mu"

"Hakane Alhaji, to mu bari zuwa Monday in Allah ta kaimu sai muje muga likita, in yaso koni na kaita saboda yanayin aikinka"

"Anya Hajiya? ina ga tare zamu dan hankalina bai kwanta ba"

"Haba Alhaji wannan abu ba wani babba bane, ai ko ni zan iya komai akai, karka damu insha Allah ba wata matsala ba ce"

"To shi kenan tunda kin ce haka Allah ya kaimu Monday ɗin"

"Ameen"

Sai ya kalli Husna wanda ta takure gefe d'aya kanta na ƙasa duk tana sauraren su, sai dai bata fahimci inda zancen iyayenta ya dosa ba, sai wasa take da yatsun hannunta, Dady ya dafa kanta.

"Allah sarki Mamana, Allah ya baki lafiya"

Duk suka amsa da amin.

"Hajiya ayi ƙoƙari a gyara mata d'aki sannan ayi mata wanka, a kwance kannan nata a wanke sai a mata kitso"

"Ba komai Alhaji insha Allah za'a yi mata"

Dady ya miƙe ya wuce part d'insa Momy tabi bayansa da harara tare da tab'e baki, yana shigewa ta fara wani munafikin dariya, nan ta kwalawa mai aikinta kira, da sauri ta ƙaraso.

"Gani Hajiya"

"Yauwa ga Husna nan ki je ɗakinta ki gyara, kayan wankin ki fito dasu ki wanke, sai ki mata wanka tare da yi mata kitso, ai kin iya ko?"

"Eh na iya"

"Yauwa ki maza, in kin kammala sai ki wuce"

"To Hajiya nagode"

***
A cikin kwana biyu Husnah ta samu sauyi kamar ba ita ba, kasantuwar ko da can dama Jimmai ita ke kula da ita, Momy ce ma ke hanata yi mata wasu abun, amma duk da haka takan bata abinci a sace, ta yi mata wanka da wanki ba tare da sanin Momy ba.

*****      ******

*Monday*
Tushen aiki ko bature yana tsoransa. Momy ce ta fito cikin shirin zuwa asibiti, ga Husna wacce Jimmai ta gyarata cikin riga da siket na atamfa, sai ɗankwali da aka ɗaura mata, ba laifi ta yi kyau, Momy na gaba tana biye da ita a baya, motarta ta d'auka ta buɗe mata mazaunin kusa da driver, Jimmai ta zaunar da ita, sannan mai gadi ya buɗe mata gate suka wuce asibiti.

Da isar su ta yi parking suka fito ta kama hannun Husna kamar abun arziki suka shiga cikin asibitin, bayan an fito musu da folder ɗinsu suka zauna zaman jiran likita, ba'a d'au lokaci ba suka shiga.

Momy ta samu kujera ta zauna tana fuskantar likita, suka gaisa da Dr. Ismail.

"Hajiya meye matsalar ki?"

Momy sai da ta d'an jinjina maganar da zata yi saboda yadda taga Dr. Ismail kamar ba zai yi mata abin da take buƙata ba, ta nisa kana ta soma bayani.

"Likita wani alfarma nake nima, sannan ko nawa kake buƙata zan baka"

Cike da mamaki Dr. Ismail ya ce.

"Hajiya ban fahimce ki ba?"

Ta murmusa ta ce. "Yanzu zan fahimtar da kai, wannan yarinyar ƴar mijina ce, to a gaskiya tunda na soma riƙonta nake yawan samun matsala da shi akan ta, to yanzu gaskiya ina son in ɗanyi wani abu yadda zai rage sanya min ido a kanta"

Dr. Ismail ya katseta da cewa.

"Ai wannan abin da ya shafi family ne bai shafe ni ba"

"Likita ka yi haƙuri ka saurareni dan kuwa ya shafe ka. Ina so ka taimaka min don Allah in akwai

wata allura ko magani daya ke sanya mutum k'aramar hauka ka yi mata, sannan ka yi rubutu akan cewa ta samu taɓin hankali amma ba mai yawa ba, sai na riƙa kawo ta kana dubata kana kuma ƙara mana maganin"

Cike da tashin hankali Dr. Ismail yake kallon ta amma sai ya danne hakan a ransa, a fili kuma ya gyara zaman tabarau sa ya tamke fuska, ya fara zazzaga mata masifa daga bisani ya daka mata tsawa da ta fita masa a office, cikin damuwa Momy ta kalle shi.

"Haba Dr. Ismail kamar baka sanni ba, kai ne fa Likitanmu, amma ka kasa min wannan taimakon, na ce zan biya ka ko nawa kake so wallahi"

Bai ce mata komai ba face ya nuna mata hanyar waje da ta fita. Cike da masifa ta miki ta ja tsaki.

"Dz kuɗina ai ko zan samu biyan buƙata, zan je inda za ayi min kuma burina ya cika"

Sai ta fice tana jan hannunta Husna. Hankalin Dr. Ismail ba ƙaramin tashi ya yi ba, cike da damuwa ya soma tuna yanda yaga Husna.

'Yarinya ƙarama abin tausayi ana niman sabauta mata rayuwa, hakanan a d'aura mata lalura saboda zalunci'

Ganin yadda Hajiya ta fusata ba imani a tare da ita zata iya aikata komai akan burinta ya cika, yasa ya yi sauri ya kira nursing station, wata nurse ta d'auka ya yi mata umarnin da ta kira masa matar da ta fita office d'insa yanzu da ta dawo. Momy harta kai gun mota cike da damuwa tana tunanin wani asibiti zata, sai ga wata nurse ta ƙaraso da gudu ta ce.

"Hajiya Doctor ya ce ki dawo yana son magana dake"

Cike da jin da ɗi ta ce.
"Ok nagode"

A ranta kuma ta ce.

"Ɗan iskan Allah yasa ya amince da ƙudurina"

Bayan ta isa office d'in, ta samu guri ta zauna tana kallonsa fuska ba fara'a, Dr. Ismail ya cire tabarau kana ya nisa kana.

"Hajiya na yi dogon tunanin akan buƙatar ki, wanda daga bisani naga ya dace na yi miki hakan tunda an zama d'aya, yanzu dai a kwai maganin da zan bata, a yau d'in nan zai fara aikinsa, sai dai a hankali a hankali zai yi aiki a jikinta, sai bayan sati d'aya kuma sai ku dawo sannan na sake bata wani, shi kenan kuma ba sai an k'ara bata ba"

Cike da farin ciki Momy ta ce.

"Nagode Doctor Allah ya saka da alkhairi"

Bai ce mata komai ba ya miƙe ya fita, bai ɓata lokaci ba ya dawo riƙe da magani a hannun sa har kwaya uku, ya ce.

"Hajiya ya sunanta?"

"Husna"

"Ok, Husna zo nan kusa"

Jiki a sanyaye ta matsa kusa da shi, ya d'auko wani gorar ruwa ya zuba a wani cup sannan ya bata wannan maganin kwaya uku ta had'iya da ruwa, da kyar ta iya sha saboda bata son magani, taji kamar zata yi amai sai ta soma yunƙuri, Momy ta fizgo ta ta ce.

"Idan kika kuskura kika amayar da maganin nan wallahi sai na kusan halakaki tsinanniyar yarinya"

Husna ta fara kuka, Momy ta sakar mata wani wawan mari kad'an ya rage ta saki ihu dan tsananin azaba.

"Dan ubanki zaki min shuru ko saina ƙara miki"

Tuni ta shiga taitayinta ta kama bakinta, sai hawaye ke malala a kuncinta, Dr. Ismail dai yana kalon ikon Allah, a ransa ya ce.

"Allah ya saka miki hutsna"

A fili kuma ya ce.
"Hajiya wannan maganin dana bata zai kawo mata canji sosai, da farko zata yi barci mai nauyi, sannan na biyu tana farkawa zata buƙaci abinci kuma zata ci abinci sosai, sannan na uku zata zama silent sosai fiye da da, dan haka sai ki tabbatar da in ta farka a bata abinci mai kyau, sannan a riƙa sanya ta barci da wuri, shi kenan buƙata ta biya"

Cike da murna Momy ta yi masa godiya kana ta ciro bandir ɗin dubu d'aya ta aje masa kan table, Dr. Ismail ya yi murmushi ya ce.

"Hajiya wannan kud'in sunyi yawa"

Ya d'auka ya zari guda biyar ya mi'ka mata sauran tare da yi mata godiya.

"Haba Doctor kafi ƙarfin haka a guna da ka barshi"

"A'a Hajiya mutunci ai yafi kud'i wannan dana d'iba sunyi"

"To shi kenan nagode kwarai Allah ya bar zumunci"

"Ameen Hajiya nima nagode"

Sannan ya miƙa mata takardar sakamakon gwajin ƙaryan da suka yi,  sai ta miƙe ta kama hannun Husna suka wuce.

Da fitarsu Doctor ya kira wayar nursing station ya yi umarni da d'aya daga cikinsu ta zo, bayan ta ƙaraso ta gaishe shi ya amsa tare da miƙa mata kuɗin daya kaɓba na Hajiya ya ce suje su raba, ta amsa cike da murna ta yi masa godiya sannan ta wuce.

A kan hanya Husna ta soma barci, hakan yasa Momy ta yi parking mota a bakin hanya ta gyara mata kwanciya, sannan ta kira Haj. Uwani ta shaida mata duk abin da ake ciki, hira suka yi sosai cike da farin ciki kana suka yi sallama.

Husnah tun ƙarfe sha biyun rana take barci bata farka ba sai ƙarfe hud'u na yamma, ta fito falo taga Momy tare da Yaya Nura suna kallo a TV, ta tsaya tana kallonsu bata ƙarasa cikin falon ba, saboda gudun karta jawo wa kanta duka, Momy cikin fara'a ta ce.

"Su Husna an tashi kenan"

Sai ta kwalawa Jimmai kira, cikin sauri ta zo.

"Abinci zaki kawowa Husna, yanzu ta tashi barci"

Ta amsa sai ta koma kicin ta d'ibo abinci a plate da kofin ruwa ta kawo mata, Husna har Allah-Allah take a kawo mata saboda mugun yunwar da ke damunta, ta zauna nesa dasu Momy ta jawo plate ɗin ta soma ci ba ƙaƙƙautawa, Momy tana yi tana satar kallonta, farin ciki ne fal cikinta saboda duk bayanin da Doctor ya yi mata gasu suna bayyana, Nura yana gefe yana kallon yanda take cin abincin hannu baka hannu kwarya, sai ya daka mata tsawa.

"Ke baki da hankali ne? ji yanda kike cin abinci kamar tsohuwar manya, ki ci a hankali mana bamai kwace miki"

"Rabu ta ita mana ai mai hankali ba zai yi haka ba, baka san tanada taɓin hankali ba, ɗazun nan muka dawo daga asibiti, kuma bincike ya nuna kwakwalwarta ta taɓu"

Cewar Momy.

"Haba biri ya yi kama da mutum ji fa yadda take cin abinci, lallai a kwai alamun hauka, shegiya mai siffar mayu"

Dariya Momy ta yi. "Kai my Son wallahi ka bani dariya, ai na ƙosa Alhaji ya dawo muga ta ƙarshen so, ƴar daya kwallafawa rai gata dai ta zama mahaukaciya"

Jimmai duk tana jinsu zuciyarta tana yi mata ƙuna.

'Allah ya maida muku da mugun nufinku, haka kawai kuna niman ɗaura mata hauka, duk zaluncin da kike mata bai isheki ba sai kin yi mata wani sharrin, yarinya ƙarama haka kawai ki ɗaura kishi akanta saboda rashin tunani, Allah yasa ki gane'

Tana cikin zancen zuci ta ji Momy ta ƙara kwala mata kira, da sauri taje.

"Ki ƙara zuba mata wani abincin"

Ta karɓa plate ɗin ta tafi kicin da mamaki ta ƙara ɗiban abincin ta kawo mata. A taƙaice dai Husnah sai da taci abinci har plate uku sannan ta d'aura da ruwa, cikin nan nata ya yi ƙato da kyar take tafiya, haka ta ratsa ta cikin falon ta wuce wurin Baba mai gadi sai nishi take yi.

Baba na ganinta, ya ce "Husnah yau kinyi shuru a cikin gida kamar baki nan, hala barci kika yi?"

Ta gyaɗa masa kai alaman eh, daya ke ita ba gwanar yin magana bace.

"Baba cikina ya cika sosai, ka bani kuɗi inje in siyo chewing gum"

Baba ya yi dariya.
"Da alama kin yi mugun ci ko, ji yanda kike ta nishi kamar kin hiɗiye dutse, waye ya ce ki yi mugun ci? To ba zan baki komai ba"

"Dan Allah Baba ka bani zanci ne"

Ta ce cikin shagwaɓa.

"Husna bani son rigima, ga naira goma je ki siyo amma ki kula da hanya kuma karki dad'e"

Kai ta gyada mai sannan ta fita da sauri.

*****
Sadiq ya dawo daga aiki kenan yana ƙoƙarin bud'e gate dan ya shiga da motar sa, ya hangota tana tafiya a nutse, kafeta da ido ya yi a ransa ya ce.

'Duk yadda aka yi wannan yarinyar ita ce Husna, ko ina zata kuma?'

Haka ta zo ta wuce shi yana binta da kallo, ya gyara tsayuwarsa ya jingina da mota yana jiran dawowarta, wani shago taje wanda yake saman layinsu, ta siya chewing gum na naira goma sannan ta juwo gida, ta zo zata wuce shi sai ya kirata, ta  kalle shi cike da tsoro ta maƙe kafaɗar ta alamar taƙi, tA juya ta cigaba da tafiya, ganin zata wuce shi yasa ya kirata da sunanta.

"Husnahhh"

Cak ta tsaya ta juyo, ya ƙaraso kusa da ita ya tsugunna.

"Me kika siyo ne?"

Sai ta nuna masa chewing gum d'in, ba tare da ta ce komai ba ya yi mata murmushi.

"To tsammin zanci"

Ita ma murmushi ta yi sai ta miƴa masa, ya karɓa ya ce.

"Naki ne duka?"

Ta gyaɗa masa kai alamar eh, sai ya shiga buɗewa ya b'alla rabi ya mi'ƙa mata rabin.

"Ashe ba ki da rowa, to ya sunan ki?"

A nan ne ta buɗe baki ta yi magana.

"Husna khalil"

"Masha Allah suna mai kyau, ni sunana Sadiq Aliyu, kin yarda na zama abokinki?"

Ta gyaɗa masa kai alamar ta yarda, murmushi ya mata ya kamo hannun ta suka ƙulla abota sannan ya nuna mata gidansa, ta yi murmushi wanda ya bayyana kyawunta sosai, sai ya amsa chewing gum ɗinta ya sanya mata a baki, ta soma taunawa shima ya sanya na shi a baki ya fara ci tare yin murmushi.

"Kinga daga yau mun zama abokai, my Husna Allah ya yi miki albarka"

"Ameen uncle"

Sannan sai ta juya ta wuce gida, Sadiq ya bota da kallo har ta shiga gida, haka kawai yaji ƙaunar yarinyar yana ratsa shi, ya koma ya shiga da mota cike da farin ciki, da murnar yaji kwana biyu an rage dukanta. Wannan shi ne Sadiq d'an gidan Alhaji Aliyu mai kanti.

*Rahma ce*
[10/12, 4:48 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 5 ~ 6_*

Daddy ya dawo da misalin ƙarfe tara na dare, bai samu kowa a falo ya wucr ɗakinsa ya watsa ruwa ya fito sanye da jallabiya brown color, ɗakin Momy ya nufa ya sameta kwance tana kallon wani film, da sauri ta tashi zaune ta yi masa sannu da zuwa.

"Muje abincin ka yana dinning"

"A'a bana buƙatar abinci yanzu, Hajiya ina son sanin halin da Husna ke ciki, me likita ya ce?"

Momy ta d'anyi jim kana ta soma magana.

"Alhaji ka yi haƙuri ka fara cin abinci tukunna, in ka kammala saina sanar maka"

"Bana jin zan iya shan koda ruwa ne ba tare da sanin lafiyar ta ba"

Ya ce cike sa damuwa a fuskarsa. Momy ta cika da jin haushi amma sai ta basar ta mik'e ta ɗauko masa result ɗin da Dr. Ismail ya bata, ta ba shi labarin duk ƙaryar data shirya, Dady ya shiga karanta result ɗin, jikinsa ne ya mutu tare da tsantsar tashin hankali daya bayyana a fuskarsa, gumi ne ya gangaro masa, yana fad'ar.

"Innalillahi wa inna ilai hir raji'un"

Ya dafe goshonsa yana jijjaga shi saboda nauyin da kansa ya yi masa.

'Zainab kin yi nesa dani, ga ɗiyarmu cikin wani hali, banda halin zuwa inda kike, Husna tana buƙatar taimakonki'

Ya yi zancen zuci hawaye yana gangaro masa a kuncinsa, ya dafe k'irjinsa saboda nauyin da zuciyarsa ya yi masa. Momy ta zuba masa ido tana mamakin yadda Dady ya shiga damuwa sosai, sam bata yi zaton zai damu haka ba, nan take ranta ya kuma b'aci, ta k'ara jin tsanar Husna a zuciyarta.

Dady ya miƙe yana jan ɗafarsa da kyar ya isa ɗakinsa, Momy ta miƙe tana biye da shi tana ba

shi baki da lallashi, ya zauna gefen gado ya d'auki wayarsa ya danna number Dr. Ismail.

A can b'angaren Doctor kuwa a ranar ya wuni yana damuwa akan lamarin Husna, yanzu ma zaune yake a kujera matarsa Amina ta sanya shi gaba tana tambayarsa abin da ke damunsa, sai ga wayar Dady ya shigo, cike da tashin hankali ya d'auki wayar yana shakkar abin da zai gaya masa, in da ya samu sassauci ma daya tuna basu tab'a had'uwa ba sai waya kawai ke had'asu, in iyalinsa basu da lafiya ya turo su gunsa. Da sallam ya d'auka suka gaisa, yanayin yadda yaji muryan Alhaji yaji faɗuwan gaba, Daddy ya ce.

"D'azun iyalina sun zo wurinka kan batun lafiyar Husna, na kira ka ne ka tabbatar min da result d'in dana gani"

Ya k'are maganar kamar zai yi kuka. Doctor Ismail ji ya yi kamar ya shige k'asa dan tashin hankali, sai kawai ya dan ne zuciyarsa.

"Kwarai wannan sakamakon da muka samu kenan, amma insha Allah zata samu lafiya ba wai wani serious case bane"

"To shi kenan, don Allah ka bata duk kulan duk da daya kamata. Nagode"

Nan suka yi sallama suka aje kan wayar, Dr. Ismaili ya sauke wani nannauyar ajiyar zuciya, hakan yasa Amina ta ɗago ta kalle shi wanda duk wayan da ya yi tana jinsa.

"Abban Khadija da ganin alamu damuwar ka yana tattare da wannan wayar daka yi, don Allah ka sanar min abin da ke damunka"

"Ameena yau na tsinci kaina cikin damuwa sanadin k'aryan dana yi da aiki na, a gaskiya na zama maƙaryaci kuma mayaudari"

"Haba Abban Kamal meyasa kake wannan furucin? Ina so ka warware min abin da kake ciki"

Ta ce cike sa tashin hankali. Ya nisa ya shiga bata labarin duk abin da ya faru tsakaninsa da Momy, Ameena ta yi salati tare da tafa hannu.

"Oh ni Ameenatu ashe har yau ana samun mugun kishi irin haka? ba ta yi da uwar ƴa ba amma tana yi da ƴar cikin ta. Abban Kamal dagaske ka bata maganin kenan?"

Ya sauke ajiyar zuciya yana dubanta.

"Ameena ban bata maganin da Hajiya take tunani ba, maganin barci da cin abinci na bawa Husna, dan da wannan abun ne zan b'atar da tunanin Hajiyar. Na yi nazarin yarinyar ne yadda take a takure, to za'a sameta da rashin magana tare da rashin walwala, sai kawai na had'awa Hajiya bayanin da zaisa ta gamsu kamar yanda na labarta miki, sai kuma rubuta result ɗin dana

yi, amma sam banyi wani abun cutarwa ga yarinyar ba, kawai dai damuwar da nake yi shi ne, zuciyoyi nawa nasa a cikin damuwa? Kamar yanda nake tsammani kinga ga mahaifin yarinyan yana cikin damuwa sosai, a yadda na yi waya da shi Allah kad'ai yasan halin da yake ciki, wannan shi ne abin da ya hanani sukuni yinin yau"

"Gaskiya Abban Khadija ka yi matuk'ar k'ok'ari da taimakon da ka yi, Allah yaga niyyar ka akai, ba zai kamaka da laifi ba, saboda ka yi dan ceton rai ne, kuma ma da baka yi haka ba Allah kad'ai yasan ina Hajiyar zata je dan aiwatar da mugun nufinta, kasan dai da kud'i kuma mutane babu tsoron Allah a ransu zata samu masu yi mata haka, ni dai ka daina damuwa insha Allah babu wani matsala Addu'a zamu yi, Allah ya yafe maka ƙarya da ka yi dan ceto rai da kuma Allah ya fidda yarinyar daga wannan damuwa"

"Ameen ya rabbi"

A sannan ne ya iya sakin jikinsa, Ameena ta kawo masa abinci ya fara ci, sai ta shiga yi masa hira.

"Wallahi haka Khadija take bani labarin wata 'yar class d'insu a makaranta, wai Maman yarinyar bata bata abinci kullun cikin k'azanta 'yar take zuwa makaranta, ita ke tsammata abincin in ta je da shi, dalilin daya sa kenan na ƙara mata yawan abincin saboda Yarinyar ta riƙa ci"

"Yanzu haka ita ma bai wuce riƙonta a ka yi ba, Allah dai ya kyauta yasa mufi ƙarfin zuciyarmu"

"Ameen ya rabb, bari na je na duba su Khadija ko sunyi barci"

"Ok ki tawo min da coffee in zaki dawo"

Ta amsa masa to ta wuce tana jinjina labarin da Mijinta ya bata.

******* *******

Daddy bai iya cin komi ba yaje d'akin Husna ya zauna gefen gadonta tana barci, kallonta yake yi yana zubda kwalla, ya shiga tunanin Zainab mahaifiyarta wacce suka yi taƙaitaccen rayuwa cikin wahala da tashin hankali, soyayyar da yake mata shi ne ya koma katsokan kan Husna, damuwarsa yanzu shi ne, in Zainab taji halin da ƴarsu take ciki ya zata yi?

"Zainab na san duk inda kike a yanzu kina cikin kaɗaici da damuwa, na yi alƙawari zan ƙara nisanta dake ba zan taɓa bari ki san halin da Husna take ciki ba, dan na san in kika ji zaki shiga cikin tashin hankali, zan kuma kula miki da ita kamar yadda kika danƙa min amanar ta, har zuwa ƙarshen rayuwata"

Ya ce a fili yana mai goge kwallarsa, ya gyarawa Husna kwanciya ya fito ya wuce ɗakinsa jiki a mace. Momy saboda bak'in ciki ko d'akin bata biyo shi ba, tana d'akinta sai kai komo take yi

abin duniya ya dameta, harta soma dana sani akan dama bata haukata Husna ba, tunda gashi hakan na niman barazanar shiga tsakaninta da mijinta ta.  Ta ɗauki wayarta ta kira Haj. Uwani labari duk abin da ke faruwa.

"A gaskiya ina ganin Hajiya zan sauya salo, gobe insha Allah zan zo ki kaini gun boka danya bani maganin mallaka"

"Karki damu ƙawata wannan ai abu ne mai sauƙi, je ki kwanta ki yi barci mai dad'i kamar kinyi bak'o ya mutu, kin san boka cika aiki bai da matsala"

"Hakane Hajiya, nagode sai na zo"

"Ok Allah ya kaimu "

Sai suka aje kan wayar.

******     ******

 *Washe gari*

Momy ta fito daga sashin ta, ta nufi ɗakin Husna ta d'aka mata duka ta farka a firgice.

"Maza tashi ki shirya ki tafi makaranta, daƙiƙiyar yarinya kawai, wannan ma ai asarar kuɗin makarantar yake dan nasan ba wani abun kirki kike ɗauka ba"

Husna ta sauko daga gadon da sauri ta nufi ba yi, Momy taja dogon tsaki kana da juya ta fice tana sababi. Husna ta wanke fuska da k'afa ba zancen wanke baki ko ta yi wanka babu wanda yake nuna mata, haka ta taso cikin rashin kula da gata, cikin sauri ta shirya ta sanya uniform ta ɗauki jakarta ta fito falo taga Momy zaune ta d'aura ƙafa ɗaya kan d'aya, jiki a sanyaye ta je gabanta ta tsuguna ta ce a tsorace.

"Momy ina jin yunwa"

ta yi maganar kamar zata yi kuka, Momy ta daka mata tsawa.

"Bari na zama abinci sai kici ko, maza ki b'ace min da gani wawuya kawai, mahaukaciya"

Jikinta yana ɓari ta bar falon har tana cin tuntuɓe, ta nufi wurin Baba mai gadi.

"Baba ina kunu na da kosai"

Ta ce fuska kamar zata yi kuka, Baba ya yi murmushi yana kallonta cike sa tausayawa

"Na cinye ban rage miki ba"

Husna ta yi rau-rau da ido kamar kwalla zai zubo ta ce.

"Allah yunwa na keji fa"

Baba ya miƙe zai d'auko mata sai kuma ya tuna da gargad'in da Dady ya yi masa, sai na ciro naira ashirin a aljihunsa na gaban riga ya bata.

"Gashi ki siya kosai kici yau ban aje miki komai ba, kiyi haƙuri ƴar Baba"

Sai ta fara yi masa kuka ta amsa kud'in ta fita gate ranta a dagule.

*****

Bayan ta isa makaranta ta zauna inda ta saba zama, duk yaran suna cikin walwala sannan sun kasance fes amma banda Husna da take warin datti, ta zama abin kyama da tsangoma cikin ɗalibai, ta manta da kayan da Jimmai ta wanke mata, garin sauri da fargaban kar Momy ta bugeta ta sanya masu datti, dan ba gaba ɗaya Jimmai ta wanke mata ba saboda bata aje su a fili ba. Khadija ce ta shigo riƙe da basket na abinci ta zo kusa da ita ta zauna tana dariya.

"Husna yau kin rigani zuwa, Abbana ne yasa ni latti"

"Um ni, ni ko brush banyi ba Momy ta koroni wai in tafi makaranta, um um ko kar yawa banyi ba yunwa nake ji"

Ta ƙare maganar kamar zata yi kuka.

"Momin ki bata sonki muguwa ce, to ga abincina ki ci Momy na indomie ta dafa min harda kwai"

Cewar Khadija, Husna ta amsa abincin ta fara ci hannu baka hannu kwarya, sai da ta ci kusan rabi sannan ta rufe kular, ta ɗauki gorar ruwa tasha kana ta yi gyatsa.

Anty Meena ce ta shigo class d'in, duka yaran suka tashi suna gaishe ta, ta musu umarni dasu zauna cikin harshen turanci, nan ta fara musu karatu bayan ta kammala ta umarce su dasu kawo mata assignment ɗin da ta basu na ranar friday, duk suka kai mata amma banda Husna, ta dago kai ta ce.

"Husnah Khalil"

Husna ta amsa sai ta isa gaban Malamarsu ta tsaya.

"Ina naki assignment ɗin ban ganshi a nan ba, ko yau ma ba ki yi ba?"

Idon Husna ya ciko da kwalla.

"Um um na ce ma Momy na ta min amma taƙi sai ta koreni"

Anty Meenat ta dafe kai ta shiga yin zancen zunci.

'Wai yaushe yarinyar nan zata zama mai ƴanci ne? kullun cikin matsala ohhh ya rabbi'

Ta ɗago ta kalle taga kayan jikinta duk datti.

"Husna wai me yake damunki ne? meyasa Maman ki bata baki kulawa ne? gaki da kwakwalwa amma iyayenki suna mai da miki karatun ki baya, me yasa jiya monday baki zoba?"

Husna ta fara kuka ta fara ta ce.

"Anty, Momy ne bata min wanki ni kuma ban iya ba, Baba mai gadi nake bamawa ya wanke min ko Mama Jimmai, kuma Momy tana duka na sosai har zagina tanke yi ta ce min mahaukaciya"

Damuwa ya ziyarci Anty Meena sai ta ƙirƙiro murmushi.

"My dear ki daina faɗar haka Momy ki tana sonki, k'ila kina mata laifi ne, dan haka ki riƙa mata biyayya kinji zata daina dukanki"

Husna ta girgiza kai alaman ta daina, Anty Meena ta share mata hawaye ta umarce ta data koma ta zauna...

_Wace ce Husna Khalil?_

*Rahma ce*
[10/14, 5:42 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 7 ~ 8_*

*WACE CE HUSNA KHALIL?*

_Waiwaye adon tafiya_

Alh. Ahmad tanko mai kanti babban ɗan kasuwa ne acikin garin Kaduna, babu wanda bai san Alhaji mai kanti ba faɗin garin da kewayenta, dan ya kasance mutum mai karamci da mutunci, yana kasuwancin kayan hatsi da ɓangaren madara da sauran kayan masarufi, yakan yi order daga garuruwa daban-daban, ya bayar da sari ga ƙananan ƴan kasuwa.

Asalin sa d'an garin yola ne bafulatanin asali daga ƙaramar hukuman michika, yana da mata d'aya mai suna Haj. Asma'u Sani mai kanti, auren zumunci aka yi musu. Sunan mai kanti ya samo asali ne tun daga gun kakannisu wanda daga yawon kiyo har suka yada zango a cikin garin Kaduna, daga bisani suka zama sun yad'u a garin sosai, duk iyayensu sun rasu.

Alh. Ahmad yana zaune a unguwar malali, yaran su hud'u maza biyu mata biyu, Aliyu shi ne babba, sai Ismail da yake bi masa, sai Fatima sannan Zainab ita ce auta.
Alh. Ahmad mai kanti wanda yaransa suke kiransa da Baffa, sai kuma Haj. Asma'u da suke kira da Umma, sun tsaya sosai wajen tarbiyyar yaransu, sun basu ilimi na Addini har zuwa na zamani.

Yaya Aliyu kamar yanda ƙannansa ke kiransa ya yi karatu a ɓangaren kasuwanci, bayan ya kammala ya cigaba da riƙe kasuwancin mahaifinsu, ya yi aure sunan matarsa Jidda d'iyar abokin Baffansu. Yaransu biyu, Abubakar Sadiq ne farko sai Fatima dake bi masa, wacce suke kira da Zahra.

Yaya Ismail shi kuma ya kasance mai matuƙar son karatun boko ɓangaren lafiya, Baffa ya turashi kasar India a can ya yi digree d'insa har ma da masters ya zama cikakken medical Doctor, bayan ya dawo k'asarmu Nigeria ne ya soma aiki a general hospital dake nan cikin Kaduna, a lokacin Anty Binta tana karatu a ABU Zaria 400level tana karanta Biology. Sai auta Zainab da take secondary school matakin ƙarshe.

****** *******

_*Bayan shekara ɗaya*_

Ya Ismail anyi masa transfer zuwa kano wanda bai so haka ba, amma ba yadda ya iya dole ya tafi. Bayan watanni da tafiyarsa yazo wani hutu a kaduna, Baffa da Umma suka sanya shi gaba da zancen aure dole sai ya fito da mata, da farko ya tubure bai so saboda shi ko budurwa baida ita, Baffa ya ce ya yi masa had'i da 'yar wajen abokinsa dake nan Kano Alh. Kamal, yaje su gana in sun fahimci juna a sanya biki.

Ana cikin haka sai bikin Anty Binta ya tashi, bayan ta kammala karatunta service take yi a ministry of education dake nan Kaduna, a nan ta haɗu da Al-mustapha Salis mai siminti, mahaifinta ya kasance ɗan kasuwa yana sai da siminti da duk abin da ya shafi gini, bayan sun fahimci juna aka sanya biki har sai ta kammala service nan da wata bakwai.

ya Ismail da yaje kano, ya tafi gidan Alh. Kamal, sun gana da Amina kuma sunyi na'am da

junansu, sun fahimci juna cikin k'ank'anin lokaci soyayya mai k'arfi ya shiga tsakaninsu, ganin haka ne iyayensu suka tsaida kwanakin biki dai-dai dana Anty Binta a lokacin bikin sauran wata huɗu.

******

*_Biki wan shagali_*

Lokacin bikin ya gabato, inda dangi da mutanen arziki duk sun hallaro, daga ɓangaren mutanan Kano harna Kaduna duk suna ta fama da shagalin biki. Ranar asabar aka d'aura auren Anty Binta da Al-mustapha, su Baffa suku ɗunguma zuwa Kano aka d'aura na Yaya Ismail, ansha shagalin biki kowa yana cikin farin ciki. Auta Zainab ta yi farin jini kowa Zee, Al'amin d'an k'anin Umma wanda suke kira da Baffa Iro, suna zaune a nan cikin Kaduna da matarsa Inna Kulu, Al'amin shi ne d'a ɗaya da Allah ya basu, duk wani son duniya sun d'aura masa, ya yi karatu a ƙasar Germany ya kammala, dawowar sa kenan ya cimma wannan shagalin, tunda ya yi arba da auta Zee zuciyar sa ta kamu da sonta.

Haka aka sha biki, matar Yaya Ismail an kaita sabon gidan da Baffa ya siya masa a nan Kano, ba'a sha wahalar kai Amarya ba, da yake ita ma nan kano suke, Anty Binta kuma an kaita can gidan mijinta dake tudun wada, anyi biki an watse kowa ya koma gidansa lafiya. Angwaye da Amare sun angonce cikin farin ciki tare da ƙaunar juna.

******

*Bayan wasu lokuta*

Shaƙuwa mai karfi ya shiga tsakanin Al'amin da Zainab tun sunayin abunsu su kad'ai har 'yan uwa kowa yasan tsakaninsu, ana haka sai Zainab ta samu admission a ABU Zaria ta samu pharmacy, farin ciki gunta ba a magana kowa ya yi farin ciki aka fara haɗa mata kaya da sauran abubuwa na buƙata, lokacin da Al'amin yaji labari zuciyar sa bai yi masa dad'i ba yaso ace a KASU ta samu saboda baya son ta yi nesa da shi, yaje ya samu Abbansa da zancen yana so a nima masa auren Zainab, Baffa ya yi farin ciki sosai ya ce insha Allah zai je ya samu su Baffa dan su dai-dai ta magana.

*Bayan kwana biyu*

Abba yaje ya samu su Baffa da maganar auren Zainab da Al'amin, sunyi murna dan dama burinsu su zab'awa Zainab miji wanda zai kula da ita, nan suka yanke magana cewar an bama Al'amin Zainab amma sai ta kammala karatunta sannan ayi bikin, duk suka yi na'am da haka, kana suna yi hirar zumunci Abba ya tafi gida cike da farin ciki. Ko da ya labartawa matarsa da maganar da kuma shi Al'amin ɗin sunyi murna kuma sun amince da hakan.

******

Ranar lahadi ya kama ranar da Zainab zata tafi makaranta, duka family sun taru a babban falon

gidan suna tattaunawa, anan Baffa ya shaida musu da hukuncin da suka yanke kan Zainab da Al'amin, duk abin ya musu dad'i har ita kanta Zainab da taji kunya ya rufe ta, bayan sun tattauna suka yi mata nasiha mai ratsa zuciya tare da mai da hankali kan karatu da kuma ta kama kanta da mutuncin ta, sai da Zainab ta yi kuka, bayan sun kammala suka d'unguma dukansu su ka nufi Zaria birnin zazzau.

Ko da suka isa, suka shiga cikin makaranta, b'angaren d'akin dalibai mata suka nufa, d'akinta dake jerin k'asa sannan ita kad'ai zata yi using d'inta, babban d'aki ne ciki d'aya sai ba yi da kicin aciki, sun gyara mata ɗakinta, sun sanya mata gado da katifa, sai kujera guda ɗaya sannan kayan kallo sai kicin da suka gyara mata da tsirarun kayan buk'ata, sun wanke mata bayinta, sun kammala mata komai, bayan sun gama suka ƙara mata nasiha kana suka kamo hanyan Kaduna, suka bar Zainab cikin damuwa da kewar su, tana tsaye har sai da taga ƙulewar motansu sannan ta juya tana share kwallan daya zubo mata a idonta.

Juyawar da zata yi sai taga mutum tsaye a gabanta, ta ɗago ido tana kallonsa ya sakar mata wani lallausar murmushi wanda ya sanya gabanta faɗuwa.

"Ki yi haƙuri kowa ma haka ya tsinci kansa lokacin da aka kawo shi karatu, insha Allah da haka zaki saba"

Ya ce yana kallonta, ta ɗaure fuska ba tare da ta ce masa komai ba ta matsa ta ba shi guri ta wuce, ya shiga binta a baya kamar an sanyashi tsaronta, ta buɗe ƙofa sannan ta juyo ta harare shi ta girgiza kai ta shige ɗakinta ta rufo ƙofa, murmushi ya yi wanda yake ƙara masa kyau kana ya juya ya tafi. Gurin da suka saba zama ya nufa, ya hango Nuhu abokinsa sai ya k'arasa da sauri yana ƴar fara'a ya ce.

"Abokina kasan kuwa yau na yi gamo da d'awisu"

"Haba a ina ka gani?"

"Hmmm yau ɗin nan na ganta, uhum kyakkyawa ce mai matsakaicin tsaho, dara-daran idanu masu kama da kalar barci, mai d'an k'aramin baki tare da siririn hanci, fara ce dai-dai mai kama da balarabiya, Allah ya yi halitta a wajen dawisu mai kyau da ado"

Nuhu ya saki baki yana kallonsa har sai da ya gama lissafowa ya ce.

"Ya kake magana a dunƙule kamar wani zautacce, ni fa ban gane maka ba, dawisu ka ganni ko mutum?"

Ya yi wani lallausar Murmushi ya lumshe ido kana ya buɗe su.

"Ba zaka gane ba tunda baka san yadda nake ji ba, idan ka ganta sai ka tabbatar da abin da nake gaya maka, hmmm yanzun nan na gamu da ita"

Nan dai ya kwashe yanda suka yi ya ba shi labari, dariya sosai Nuhu ya yi.

"Lallai Khalil yau Allah ya kamaka, ashe akwai rana irin ta yau da zanga Mace ta tafi da imanin ka, kullun mata suna binka amma ka tsanesu sam kai wai baka soyayya, to yau gashi ka shiga hannu da alama kuma zaka sha wuya"

Dariya ya yi ya ce.

"Kuma insha Allah duk wuya sai na yi nasara ba"

Yana faɗar haka ya miƙe tsaye da cewar.

"Tashi mu wuce in ka ga dama, in kuma zaka cigaba da min sharrin ne sai ka zauna"

********

Ɓangaren Zainab kuwa tana komawa d'aki ta zauna gefen gadonta ta yi ta gumi, tunanin rayuwa take yi sai ga kiran yaya Al'amin ya shigo wayarta, sai ta d'auka nan suka soma hiransu na masoya har kusan minti ashirin kana suka yi sallama, ta tashi ta gabatar da sallar la'asar sannan ta ci abinci da yake Anty Jidda ta yi mata miyar stew mai yawa, da danbun nama tare da soyayyar naman kaza, Anty Binta kuma cin-cin mai kwakwa ta yi mata sannan da meat pie, Umma kuma yaji ta yi mata mai kyau da daɗi, a gaskiya Zainab 'yar gata ce gun iyayenta da family ɗinta duka. Bayan ta kammala ci ta shiga bayi ta yi wanka, bayan ta fito ta shirya cikin riga da sket 'yar kanti, sai ga kiran Anty Jidda ta d'auka suka gaisa sannan ta yi musu bangajiya kana ta bama Umma suka gaisa sannan ta yi musu sallama ta kashe wayar.

******      ******

*Ranar Monday*

Ta fito cikin riga da zani rafa na atamfa ta yi kyau abin ta sosai, ta yi mild make up, ta sanya hijab fari takalmi baƙi da jaka, sai takardu da ta riƙe a hannunta, ta rufe d'akinta kana ta juya da niyyar wucewa class, ganinsa ta yi a gabanta yana yi mata murmushi.

"Amincin Allah ya tabbata a gareki 'yar uwata, da fatan kin fito lafiya"

Ta kallesa ido cikin ido na tsawon minti uku bata ce komai ba, kana ta bi ta gefensa ta wuce, ya shiga binta suka jeru a hanya suna tafiya ba um ba um-um, har sai da ta lalubo class d'insu kana na shige abin ta.

"Ya mai cikar kamala ina miki fatan alkhairi ki yi karatu cikin aminci"

Ya ce yana mai kallonta, Zainab ta jiyo ta kalle shi ta yi murmushi da bai kai zuci ba ta shige abin ta, shima sai ya saki murmushi ya ce a ransa.

'Masha Allah, haƙiƙa wannan ta yi kuma ko ba komai tana da cikar kamala da tarbiyya, lallai murmushinki ya nuna min ina da alaman samun nasara'

Ya juya ya cigaba da tafiya, a hanya ya gamu da Nuhu suka gaisa.

"Abokina daga ina kake?"

Khalil ya sosa ƙeya yana murmushi.

"Na rako mutumiyata ce zuwa aji"

Nan ya ba shi labari, Nuhu ya shiga jinjina lamarin.

"Hmm Abokina kana son d'auko rigima to Allah ya bada sa'a"

"Yauwa gwara dai ka fad'a Alkhairi, Ameen"

Ya ba shi hannu suka tafa kana suka wuce ajinsu suma.

*Rahma ce*
[10/15, 6:48 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 9 ~ 10_*

Bayan sun fito lectures, Zainab ta samu wani dakali kasan wata bishiya ta zauna, ta dauko wayarta dake jaka ta cire ta a silent, a nan ta ga miss called d'in yaya Al'amin da Ummanta, ta fara kiran umma suka gaisa suka dan taba hira sannan suka yi sallama, kiran ya Al'amin ne ya shigo da sauri ta d'auka nan ta shiga ba shi hakuri da kuma dalilin rashin d'aukar wayan da bata yi ba, suka yi hirar soyayya kana suka yi sallama.
Kamar ance ta kalli gefenta ta ganshi ya kura mata ido ta tsuke fuska sannan ta kauda kai, Khalil yana zaune nesa da ita kad'an duk wayan da ta yi zan iya cewa a kunnansa duka, tunda ya hangota ya zo ya zauna yana kallon ta, gundura da ta yi da zaman wurin ne yasa ta mike cikin yanayin gajiya ta wuce d'akinta, shima ya tashi yabi bayanta har sai da suka ida kofar d'akin, Zainab ta juyo cike da fushi.

"Malam wai lafiya kake bina, meye matsalar ka dani?"

"Ba komai sai Alkhairi, kawai ina jinki a raina kamar 'yar uwata ce. Dan Allah ina so ki d'aukeni kamar dan uwanki, insha Allah ba zan zame miki matsala ba ko na cutar dake"

"Na ce maka ina kalan dangi ne? ka fita a rayuwata tun kan in d'auki mataki a kan ka"

Tayi maganar a zafafe tare da jan tsaki kana ta shige d'aki ta barshi a tsaye a gun. Ya shafa sumarsa kana ya yi murmushi.

'Uhum kyakkyawar fuska ga kuma murya mai dadi, masifar ma k'ara mata kyau ya yi'

Ya ce a ransa kana ya juya ya tafi.

*KHALIL HASSAN*
D'a ne a gurin Alhaji Hassan dan gombe, Asalinsu mutanan gombe ne, mahaifinsa ya kasance 'yan biyu Hassan da Husain, su kad'ai ne gun iyayensu, sun tashi cikin kulawa da k'aunar juna, kasuwanci ne ya dawo da iyayensu garin Kano, sunyi karatu iya secondary daga nan suka fad'a harkan kasuwanci, Hassan ya yi aure da Halima wacce suka hadu a kasuwa daga nan suka kulla soyayya harta kaisu ga aure. Hussain shima ya yi aure bayan shakara uku da auren Hassan, a lokacin inna Halima ta haifo d'anta wanda ya ci sunan kakansa Ibrahim suke kiransa da Khalil.

Fad'i tashi dai na rayuwa ba wanda ba su yi ba kusan tsawon shekara goma wanda har a lokacin matar Hussain bata haihu ba, hakan ne yasa Khalil ke samun kulawa da soyayya gurin iyayensa, duk wata d'awainiyar sa Baba Husain yake masa, hasali ma gidan sa yake da zama, ana haka ne tafiya ya kama Baba Hassan zuwa Lagos dan saro kaya, suka tafi da inna Halima, suka bar Khalil gidan Baffansa Hussain.

Tafiya karar kwana, A wannan tafiya ce iyayan Khalil suka rasu, kan hanyarsu ta dawowa sukayi hatsari, wannan al'amari ya tashi hankulan dangi, Khalil ya yi kuka sosai amma daga bisani inya tuna cewa yana da wasu iyayen sai ya yi farin ciki.
Haka su Baffa Hussain suka cigaba da kula da shi, tare da kulawan kakanninsa. Baffa na kula masa da dukiyarsa wanda iyayansa suka bar masa, sun ba shi tarbiyya sosai tare da ilimi na addini, Khalil yaro ne mai natsuwa da hankali tare da biyayya ga manyansa, miskili ne kuma kyakkyawa ne, yana da idanu da matsakaicin tsawo, kalar fatansa yaba da haske sai dai ba sosai ba.

Baffa bai so sanya shi makaranta nesa ba, lokacin daya gama secondary school sunyi kokarin nima masa jami'a a nan cikin kano, amma fir yak'i ya ce shi a Zaria zai yi karatu, ba yadda suka so dole suka yi masa hakan, basu sha wahalar samun admission d'insa ba a bangaren da yake so Accounting, suka kama masa gida a nan cikin Zaria nesa da makaranta sannan suka siya

masa mota ta zuwa makaranta da d'an rage zirga-zirga.
Yanzu yana matakin na 2 kenan a karatunsa 200level, yana da mai da hankali shiyasa sam baya kula mata abokai ma baya kulasu sai Nuhu kad'ai. shima ya yaba da natsuwarsa ne yasa suka k'ulla abota.

Zainab ita ce mace ta farko daya fara jin sonta a ransa lokaci d'aya, kuma yana ji a ransa duk wiya duk runshi sai ya mallaki zuciyar ta. Kuma zuciyar sa na tabbatar masa da zasu rayu tare, dan haka ne bai yi kasa a gwiwa ba yake shanye duk wulak'ancin da zata yi masa.

******

Khalil ya zamar wa Zainab chewing gum, duk inda take yana gun kamar hand bag, duk iya masifa da bakar magana ba wanda baya sha a gunta, amma ya tsanye ya rufe idonsa kuma ya kafe, ya zamana in dai ya shigo cikin makaranta tofa kofar d'akinta yake fara dosa, haka kuma kullun yana kofar class d'insu, abokinsa Nuhu kullun cikin masa fad'a yake, daga karshe harya fara ba shi tausayi yana ganin abin ya zama masa lalura, dole ya koma masa nasiha da lallashi.

****** ******

Kwanci tashi ba wuya a gurin Allah, su Zainab sun kammala jarabawar su na third semester, wato karshen zangon 100level, kayanta ta shirya tsaf a trolley ta rufo d'akinta, ta fara jan jakarta har zuwa bakin gate d'in makaranta, Khalil yana tsaye yake a gefen hanya kamar yana jiran futowarta, yana ganin ta ya matsa kusa da ita.

"Zainab na san kina farin ciki da abu uku a yau"

Kallonsa ta yi cikin harara.

"Ehen ko meye damuwar ka a kan farin ciki na, nifa bana son shisshigi gwara tun wuri ka fita hanyata, tunda na shigo school d'in nan ka matsawa rayuwa ta, ko wani hutu in zan koma gida da salon da kake zuwa min, yau kuma ka wani zo min da iyayi"

Ta kare maganar da jan tsaki kana ta cigaba da duba mai napep, Khalil ya yi murmushi wanda ya bayyana fararen hakoransa.

" 'yar uwa, mai da wuk'ar Dan Allah bana son na b'ata miki rai a kan farin cikin da kike ciki, sannan ma ai baki jira na gaya miki meye abu ukun daya saki farin ciki ba"

Ya yi Jim yana jiran me zata ce masa, amma sai ta yi masa shuru, ya cigaba da cewa

"Da farko kina farin cikin zaki ga su Umma da sauran family dinki, na biyu kuma kina farin cikin ganin yaya Al'amin, na uku kuma kina farin cikin yin nesa dani da zaki yi na tsawon wata guda, zaki huta da naci na da kuma surutu na"

Sai ya k'arasa masanar da fuskar tausayi kamar zai yi kuka. Bata tanka masa ba, lokacin dai-dai mai napep ya tsaya kana ta shiga da kayanta ta zauna shima cikin azama ya zauna gefenta, ta sanarwa mai napep inda zata ya wuce dasu, bata bi ta kan Khalil ba saboda in da sabo ta saba da haka, dan duk hutu sai ya rakata ta shiga moka kan ya wuce shima.

Bayan sun isa ta biya mai napep harda na Khalil d'in kana ta yi shatar taxi ta biya, sannan ta shiga gidan baya da kayanta duka, Khalil ya sun kuyo da kansa gefen windon motar ya ce cikin sanyin murya.

"Zee na ina ni man alfarma guda d'aya a gunki, dan Allah ba dan na isa ba ki yi tunani na koda sau d'aya ne, in har kika yi min haka zuciya ta zata gaya min, kuma zan kasance na yi hutuna cikin nutsuwa, sannan daga k'arshe ki kula min da kan ki"

Yana gama fad'ar haka ya cire kansa daga motar ya daga mata hannu fuskar sa d'auke da murmushi. Haka nan take kallonsa bata iya masa ko da murmushi d'aya ba sai dai idonta ya kasa d'aukewa daga kallonsa, a haka har mai mota ya jata suka nufa cikin Kaduna.

Khalil yana barin tasha, makaranta ya koma ya dauki motarsa kana ya yi sallama da Nuhu sai ya wuce gidansa ya had'a kayan sa, sannan ya wuce Kano.

******

Zainab tun a mota taji ta kasa sukuni tunanin Khalil ya dameta, kamar ko wani Hutu in zata tafi da wannan yanayi take isa gida haka ma wannan karan, inta tuna wasu kalamansa sai ta yi murmushi, in ta tuna wani abu da ta yi masa na wuk'alaci sai taji ba dad'i, a haka har suka isa gida tana cikin yanayi na tunaninsa.

Duk dangi sunyi farin ciki da dawowarta musamman Umma da Anty Jidda, ta samu tarba mai kyau sosai, hira suke yi na makaranta da sauran abin da ya faru a nan gida da bata nan har zuwa dare, bayan sallah isha'i ya Al'amin yazo duk suka gaisa kana suka watse gaba d'ayansu suka bar Zainab da yaya Al'amin, haka nan Zainab taji gabanta ya fad'i take taji bak'on yanayi ya ziyarce ta, tunanin Khalil ne ya fad'o mata a rai, wanda har ta soma jin kamar yana ganinta, zuciyarta na bugawa da sauri da sauri, nan da nan yanayin ta ya canja, sai taji sam bata yi farin ciki da ganin Al'amin ba.
Sun d'auki kusan minti goma a haka ba wanda ya ce wa wani uffan, mamaki ya cika yaya Al'amin mamaki saboda ya san Zainab ba haka take masa ba a duk lokacin da ta dawo makaranta, takan yi masa abinci mai kyau tare da nuna masa yadda ta kosa ta ganshi dan ta ba shi labarin Exam d'insu, sab'anin yau da ko magana ta kasa yi masa sai wasa take yi da yatsunta. Cikin yana yi na damuwa ya ce.

"My Zee"

Ji ta yi kamar ya caketa da mashi a kahon zuciya, ta d'ago kai ba tare da ta amsa ba, ya cigaba

da cewa.

"Lafiya yau na ga sauyi a tattare da ke? ki gaya min meke damunki ko kuma na yi miki laifi ne?"

"Ba komai kawai dai kaina ke ciwo"

"Hmmm kanvki na tsiwo ne zan zo na taddaki kina hira dasu Anty Jidda harda dariya, amma suna tafiya sai kika chanza fuska, haba my Zee ki gaya min laifina sai na baki hakuri kinji"

Zainab ta saki murmushin k'arfin hali.

"Nifa ba komai, abin da na gaya maka da farko shi ke damuwa kawai"

tana gama fad'an haka ta mik'e tsaye.

"Yaya Al'amin zanje na kwanta kaina ya matsa min da ciwo, gobe in Allah ya kaimu mayi waya"

Bata jira me zai ce mata ba ta yi gaba abin ta ko zata damu sassauci daga bugun da zuciyarta ke mata.

Cike da kallon mamaki ya bita har sai da ta k'ule, zuciyarsa yaji ya takura da damuwa ga kuma rud'ani da ya ziyarce shi.

'Allah karka jarabceni da abin da ba zan iya ba, tabbas akwai matsala kuma ina gudun afkuwarta'

Ya ce a zuci tare da sauke ajiyar zuciya, ya fuskanci tunda Zainab ta koma wancen Hutu ta canza masa, in suna waya ya tambayeta sai ta ce k'alau take ko ta gindawo masa da wata maganar da zai kawar da tambayar da ya yi mata. Cikin sanyin jiki ya tashi ya tafi ba tare da ya yiwa kowa sallama ba.

Zainab d'akinta ta shiga ta rufe, gado ta fad'a tare sakin wani irin kuka da ya kubce mata mai ban tausayi, tambayar kanta take yi.

"Meyasa haka? zuciyata ki na niman sani a matsala, wai meke shirin faruwa dani ne?, Allah kamin maganin abin da ba zan iya ba"

Ta ci kukanta ba mai lallashin ta harta yi shuru kana ta share hawayenta tare da shiga bayi ta wanke fuska, ta fito ta yi shirin barci ta kwanta tare da Addu'a. Rufe idon da da zata yi ta hango Khalil na mata murmushi sa mai kara masa kyau da kwarjini, da sauri ta bud'e idonta still abin da ta gani idon ta rufe haka ta k'ara ganin sa a zahiri, nan da nan bugun zuciyarta ya k'aru, ta runtse idonta sai Addu'a take yi kuka ne ya kuma kubce mata tana cewa.

"Haba Khalil me na yi maka, dan Allah karka shigo rayuwa ta, baza ka samu abin da kake so ba"

Haka ta yita sambatu har barci ya yi awon gaba da ita da busasshen hawaye a k'uncinta.

****

*Gari ya waye*

Duk gidan sun had'u a dinning dan karyawa amma babu Zee ba alamarta, Anty Jidda ta aika Zahra data je ta taso ta, ko da ta isketa ta fito daga wanka tana shafa mai, Zahra ta gaya mata sakon Mamanta sannan ta wuce, k'aramin tsaki taja.

"Uhum ni ban jin ma yunwa"

Ta ce a fili ta mike ta sanya riga da wando ta sanya na fakistan, ta d'aura gyalen a kanta, ta fito ta samesu sun kusa gama nasu breakfast d'in, kujera ta ja ta zauna ta gaida su duka kana ta jawo plate ta shiga zuba nata, haka dai take tsakura har suka gama nasu breakfast din, sai ita data rage harta kammala sannan ta tashi, mai aiki ta kwashe kayan kana ta gyara wurin. Anty Jidda ta ce.

"Zainab zo muje part d'ina ki tayani gyara d'akin Sadiq anjima zai dawo"

"Ok, kin san na manta fa yana body schools ashe, amma ya kusa gamawa ko?"

"Ina fa, mutumin da yake jss 2"

"To Allah ya dawo da shi lafiya"

"Amin"

Suka wuce suna hira, a nan Zainab ke tambayar Anty Jidda.

"Anty meyasa in kamar mutum ya tuna da wani abu ko wani mutum sai yaji gabansa ya fad'i, bugun zuciya ya rika tafiya da sauri?"

Anty Jidda ta tsaya da aikinta taba kallon Zainab.

"Meyasa kuka tambayeni?"

Nan Zainab ta shiga bama Anty Jidda labarin Khalil bata boye mata komai ba har zuwa yadda take ji game dashi, Anty Jidda ta jinjina maganar ta ce a ranta.

'Lallai akwai matsala'

A fili kuma ta ce

"Zainab zauna muyi magana"

Duk zuka zauna suna kallon juna.

"Zainab kin tab'a jin irin haka akan yayanki Al'amin?"

"A'a ban taba ji ba"

"Zainab a iya fahimtar da na yi ma zancen ki, babu abin da ke sanya mutum yaji haka face So"

Zainab ta dago da sauri ta kalleta.

"Anty so fa kika ce? kina nufin ina Son Khalil?"

"Kwarai kuwa amma ki kwantar da hankalin ki, Zainab ina so ki sani kuma ki sanya a ranki babu ke babu Khalil, ki nisanta kanki da shi, ki guji duk abin da zai had'aki da shi, ki tuna da akwai baikon d'an uwanki Al'amin aka ki, wanda muna jira ki gama karatunki ne mu sha biki, ki manta da kin tab'a sanin Khalil, saboda wallahi in har kika bari soyayyarsa ya rinjaye ki tofa akwai babban matsala, ki ta Addu'a Allah ya cire miki sonsa da hakuri, wannan ita ce shawarar da zan baki nima kuma zan ta yaki da Addu'a kuma insha Allah ba zan fad'awa kowa wannan maganar ba, ki kuma daina canza ma Al'amin fuska gudun karya zarga wani abu"

Hawaye ya wanke idon Zainab, cikin shasshekar kuka ta ce.

"Anty Jidda nagode insha Allah zanyi amfani da shawarar ki da kika bani"

Nan dai Anty ta lallashe ta kana suka cigaba da aikin su.

********     ********

Kwanci tashi ba wuya a wurin Allah, Zainab sun kammala hutun su, a ranar lahadi ta shirya ta wuce makaranta. Ta iske d'akinta duk ya yi k'ura haka ta yi shara ta gyara dakin tare da jera kayanta data dawo dasu, da misalin karfe biyar na yamma, ta fito zuwa bakin gate dan ta siyo kankana, kamar daga sama ta ga Khalil ya tsaya a gabanta, nan take ta ji gabanta ya fadi, ta ce cikin fad'a.

"Malam lafiya meye haka?"

"Kalau, na hango ki ne nace bari na zo mu gaisa, ya hutu?"

"Ban sani ba"

Ta ce a tsiwace ta cigaba da tafiya harta isa wajen wani mai sai da kayan fruit, ta ba shi kud'inta ya yanka mata kankana, ya mika mata ledan da sauri Khalil ya karb'e kan ta amsa, cike da masifa ta ce.

"Wai kai maye ne? to wallahi nama na d'aci gare shi, ka fita hanya ta, haba Malam sai kace ance dole sai kamin magana"

Masifa take masa ta inda take shiga bata nan take fita ba, a takaice dai sai da mutane suka fara taruwa suna ganin ikon Allah, shi dai mai fruit hakuri yaketa bata, Khalil saboda mamaki ya kasa ce mata uffan sai kallonta da yake yi, ta gama masifarta ta karb'e ledan kankanar ta yi gaba abin ta ta barshi tsaye cike da damuwa. Cikin sanyin jiki yabi bayanta har suka shiga makaranta, d'akinta ta wuce amma bai daina bin bayanta ba, tana gab da isa d'akinta ta juyo cike da matsananciyar damuwa.

"Yau ka tabbatar min da kai maye ne to nafi k'arfin ka"

Ta cigaba da tafiya, cike da damuwa ya ce.

"Zainab"

"Karna sake jin sunana a bakin ka"

Ta ce cikin bacin rai, ya tsaya yana kallonta.

"Haba Zainab yanzu na cancanci wulakanci a gurinki? me na yi miki ne haka? rabon da mu had'u kimanin wata guda kenan, wallahi hukuncin da kika d'auka akan na daina miki magana ba zan iya d'auka ba"

Zainab ta yi saki ta cigaba da tafiya, da sauri ya kamo hijab d'inta, cikin k'unan zuciya ta juyo ta wanke shi da mari guda daya mai kyau, nan take hankalin mutane gurinsu, da sauri Khalil ya sake mata hijab d'in, ya zaro ido yana kallonta cike da mamaki.

Zainab taji zuciyar ya yi mata nauyi numfashinta yana fita da kyar sakoman hukuncin marin da ta yi masa, hankalinta ya yi matukar tashi bata san sanda ta fashe da kuka ba, ta ruga zuwa d'akinta da gudu ta bude ta shige, Khalil ya shiga kallon yanayin data shiga tare da rik'e k'uncinsa, ganin ta wuce yasa mutanen da suka taru suka fara janye jiki, wasu na tausaya masa wasu kuma nacewa Allah ya k'ara.

Nuhu ne ya karaso gurin Khalil ya ganshi a cikin wannan yanayin ya ce.

"Khalil lafiya naga jama'a sun tasaka a gaba suna kallonka?"

Hawaye ne ya gangaro wa Khalil a kuncinsa ya girgiza kai, ganin haka sai hankalin Nuhu ya tashi, ya kama hannunsa ya ja har wajen motarsa ya bude tare da zaunar da shi kusa da mazaunin driver sannan shima ya zagayo ya shiga tare da tada motar suka bar makaranta.

Tana shiga d'akinta ta fad'a kan gado kuka ta yi mai isarta, wayarta taji yana k'ara alamar kira ya shigo sai ta duba ta ga Anty Jidda ce, da sauri ta dai-dai ta natsuwarta ta share hawayenta ta d'aga kiran, bayan sun gaisa Anty Jidda ta ce.

"Zee yana ji muryanki kamar kina cikin damuwa?"

Aiko kamar Anty Jidda ta zugata ta fashe da wani sabon kuka, cikin lallashi da tausasa murya Anty Jidda ta rika bata magana, har ta samu ta daina kukan sai ajiyar zuciya, nan ta bata labarin abin da ya faru tsakanin ta da Khalil d'azun. Anty Jidda ta ce.

"Haba Zainab me ya yi zafi da zaki mare shi, nifa dana ce ki yi nesa da shi ba ina nufin ki yi masa wulakaci bane, ko ki yi masa rashin d'a'a, irinsu fa da lalama ake rabu dasu, nuna fushi ko masifa ba shi ne zai sa ki samu nasara ba, dole sai kin danne zuciyarki, haba Zainab ki rika aiki da hankali mana, inda ace wani ne ya bani labarin nan sai na k'aryata saboda ba halinki bane"

Zainab ta saki ajiyar zuciya mai nauyi ta ce cikin rawar murya.

"Insha Allah Anty hakan ba zai sake faruwa ba"

"Yauwa Zee ki yi k'ok'ari ki ba shi hakuri dan ku rabu lafiya dan Allah, kin ji autar Umma"

Zainab ta yi guntun murmushi.

"To Anty zan yi yadda kike, nagode"

Haka dai Anty Jidda ta cigaba da bata magana har taji zuciyarta ta yi mata sanyi, daga bisani suka yi sallama.

*Rahma ce*
[10/17, 8:17 AM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 11 ~ 12_*

*Da gari ya waye*
Zainab ta yi shirin zuwa class haka nan taji bata son fita saboda abin da ta yiwa Khalil jiya tana jin kunyar had'uwa da shi, bayan ta gama ta fito rike da littafanta, waige-waige take yi kamar mai niman wani abu, jikin ta a sab'ule take tafiya duk sai taji ranta ya yi mata ba dad'i, yau ne rana ta farko da Khalil bai rakata zuwa class ba, iska taji yana busota da sauri ta kara yin waige-waige jikinta yana gaya mata Khalil yana kusa da ita sai dai bata ganshi ba. Kuma tabbas yana nesa da ita tare da Nuhu bayan wata bishiya, lab'ewa ya yi yana hangenta abin tausayi, kawai dai ya yiwa zuciyarsa alkawari zai yi nesa da ita.

Zainab haka ta yini sukuku cike da damuwa da tunanin halin da Khalil ke ciki, Addu'a take yi Allah yasa ba abin da ta yi masa jiya bane ya sanya shi wani hali.

*****

Kimanin mako uku kenan Zainab bata sanya Khalil a idonta ba, duk wani damuwa da tashin hankali ba wanda bata ciki, Addu'a kawai take yi da fatan Allah yasa yana cikin koshin lafiya, cin abinci sai ta yi da gaske take iya ci, duk ta rame daka ganta zaka shaida tana cikin damuwa, duk yamma take shiryawa ta shiga zagaye makaranta ko zata ganshi amma shuru sai dai ta gama bulayinta ta koma d'aki taci kuka mai isar ta sannan ta yi shuru dan kanta. Kuma duk zagayen da take yi lungu da sakon da take shiga, Khalil na biye da ita sai dai baya bari ta ganshi. Da farko tun Nuhu na gaya masa shi take nima yana k'aryatawa har ya gasgatawa zuciyarsa cewa tabbas shi take nima. Tausayin ta ne ya dame shi wanda yaso tuntuni ya bayyana kansa gunta, amma Nuhu ya hanashi ya ce ya bari da sauran lokaci tukunna kan ya bayyana gareta.

Ranar wani weekend da safe, misalin karfe 10am ta kimtsa ta karya kana ta koma ta kwanta tana kallon tashar Arewa24, d'akinta taji a na mata knocking, da sauri ta mike tana tunanin kila Khalil ne, tana bud'ewa taga yaya Al'amin tsaye yana aiko mata da sakon murmushi, ta koma cikin d'akin shima yabi bayanta, kallon ta ya shiga yi da yake ba hijab a jikinta nan ya hango ramar da ta yi, wuri ya samu ya zauna suka gaisa da d'an fara'a a fuskarta sannan suka shiga hira na yaushe gamo, abin motsa baki ta tashi ta d'auko masa cin-cin ne da meltina da kuma ruwan gora, ta ce.

"Yaya me zama ci na d'aura maka?"

Murmushi ya yi ya ce.

"Sha zamanki na taho mana da takeaway"

Tashi ya yi ya fita zuwa motarsa bai jimaba ya dawo rike da manyan fararen ledoji guda biyu ya dire su a gabanta, ya komawa ya zauna.

"Haba yaya baka gajiya da d'awainiya?"

"isshh ya isa haka, ko ba komai ke k'anwata ce kinga dole ne na yi miki balle kuma nan da wani lokaci ina sanya ran zaki zama mata ta"

Da sauri Zainab ta dago fuskarta tana kallonsa kamar mai nazari, bugun zuciyarta ne taji ya sauya numfashinta ya fara bugawa sauri-sauri, ta mai da kanta tana lallon k'asa, nan da nan Al'amin ya gano cewa akwai abin da ke damunta. Cikin nutsuwa ya kira sunan ta.

"Zainab me yake damunki?"

"Laa  me ka gani? ba abin da ke damu na fa"

Ta ce cike da wayencewa.

"A'a my Zee ban yarda ba, kinga yanda kika rame kuwa? gwara ki sanar min in da akwai matsala sai mune ma miki magani"

"Yaya na ce maka ba komai karatu ne kawai ya sani gaba na rame"

Ba yadda ya iya dole ya yarda amma a zuciyar sa bai gamsu da amsar ta ba. Haka suka ci suka sha sai misalin k'arfe 4 na yamma suka yi sallama ya tafi. Khalil yana kallon su lokacin da ta yi masa rakiya tana tafiya sai da ta yi waige-waige tana jin wani iri a ranta kamar Khalil yana kallonta. Tana komawa d'aki ta gyara ko ina ta gabatar da sallah la'asar, ta mik'e bata cire hijab d'inta ba ta d'auki waya da malullun d'akinta ta rufe sannan ta nufi bakin gate. Tafiya take yi a kafa ta rasa ina zata, can bayan makarantan su ta nufa kusa da wani ciyayi, mutane na wuce wa kad'an-kad'an ta samu wani dakali ta zauna, danne danne take yi a waya ta shiga tunani mai zurfi, zuciyarta duk ta takura kuka ta fashe dashi mara sauti tana yi tana share hawaye, iska ne taji yana busata sosai kasan tuwar lokacin damuna ce, hadari ya fara had'uwa. Waige-waige ta soma yi tana k'ok'arin tashi, idon nan nata ya kod'e saboda tsabar kuka, kamar ance ta juya bayanta sai taga mutum tsaye ya rungume hannun sa sai kallonta yake yi, ta zare ido waje, mamaki da tsoro ne ya ziyarce ta. Khalil ya sakar mata murmushi ya zagayo kusa da ita ya zauna yana kallon ciyayin da ke wurin, ita ma ta sunkuyar da kai kasa kamar mai nazari, sun d'auki kusan minti goma ba su cewa junansu komai ba, ita ce ta katse shurun, cikin dashewar murya ta soma magana

"Umm umm lafiya ka zo nan wurin?"

Ya Juyo da fuskarsa gareta ya ce.

"Kema lafiya kika zo nan?"

"To ai ni ce na rafa tambayarka, sannan kuma kaine ka sameni a nan din"

"To naji, yanzu me yasa ki kuka? sannan ma meyasa kika keb'ance ke kad'ai anan gurin, kuma me yake damunki?"

Tambayar ya zo mata a ba zata, sai ta shiga tunanin zuci.

'Ba dai dama tun d'azu yana nan wurin ba? wato ma har kukan dana yi ya gani?'

Ya katse mata tunaninta da kiran sunanta.

"Zainab"

A hankali ta dago fuskarta tare da motsa bakinta a hankali ta amsa.

"Baki bani amsata ba amma kin yi shuru kamar kina tunani"

Ta sunkuyar da kai kasa jikinta ne ya yi mata sanyi, nan take ta tuno da irin wulak'ancin da ta yi masa amma bai iya nuna mata ba sai ma nuna mata daya yi ya damu da halin da take ciki. Hawaye ne taji ya wanke mata fuska ta kasa dago ido ta kalle shi, cikin rawar murya ta ce.

"Khalil, na kasance mai babban laifi a gare ka amma sam baka iya nuna min b'acin ranka ba, saima nuna min wani kulawa na daban kake yi, a kwanakin da suka wuce ina cike da fargaban mu sake had'uwa saboda ban san irin matakin da zaka d'auka a kaina ba, amma a yanzu na tabbatar da ba haka kake ba, dan Allah ka yafe min, da ina ganin hukuncin dana d'auka maka shi ne dai-dai a she babban kuskure na tafka"

Ta karashe maganar da kuka, kallonta yake yi ba kifta ido, yana gasgata nadamar da ta yi, kuma zuciyar sa ta amshi hakan harma yake zargin ta karbi soyayyarsa cikin kankanin lokaci. Kukan da take yi sai yaji baya masa dad'i, yayi gyaran murya.

"Haba Zainab ki yi shuru ni Khalil na yafe miki, ki kwantar da hankalinki kuma ni sam banji zafin abin da kika yi min ba, haushin kaina naji nada kasance mai takura miki a baya, kuma wannan dalilin ne yasa nayi nesa dake ko zan iya cire sonki a zuciyata na barki kisha iska"

Da sauri ta dago idon ta da suke fal da hawaye.

"Nesa dani da ka yi shi ne abu mafi girma da muni daya jefani cikin tashin hankali da damuwa, dan Allah Khalil ina rokanka karka kuma nesa dani in ba haka ba wallahi zan shiga cikin wani sabon damuwa"

Kallonta yake yi cike da mamakin kalamanta bai taba zaton zai ji irinsu sun fito daga dakinta ba, shuru suka yi na minti biyar, hadari ne ya had'u sosai iska ya fara kad'awa sosai, mik'ewa ya yi.

"Zainab tashi mu koma cikin makaranta kinga ruwan nan ya kusa sauka"

Ta mike suka jera ba um ba um um. Har k'ofar d'akinta ya rakata ta bud'e kofa, ya ce.

"Zainab sai da safe"

Da sauri ta juyo ta kalle shi.

"Ban gane sai da safe ba, ka shigo mana"

"A'a ki barshi kawai nagode zanje gida yanzu"

"A'a ka shigo ka zauna kaga ruwan nan ya kusa sauka"

Ba yadda ya so ba dole ya shiga cikin d'akin, wannan shi ne karon farko da Khalil ya shiga dakin Zainab, kalle-kalle ya shiga yi d'akin ya yi matuk'ar burge shi ya tsaru dai-dai gwargwado, ga wani sanyin k'amshi mai rasha zuciya da yake bin bargonsa, bai san sanda ya yi ajiyar zuciya ba a hankali, a kujera ya zauna a takure ya kasa sakin jikinsa, kicin ta shiga ta debo masa abin motsa baki, kad'an yaci saboda bak'unta, TV ta kunna musu suna kallo ba wata hira suka yi ba sai dai ko wannan su da abin da yake sakawa a zuciyarsa. Ruwa ne ya tsuge kamar da bakin kwarya, sai nepa suka d'auke wuta wayarta ta lalubo ta kunna haske, sannan ta kunne rechargeable d'inta d'akin ya gauraye da haske. Haka suka yi shuru ba wani hira da suka iya yi saboda rashin sabo, ruwan ne yad'an tsagaita saka makon kiran sallah magrib da ake yi, mikewa ya yi ya ce.

"Zainab zan tabi masallaci"

"Zaka tafi ai ruwan bai tsaya ba"

"Ba damuwa ai tunda yayyafi ake yi"

"To shi kenan bari na baka lema ta"

Tashi ta yi ta d'auko masa sannan ta bud'e d'akin suka yi sallama da alkawarin in Allah ya kaimu gobe zai kawo mata leman. A wannan ranar daga Zainab har Khalil sunyi barcin farin ciki, ko wannansu da tunanin juna suka kwana.

Tun daga wannan rana Khalil da Zainab suka shak'u sosai, duk inda zasu a tare sannan suna gunadar da soyayya a tsaftace, Khalil shike yiwa Zainab cefane ta girka musu abinci kullun. D'akinta ya zamar masa wajen zuwansa, hatta Nuhu abokinsa shi ma wataran da shi suke hira daga nan shima ya cika tumbinsa.

*****
Sun fara shirye-shiryen exam na last semester, sun mai da hankali wajen karatunsu, tare da gudanar da soyayya mai cike da kauna da yarda, duk sunyi k'iba sunyi kyau hankalin su a kwance.

Wata rana da misalin sha d'aya na safe, Khalil suna d'akin Zainab shida Nuhu suna karin safe, ita kuma tana gefe sunata hira, sai suka ji ana yin nocking k'ofa, cikin sauri Khalil ya mik'e danya je ya bud'e d'akin, koda ya bude abin da ya gani ba k'aramin kad'a masa hanjin cikinsa ya yi ba, sai ya fuske ya dawo cikin d'akin, mai nocking k'ofar ya biyo bayansa cike da mamaki. Khalil ya zauna, Zainab na ganin bakon daya shigo hankalinta ya tashi, mik'ewa ta yi cikin damuwa da fargaba, murmushin tak'aici ya yi mata ganin yanda ta rikice lokaci d'aya, cikin rawar murya ta ce

"Yaya Al'amin sannu da zuwa"

Ya dakatar da ita da hannunsa.

"Bana buk'atar gaisuwarki, Alhamdulillah yau abin da kike yi a boye ya bayyana, haba biri ya yi kama da mutum shiyasa kike wulak'anta ni, ashe kin samu sabon farka ne, kin bani mamaki Zainab duk iya tarbiyya da su baffa suka baki a she a banza suka yi kina nan kina ai kata tsiya son ranki"

Cikin kuka da takaicin kalamansa ta ce.

"Ya isa Yaya, maganganun ka sunyi min yawa yana da kyau kafin ka yanke min hukunci ka ji ta bakina tukunna"

Cikin fad'a da d'aga murya ya ce.

"Me zan tsaya na saurara bayan abin da idona ya gane min ya isheni amsa"

"Da kata Malam yana da kyau ka sauraremu kafin ka yanke mana hukunci"

Cewar Khalil cikin saga murya.

"Kai ban sa da kai ba kaja bakin ka ka min shuru mutumin banza kawai, kai in k'anwarka ce kazo ka samu a haka zaka bari ne, dan haka kafin na yi kasa-kasa daku maza Ku fice a cikin d'akin nan mutanan banza kawai"

Cikin kunan rai Khalil ya ce.

"Sai dai kaine mutumin banza"

Ya karasa yana huci idanunsa sunyi jawur saboda bacin rai, Yaya Al'amin kansa ya yi yana son tsakumo Khalil, da sauri Nuhu ya shiga tsakaninsu ya ce.

"Dan Allah ku yi hakuri kar kuyi fad'a, munji munyi laifi ka yi hakuri"

Ya juya wurin Khalil.

"Kai kuma mu tafi ban son na k'ara jin kayi magana a nan"

Khalil ya yi murmushin yake.

"Ba zan bar wajen nan ba sai ya san matsayina a gunta"

"Matsayin ka na banza kai waye? Wallahi saina sa an d'aureka da duk abin da kake tak'ama dashi"

Cewar Al'amin. Zainab in banda kuka babu abin da take yi, ta shiga rud'ani.

"Ni ba kowa bane amma fa ka sani baka isa ka sanya a d'aure ni ba dan kai ba kowa bane face Mara tunani, sannan ka sani Zainab tawa ce wallahi babu wanda ya isa ya shiga tsakani na da ita sai Allah kad'ai"

Cewar Khalil yana huci. yana gama fad'an haka ya yi waje cike da b'acin rai. Al'amin ya bishi da kallon mamaki har ya fice, tare da maimaita kalmar.

'Zainab ta wace'

A cikin ransa. Nuhu ma yabi bayan Khalil ba tare da ya k'ara furta komai ba. Yaya Al'amin ya kai dubansa ga Zainab cikin d'aga murya ya daka mata tsawa.

"Maza ki had'a kayanki mu tafi Kaduna do min yau sai kowa sunji wannan bak'in labarin"

A tsorace jikinta na rawa ta d'auki hand bag d'inta tana kuka ta fita, key d'in d'alin ya amsa ya kashe duk kayan wutan d'akin ya rufe kana ya nufi motarsa tana biye da shi a baya. Haka suka kama hangar Kaduna ba shiri, Zainab banda kuka babu abinda take yi har suka isa kaduna

********* *********

*Kaduna*

Direct gidansu ya wuce da ita ya yi sa'a duk mutanan gidan suna nan, daya ke ranar weekend ne, har Yaya Ismail yazo da matarsa, sai Anty Binta itama da tazo yinin gida, Yaya Aliyu shima yana gida bai fita kasuwa ba, Baffa ma haka, Umma dama da Anty Jidda kullun suna gida.

Da salama ya shiga falon ransa a b'ace duk suka amsa cikin fara'a, ganin yanda fuskarsa yake yasa suka fara tambayar sa ko lafiya, duk hankalinsu ya tashi tunaninsu ko wani abu ne ya samu iyayan nasa.
Wuri ya samu ya zauna ba tare da ya amsa musu tambayoyin da suka jero masa ba, sun gaisa gaba d'aya, Yaya Aliyu ne ya ce.

"Kai wai lafiya muka ganka cikin wannan yanayin? Da fatan dai ba wani abu bane ya faru dasu Baffa?"

Murmushi ya yi wanda yafi kuka ciwo ya ce.

"Ba komai daga Zaria nake yanzu haka ko gida banje ba nan na tawo"

Baffa ne ya ce.

"To da fatan ba Zainab d'in ba ce ba tada lafiya?"

Murmushi ya kuma yi.

"Tare da ita nake, yanzu haka tana waje taki shugowa, Ku barta in ta gama nuk'u nuk'unta zata shigo"

Yana gama wannan bayanin yaja bakinsa ya yi shuru. Anty Jidda, Anty Binta, Anty Ameena, mik'ewa suka yi dukansu suka nufi farfajiyar gidan suga me ya hanata shigowa.

Bayan su Anty Binta sun fita, sun sameta a zuk'unne tana kuka mara sauti hawaye kwance a kuncinta, anty Jidda ce ta tada ta tsaye ta ce.

"Zainab lafiya meyasa baki shigoba?"

"Yar uwa lafiya? ina ganin mu shiga ciki tukunna, sai mu saurari duk kanin bayani wajen Al'amin"

Cewar anty Ameena. Shawaran ta suka d'auka, sai suka d'unguma zuwa falo. Suna shiga suka samu wuri duk suka zauna, Zainab kusa da Umma ta zauna sai kuka take yi, ta kai kusan minti biyar a haka, k'aran fanka ne ke kad'awa sai kuma sautin kukanta, sannan ta tsagaita kukan ta gaida su Baffa da sauran wanda suke falon. Yaya Aliyu ne ya kai dubansa ga Al'amin ya ce.

"Al'amin gata ta shigo kai muke saurare"

Ya yi murmushi da gyaran murya, ya fara basu labari tun daga lokacin daya fara samun sauyi ga Zainab, har zuwa yau daya ga su da Khalil a dakinta, Duk suka fara salati. Wannan labari ba

k'aramin tada hankalinsu ya yi ba tare da mamaki, Umma ce tabce.

"Haba Zainab duk iya tarbiyar da muka baki, ki rasa wanda za kiyi abota da su sai maza, shin ma su waye wannan rayan? wanda a sani na dake ko kawaye mata baki da su a nan balle ma ace maza"

Baffa ne ya cab'e maganar da cewa.

"Amma Zainab kin bani kunya kuma kin bani mamaki, banyi zaton haka daga gareki ba, waye wannan yaron da har yake ik'irarin ke tashi ce?"

Kukan Zainab ya k'aru ta ce.

"Dan Allah Baffa ku yafe min nasan na yi kuskure, amma dan Allah Karku rabani da Khalil wallahi a yanzu shi ne zab'in zuciyata, in kuka ce zaku rabani da shi kamar zaku rabani da rayuwa ta ce, na riga na yi sabo da shi

Kukanta nata ya sirk'eta sai ta kasa k'arasa maganar. Yaya Ismail ne ya mik'e cikin fushi ya fara fad'a yayo kanta kamar zai mareta, da sauri Al'amin ya tare shi da cewa.

"Yaya Ismail bai kamata ka duketa ba"

Ya koma ya zauna yana huci. Anty Jidda ta ce.

"Kwarai bai kamata a ce za'a bigeta ba, ai Zainab ta wuce duka, dan haka ke muke saurare ki bamu labarin yadda aka yi kika yi sabo da shi Khalil din"

Share hawayenta ta yi ta soma bayani tun daga farkon haduwarta da Khalil har zuwa ranar yau, sai dai bata gaya musu cewa sunyi maganar da Anty Jidda ba, ita kanta Anty Jidda taji dad'in yanda Zainab bata sanya ta ciki ba. Kuka ne ya sirketa ta cigaba da rerawa. Yaya Aliyu saboda damuwa ya kasa magana haka ma Baffa, Umma ko tagumi ta rafka, su Anty Binta ko shuru suka yi kamar ruwa ya cinye su, Al'amin kuwa sun kunyar da kai ya yi kasa zuciyar sa na masa rad'ad'i. Yaya Ismail ne ya mike ya zare belt din dake jikinsa, ya nufota, da sauri ta mike jikinta na rawa ta fara ja da baya tana fad'in.

"Yaya dan Allah ka yi hakuri karka bigeni ba zan sake ba na tuba"

Da taga dai dagaske yake yi sai ta arce d'akinta a guje, tana k'ok'arin rufe k'ofa ne ya banko k'ofar ya fara zuba mata belt d'in, dukanta yake kamar zai kashe ta, da sauri su Anty Binta suka k'araso suka ceceta.

"Isma'il ai ba duka ya kamata ayi mata ba, tunda Zainab ba yarinya bace, kamata ya yi a bi abin a hankali"

Anty Amina ce ta ke fad'ar haka. Yana huci ya bar d'akin, kusa da ita suka zauna suna lallashinta, A falo kuwa su Baffa suna cike da jimami, a nan dai suka tattauna maganar kana ya ce.

"Al'amin ya sanar da Baffa Sani yana son ganinsa da daddare, da haka falon ya watse cikin da damuwa.

*******

*ZARIA*
Khalil ne kwance cike da damuwa yana ganin kamar an raba shi da Zainab kenan, yana ta juyi a kan gado ya dafe kansa, can sai ya barke da kuka, Nuhu ne ya ke lallashinsa.

"Haba Abokina kamar ba namiji ba, ka yi hakuri ka amsa k'addararka, mu cigaba da Addu'a, in Zainab matar kace duk yadda zasu so rabaku in Allah yanu fa sai ka aure ta"

Idonsa ne ya dago wanda suka yi jajir saboda tashin hankali ya ce.

"Ni bana tunanin zasu iya barinmu mu cigaba da soyayya, ina ganin kamar wannan tafiyar da suka yi da ita sunyi sanadiyyar da zasu raba mu ne, domin na lura family d'insu suna da wani tsastsauran ra'ayi, nasan dai Zainab tana sona ina sonta, sannan shi wannan Al'amin d'in da kake gani shi ne wanda iyayenta suka zab'a mata a matsayin mijinta, a lokacin suna musu kallon soyayya suke yi wanda ita soyayya take masa na 'yan uwantaka saboda Zainab a kaina ta fara sanin so, haka nima a kanta ne na fara sanin so"

Nan dai Nuhu ya cigaba da ba shi baki akan ya yi hakuri, yaso ya bita amma Nuhu ya hana shi.

"Ka kwantar da hankalin ka, kaga yau asabar dole ta dawo gobe insha Allah, in kuma bata dawo ba dole ta dawo Monday dan suna da lectures kuma ita ma tasani, kuma ni ina ganin ba zasu tab'a yanke mata karatunta ba, saboda ta yi nisa tunda a yanzu muna shirin zana exam ne na last semester"

Dole yasa Khalil ya yi hakuri ya mik'a lamarin ga Allah.

Da daddare duk sun hallara a falon gidan har dama wasu dattijai na family d'insu duka, bayan sun gaisa ne, sai Baffa ya umarci matan dasu basu guri zasu tattauna, haka Umma ta tattara surukanta suka koma falon d'akinta suka cigaba da hira, Zainab dai na takure ba um ba um um, kusan kowa ya fita harkanta saboda su Anty Jidda sunyi lallashin har sun gaji taki cin abinci sai kuka da take yi.

A falo su Baffa sun tattauna sosai wanda daga k'arshe suka yanke hukunci akan.

*Rahma ce*
[10/17, 11:19 AM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 13 ~ 14_*

A falo su Baffa sun tattauna sosai wanda daga k'arshe suka yanke hukunci akan cewa tunda Zainab zata zana jarabawa to sun sanya auren ta da Al'amin nan da wata d'aya, lokacin ta kammala jarabawa da sati d'aya za ayi bikin. Baffa ya sanya aka kira su Umma, nan ya fada musu abin da suka yanke, sannan suka d'aura da yi mata fad'a sosai, daga k'arshe suka d'aura da nasiha, Zainab ce ta mike cike da tashin hankali ta sanya hannu a bakinta ta rufe gudun kar kukanta ya fito, da gudu tabar falon tana kuka mai tsuma zuciya. Haka dai taron ya watse wasu najin dad'i wasu kuma suna cike da damuwa.

Zainab da Khalil yanda suka ga rana haka suka ga dare ba wanda ya iya runtsawa, Khalil ya kira ta a waya yafi a k'irga amma wayar a kashe.

****** ******

*Washe gari.*
Da yamma Yaya Ismail ne cikin shirin komawa Kano tare da matarsa, sun kammala shirinsu sannan suka taru a falo aka k'ara yiwa Zainab fad'a sosai, sannan aka bata kud'i da sauran abin buk'ata, tare suka tafi da Yaya Ismail zasu sauketa a makarantarsu. Tun a hanya yake mata nasiha har suka kai cikin makarantar, parking ya yi suka rakata har d'aki sannan suka juyo suka kama haryar Kano.

Khalil yana ganin saukarsu a mota, sai ya gyara zama yana jiransu Yaya Ismail su tafi. Sai da yaga k'ulawar motar su sannan ya nufa d'akin nata, bugu d'aya ya yiwa k'ofar ta zo ta bud'e masa ya shiga, zama suka yi suna kallon juna, Zainab ta katse shurun ta gaida shi, ya amsa cike da kulawa, daga bisani ta d'aura da ba shi labarin duk abin da ya faru da suka isa gida har da dawowarta yanzu. Hawaye ne mai zafi yake fita a idon Khalil.

"Zainab kin amince zaki rabu sani?"

Cikin shasshekar kuka ta ce.

"Khalil ya zanyi kaga dole yani musu biyayya"

"Shi kenan tunda kin zab'i rabuwa dani"

Bai jira mai zata ce masa ba ya mik'e ya isa bakin k'ofa zai fita, da sauri Zainab ta je da rike rigansa ta baya.

"Ba zan iya rabuwa da kai ba Khalil ina sonka, mafita zaka samar mana, na dank'a maka ragamar rayuwa ta"

Fuskarsa cike da hawaye ya juyo da murmushi, hab'arta ya d'ago suna kallon juna.

"Dagaske kin yarda in samo mana mafita?"

"Eh na amince"

Murmushi ya yi ya cire farin hankacif ya guge mata hawayenta sannan ya goge nashi, ya kama hannunta ya kaita har zuwa bakin gado ya zaunar da ita, ya zuk'unna a gabanta, ya shiga bata magana mai kwantar da hankali, cikin kankanin lokaci ya fara sanya ta dariya har ta soma mancewa da damuwar da take ciki, ganin hakane yasa ya mike ya ce.

"Zan tafi kano yanzu ki sanya ni a Addu'a"

"Meyasa zaka tafi?"

"Saboda ke zan tafi, zan sanar ma iyayena domin su zo su nima min auren ki"

Cike da jin dadi ta k'arfafa masa gwiwa da maganganu masu dad'i, kana ta yi masa Addu'a ya wuce.

****** ******

*KANO*

Sai bayan magarib Khalil ya isa Kano, direct gidansu ya wuce yaje ya samu Baba Husain da Inna, ya yi musu bayanin maganar daya kawo shi, cike da mamaki Baba Husain ya kalle shi saboda bai taba tsammanin zancen aure daga bakin Khalil ba, fad'a ya fara yi masa sannan ya nuna rashin amincewarsa, haka Inna ma fad'an ta yi masa ta goyi bayan Baba Husain, Khalil na kuka yana musu magiya amma fir suka k'i amincewa k'arshe ma Baba Husain kuka ya sanya yana cewa.

"Saboda kaga bamu muka haifeka ba shiyasa zaka k'i bin umarnin mu ko, na d'auke ka d'an ciki na amma kai ka nuna mana bamu isa da kai ba"

Cike da tashin hankali Khalil ya fara basu hakuri da amincewar ya janye maganar kuma ba zai sake yi musu shi ba, Baba Husain yaji dad'in haka, dama ya yi masa kukan ne saboda ya janye,

lallashinsa suka yi tare da nasiha, ya mik'e ya yi musu godiya. D'akinsa ya shiga ya zauna, kuka ya k'are masa sai ajiyar zuciya, tunani yake yi shin ta ina zai bullowa lamarin? Mikewa ya yi a zabure ya lek'o, sai da ya tabbatar ba kowa a tsakar gidan ya lallab'a ya fita saboda karsu hana shi komawa Zaria a ranar, tasha yaje ya hau motar Zaria, basu suka isa ba sai goma da rabi na dare.

Direct makaranta ya nufa, harta kwanta taji ana buga mata kofa, da kamar baza ta bud'e ba sai ta mik'e ta isa bakin kofar ta ce

"Waye ne?"

Cikin dishewar murya ya ce mata.

"Khalil d'inki ne"

Da sauri ta bud'e k'ofar ya shigo, binsa da kallo ta yi cike da mamaki.

"Baka samu zuwa Kano din bane?"

guntun murmushi ya yi.

"Naje yanzu na dawo ko gida ban isa ba nan na duro"

Kallon mamaki ta bishi da shi, wuri suka zamu suka zauna, cike da damuwa ya fara bata labarin zuwansa Kano da yadda suka kwashe da iyayensa, kuka ne ya kubce musu baji ba gani, da kyar Khalil ya iya lallashin kansa sannan ya rik'a lallashinta da kalamai masu dad'i, Nuhu ne ya buga kofar d'akin, Khalil ya mik'e ya bud'e masa. Kafin ya yi masa magana ya ce.

"Haba Khalil tun d'azu ina nimanka ashe kana nan, cewa na yi bari nazo na duba ka ko kana nan"

Murmushi ya yi masa sannan ya c.

"Zauna abokina yi hakuri wallahi bana cikin nutsuwa ne"

Zama suka yi Khalil ya bashi labarin halin da suke ciki, damuwa ne ya bayyana a fuskan Nuhu ya shiga basu hakuri, sannan ya ce.

"Akwai mafita d'aya da zan baku kuma ita ce dama ta k'arshe da zaku yi amfani da shi, amma fa sai kunyi min alkawarin kun daina kuka, kun cire damuwa akai sannan kun mai da hankali akan karatunku har mu kammala exam, sannan kuma ku dage da Addu'a"

Cikin sauri dukansu suka ce sun amince da hakan, Nuhu yayi murmushi ya ce.

"Ku matso kuji"

Nan suka matsa ya yi musu bayanin komai, bayan ya gama, murmushi ne ya ziyarci fuskokinsu da alama dai sun gansu da bayaninsa.

*******

Tun daga wannan rana Khalil da Zainab suka saki jiki, sun mai da hankali sosai wajen karatunsu. A bangaren Kaduna kuwa shirye-shiryen biki suka yi ba kama hannun yaro. Ta bangaren Kano kuwa su Baba Husain sun saki jiki da tunanin Khalil ya hakura da zancen auren, tunda suka ji shuru kuma suna waya bai sake d'auko musu zancen ba.

*****

Ranar Juma'a ya kama ranar ne su Khalil suke kammala exam d'insu, sun fito paper da misalin 11 na safe Zainab tana d'akin ta, da yake ita tun ranar labara ta gama nata exam d'in, zaman jiran su Khalil take su kammala nasu. Khalil ne ya shigo d'akin cikin shigar manyan kaya shadda sky blue yasha aiki tare da sanya hula bak'ar dara da takalmi bak'i, agogo golden ash, yayi kyau sosai. Ya zamu Zainab ita ma zaune tana zaman jiransu, sanye take da less sky blue mai zanen fulawa fari, ta sanya babban gyale bak'i da takalmi da jaka farare, sai kamshi take yi kamar Amarya, ta yi kwalliya sosai ta yi ta kyau. Khalil kafeta ya yi da ido yana k'are mata kallo gaba daya hankalinsa baya jikinsa, a ransa yana yaba kyau da Allah ya yi mata, Nuhu ne ya lek'o yana cewa.

"Haba Khalil kun barni tun dazu sai jiranku nake yi a cikin mota ku fito mu tafi mana"

"Gamu nan zuwa"

Khalil yace yana yar dariya. Bayan sun fito mota suka shiga suka fita daga cikin makarantar, motoci ne na dalibai maza da mata suke biye dasu a baya, har zuwa cikin Zaria city.

Sun yi parking a k'ofar wani gida inda Khalil ya fito shi da Nuhu, suna k'ok'arin yin sallama a gidan sai ga wani Dattijo ya fito daga cikin gidan sanye da manyan kaya da alkebba, suka tauguna suka kwashi gaisuwa, yanda Malamin ya amsa da alama ya san su, ya ce.

"Khalilu har kun iso?"

"Eh Malam mun iso"

"To masha Allah, Ina ita yarinyar take?"

Nuhu ya ce.

"Tana cikin mota"

"Madallah, to sai ta fito ta shiga cikin gidan ko"

Cikin hanzari Nuhu ya kirata tare da sauran students mata da suka rakosu, suka gaida Malam sannan suka shiga cikin gidan, sun samu mutane a ciki ba laifi yara nata wasa, wasu nata cin abinci da alama dai wani k'aramin shagali a ke yi, sun gaisa da matan gidan aka ware musu d'aki na musamman suka shiga ciki, abinci ne aka kawo musu.

A waje kuwa Malam Isah mai hadisi ne da tawagarsa, suka tsallaka babban masallacin dake kallan gidansa, mutane sun fara taruwa don gabatar da sallar Juma'a, suma su Khalil duka shiga ciki. A haka dai jama'a suka taru sosai har a wajen masallaci kana aka gabatar da sallar Juma'a.

Su Zainab suna ciki, banda fad'uwar gaba babu abin da take yi sai Addu'a da tasbihi, hakanan taji hankalinta ya tashi, sauran friends d'in ta ne suka ci abinci suna ta hira amma ita ta kasa cin komai sai kallonsu take yi. Tana cikin wannan yanayi ne, suka ji sanarwar an d'aura auren Zainab da Khalil bisa sadaki dubu Hamsin lakadan ba ajalan ba. Gabanta ne taji ya fadi rass sai kawai taji hawaye na bin kuncinta. Matan dake cikin gidan ne, naji suna ta gud'a suka lek'o d'akin dasu Zainab suke ciki, tare da ran gad'a gud'a suna sanya albarka, wanda basu san amaryan ba sai lek'ota suke yi friend d'in ta suna nuna musu ita, suma da suke d'akin suna gud'a tare da shewar farin ciki.

Bayan komai ya lafa, da misalin k'arfe Hudu, Malam Isah mai hadisi ne da su Khalil suna zaune gabansa cikin zauren gidan, sannan ya aika aka kira masa Zainab, ta fito sanye da lullubi akanta, zama ta yi gefen Khalil ta gaida Malam, nan ya sanya musu albarka tare da addu'o'i na samun zaman lafiya da zuria d'ayyiba, ya mikawa Khalil certificate d'in aurensu, sannan ya ce

"Ga nawa da kace na rike a guna, sannan zuwa bayan Sallan Magariba sai ka zo ka d'auketa, yanzu ni na gama nawa, Allah ya muku Albarka, zaku iya tafiya"

Nan suka yiwa Malam godiya sannan Khalil ya ajiye masa kud'i a gabansa wanda shima bai san adadinsu ba ya ce.

"Ga wannan aci goro"

Malam ya yi godiya shima, kana Zainab ta koma cikin gidan, shi kuma suka wuce da abokansu harda matan ma suka tafi dasu cikin makaranta, Zainab kad'ai suka bari a gidan.

Bayan sun isa makaranta suka yi musu godiya suka sallami kowa. Khalil da Nuhu d'akin Zainab suka wuce da yake key d'in na hannun sa, kayanta suka kwashe, dama ta gama shirya wanda zata d'auka da sauran kayan kicin sai kuma kayan sawanta da littafanta, suka sanya a mota suka bar sauran kayan a ciki suka rufe, sannan suka wuce gidan khalil suka shirya kayan ko

wanne suka sanya shi a mazauninsa, abin mamaki har da fanti ya yiwa d'akunan sai kamshi suke yi kamar dama sun shiryawa abun, sun kai kusan karfe shida na yamma suna aikin, bayan sun gama suka share gidan tas kana Khalil ya yi wanka ya sanya farar shadda sai walk'iya yake yi, suka kama hanyar zuwa gidan Malam Isah mai hadisi.

Sun isa gidan dai-dai ana kiran sallar Magrib, suka gabatar da Sallah a Masallaci, sannan suka dawo k'ofar gidan, sallama suk ayi sannan suka shiga cikin gidan, Malam ne ya amsa tare da yi musu iso suka shiga cikin dakin da Zainab take zaune, nasiha ya yi musu sosai akan zaman aure kana ya sallame su. Akwati naga an fito da shi mai kyau trolley mai guda biyu da kit, a bayan motarsu aka sanya sannan Zainab ta shiga baya Khalil ya zauna gefen driver, sai Nuhu ne ya jasu suka wuce.

Koda suka isa gidan suka shiga ciki, Nuhu ya yi musu sallama da alkawarin zai zo da safe. Khalil ya yi masa godiya bisa ga taimakonsu da ya yi, ita ma Zainab d'in godiya ta yi masa kana ya wuce.

Khalil da Zainab sun zama mata da miji bisa auren sunnah, sai dai dukansu suna cikin fargaba da damuwar abin da hakan zai haifar musu a nan gaba. Zainab ta yi kuka sosai har take jin dama bata aikata haka ba, tunanin iyayenta take yi da yadda zasu d'auki wannan lamari, haka shima Khalil, sai dai in ya tuna yana tare da ita sai yaji natsuwa. A wannan dare a takure suka kwana, da tunani kala-kala har barci b'arawo ya sacesu.

****** ******

*Washe gari*
Da misalin karfe tara na safe Nuhu yazo, suka gaisa kana suka yi breakfast, wata jaka na ga ya bud'e ya ce.

"Ga photocopy din certificate dana yi, yanzu kune nake jira"

Khalil ya kalli Zainab ya ce.

"Sweet Zee ga shi ya kawo, Amma bamu rubuta letter ba"

Ta yi guntun murmushi da bai kai ciki ba ta ce.

"To bari na rubuta nawa

Nuhu ya mika mata farar peper da bairo, ta karba ta fara rubutu kamar haka.

*_ASSALAMU ALAIKUM_*
*_"Baffa da Umma da kuma sauran 'yan uwana ina miko gaisuwa gare ku tare da fatan alkhairi. Na zama mai babban laifi agareku, ku yafe min hakika nasan ban kyauta muku ba, amma gaba

daya na d'auke shi k'addarata ce. Wannan sako da na yi muku nasan zai girgizaku amma ku yafemin. A jiya Ranar Juma'a aka d'aura min Aure da Khalil bisa sadaki dubu Hamsin, kuma ya ba ni tare da kud'in gaisuwa da kayan sa rana dubu Hamsin duka dubu d'ari, sai akwati biyu da kit ya zuba kaya iya k'arfinsa, sannan ya kama mana haya a nan cikin Zaria. Malam Isah mai hadisi shi ne ya yi min waliyyi shi kuma na'ibinsa ne ya yiwa Khalil waliyyi._*

Nan ta rubuta musu labarin yanda iyayen Khalil suma suka ki amincewa da k'udurinsu, sannan ta d'aura da cewa.

*_"Mun yanke wannan hukuncin ne saboda mu gujewa sab'on Allah sannan bazamu iya guduwa ba, shiyasa muka ni mawa kanmu mafita saboda in bamu aure junan mu ba to tabbas za a iya rasa d'aya daga cikin mu, Allah shi ne ya had'a wannan soyayya, kuma munyi soyayya mai tsafta da k'aunar juna cikin Aminci, mun gujewa sab'on Allah ne shiyasa muka yanke hukuncin muyi aure dan cikar burinmu. Sannan kar kuga laifin Malam Isah mai hadisi akan ya d'aura mana aure, saboda bamu sanar masa da ainihin labarinmu ba. Tun lokacin da muka sanar ma juna rashin amin cewarku muka shiga damuwa, daga karshe muka yanke hukuncin mu yi aure, tun daga wannan lokacin ne Khalil ya bukaci kudi masu tsoka a gun iyayensa, kuma sun ba shi ne bisa dalilin ya ce zai yi amfani dasu ne wajen hidimar karatunsa, wannan ne yasa muka isa wurin Malam da tai makon Abokinsa Nuhu shi ya yi mana hanya, muka je a matsayin Khalil maraya ne ya rasa iyayensa shi ke rik'e da kansa, sai kuma ni a matsayin na musulunta ne kuma nabar iyayena saboda sun mini barzanar kashe ni. Da wannan bayani muka je gareshi harya d'aura mana aure dan mu gujewa aikin shaid'an. Dan haka ina mai rok'anku gafara wallahi So ne yasa muka aikata haka, Ku yafe mana gwiwowinmu a k'asa. Har abada ba zan daina kuka ba har sai kun yafe min laifin dana muku. Ina son ku iyayena da 'yan uwa na, har abada ni taku ce. Insha Allah zan dawo gareku nan ba dad'ewa ba, amma sai na tabbatar da zuciyarku ya yi sanyi bisa ga laifin da muka aikata_*

_Nice 'yarku_
*Zainab Ahmad Tanko Mai Kanti*

Khalil ne ya karb'a ya karanta sai da kwalla ya zubo masa ya girgiza kai, kana ya mik'awa Nuhu ya amsa shima ya karanta damuwa ne a fuskarsa, haka ya nad'e letter tare da certificate d'in ya sanya a wata jaka. Shi ma Khalil ya amsa ya rubuta nashi letter kamar yanda Zainab ta rubuta, sai dai shi ya bambanta wasu wuraren, yana gamawa ya ninke ta ya bama Nuhu.

******

Sako ya isa Kaduna, mai gadi ya shiga falon Umma da sallama ya samu Anty Jidda tana yankan alayyaho, Umma kuma tana zaune suna hira, sun amsa masa sallamarsa ya gaida su, sannan ya karaso kusa da Anty Jidda ya mik'a mata sakon Zainab, ta amsa cike da mamaki, sai ya fita, kiciniyar bud'e jakan take yi sai ga Yaya Aliyu ya shigo falon...

*Rahma ce*

[10/19, 9:53 AM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 15 ~ 16_*

Ta ciro abin da ke cikin jakan sai taga paper guda d'aya da certificate, a lokacin yaya Aliyu yana magana da Umma, salati a tsorace suka ji Anty Jidda ta saki, jikinta na rawa ta mik'e tana fad'in.

"Baban Sadiq kalla ka gani sak'o ne Zainab ta aiko da shi"

Cikin hanzari ya karb'a, abin da ya gani shima ya girgiza shi, zufa ne yaji yana keto masa, bugun zuciyarsa ya k'aru.

"Anya wannan sakon Zainab ta yi shi kuwa? muga dai dayan paper"

Ta mik'a masa ya amsa ya fara karanta wasik'ar da k'arfi su Umma suna saurare,  Umma ta kagara akai karshen labarin dan ta tambayesu akan shin anya Zainab ce kuwa? kan ya gama karantawa zufa ya lullub'eshi, Anty Jidda kuwa kuka ta fara yi, Umma kuma saboda tsabar bak'in ciki ta kasa magana sai kukan zuci. Duk suka zauna jugum-jugum kamar anyi musu mutuwa, suna cikin wannan halin ne sai ga Baffa ya shigo, ganin su da ya yi cikin wannan yanayi sai ya shiga tambayarsu.

"Lafiya na ganku a haka?"

"Lafiya lau Baffa zauna tukunna"

Cewar yaya Aliyu, Baffa ya saki guri ya zauna, nan take Yaya Aliyu ya shiga karanta masa sak'on Zainab, bayan ya gama ya nuna masa certificate d'in auren nata, Baffa yaji kansa ya sara zufa na keto masa, ya shiga jero salati yana ta'ajibin lamarin, sai a lokacin Umma ta samu halin yin kuka mara sauti kamar anyi mutuwa, basu tab'a tsammanin haka daga Zainab ba. Yaya Aliyu ya kira Ismail ya fara sanar masa abin da ke faruwa, shima salatin ya yi ya ce gasu nan zuwa sai ya kwashe wayar. Ya kuma kiran Al'amin ya shai da masa, kana ya kira Binta ita ma ya fada mata, dukansu sunyi mamakin lamarin mai cike da tsantsar damuwa.

********

*A KANO*

Nuhu da kansa yaje ya kai sakon Khalil, ya bama wani yaro ya kai cikin gidan su Khalil d'in, kan

yaro ya fito ya shiga mota ya juyo zuwa Zaria.

Baba Husain yana zaune a baranda shi da Inna suna hira, da yake ya tashi da ciwon kai shiyasa bai samu zuwa kasuwa ba, yaron ya shiga da sallama ya gaishe su kana ya mik'a masa sak'on da Nuhu ya ba shi.

"Gashi wani mutum ya bani a waje wai Khalil ya ce a kawo maka"

Baba ya amsa.

"Sannu yaro mu je daga ko waye ya aiko"

Ko da suka fita ba alamar mutum a wajen, sai zanen tayar mota wanda ya nuna mota ta tsaya a gun, Baba ya sallami yaron, ya shiga gida cike da mamaki yana labartawa Inna, ya zauna ya bude jakar ya ciro abin da ke ciki ya bud'e wasikar ya shiga karantawa a fili Inna tana saurarensa, mamaki ne ya bayyana a fuskansu har ya gama karantawa, salati suka shiga yi Inna harda tafa hannu tana rik'e hab'a, murmushi ya yi ya girgiza kai.

"Ka haifi da baka haifi halinka ba yaran zamani kenan, ban tab'a tunanin haka daga gareka ba Khalil"

"Ai Malam ya ga dan bamu muka haife shi ba shiyasa"

"A'a karki ce haka, yau ko da Hassan na raye da Halima tabbas haka zai yi, bana zargin dan bamu muka haife shi ba, kawai dai son zuciya ne da kuma kuruciya"

Inna ta yi murmushin takaici.

"Shiyasa ya karb'i kud'i da yawa a she ga abin da zai aikata, ni dama na yi mamakin kud'in da ya tambayeka, na ce wani irin karatu ne haka mai cin kud'i, a she da walakin goro a miya"

Nan dai suka cigaba da tattaunawa cike da alhini, Baba hassan ya mik'e ya ce zai je ya sanar da Mahaifiyarsu halin da ake ciki.

*******

*KADUNA*

Bayan sallah la'asar falon gidan cike yake da wannan dangi, na nesa duk sun zo, Baffa ne ya umarci Yaya Aliyu daya karanto sak'on da Zainab ta yi, cikin nutsuwa ya fara karantowa, tun kan ya gama falon ya hargitse da salati, Anty Binta sai kuka ita da Anty Ameena, ya nuna musu certificate d'in aure wanda hakan yasa dole suka gasgata lamarin. Shuru ne ya ratsa falon na tsawon minti biyar sai karar fanka ke tashi. Yaya Al'amin ne ya barke da kuka yana fad'an.

"Haba Zainab da nasan zaki iya aikata haka dana hakura kin aure shi, yanzu kin kyautata mana kenan kin rabu da danginki kin kama namiji da baki san asalinsa ba..."

Kukan ne ya sirk'e shi ya kasa karasa maganar, yaya Ismail kuwa ya fara masifa kamar zai ari baki ya tsine maya, nan dai Abba Iro ya ce ya yi shuru ba lokacin fad'a bane tunda ta riga ta aikata, ya cigaba da cewa.

"Yanzu abin da za ayi kai Aliyu da Ismail da kai Al'amin Ku tashi kuje Zaria Ku bincika cikin makarantar, tunda an kira wayarta a kashe sai...."

Bai k'arasa maganar ba Baffa ya katse shi da cewa.

"Malam Sani ai ko sunje ba zasu gansu ba a yanzu dan sun gama jarabawa, ina ganin muyi hakuri mu amshi k'addarar daya samemu, sai mu d'aura da yi mata Addu'a, Allah ya shirye su gaba d'aya, yasa su gane sun tafka kuskure"

"Hakane, ka kawo shawara mai kyau zamu sanya ta a Addu'a Allah ya mai do da hankalinta gida, a ganina kamar da asiri a cikin lamarin kamar yaron nan bai barta haka ba"

Cewar Abba Iro.

"Yaya Iro son zuciya ce kawai, amma bana tsammanin da asiri, ai jiki magayi"

Cewar Umma. Yaya Ismail ne ya gyaran murya ya ce.

"Baffa ni kam ba zan barshi ba wallahi sai ya san ya aikata mana haka"

"Ismail meye na d'aukar zafi? ai kar kaga laifin yaron, ance nake shi ke bada kai, dan haka laifin na gun 'yar uwarka, daga yau na rufe wannan maganar kowa ya cigaba da al'amuransa"

Nan dai suka cigaba da tattaunawa, daga k'arshe suka rufe taron da Addu'a.

Tun daga wannan rana suka bar zancen Zainab kowa ya cigaba da harkansa, Anty Jidda da Umma suke wayan kiranta a waya basa damu, sunyi har sun gaji sun hakura sai lokaci lokaci suke nimanta ko zasu dace. Wannan zuri'a Haka suke kwana su tashi cikin wannan bak'in ciki. Al'amin har rashin lafiya ya yi haka dai ya gama jinya ya warke amma sonta yana nan a zuciyarsa.

********

Su Zainab sun angwance cikin damuwa da fargaba, Khalil mutum ne mai barkwanci da hakane

ya samu har Zainab ta saki jiki da shi, sai dai in ta tuna da 'yan uwanta sai ta yi kuka mai isarta daga karshe ta yi hakuri dan kanta. Rayuwar kad'aici har ya bi jikinsu, duk lokacin da suka yi hutun makaranta basa iya zuwa gida a nan gidansu suke hutunsu har ya k'are su koma, sai dai suna waya da 'yan uwansu. Haka suka cigaba da rayuwa da dad'i ba dad'i har tsawon wani lokaci.

******      ******

*BAYAN SHEKARA D'AYA*

Lokacin Zainab tana da tsohon ciki haihuwa yau ko gobe, tana zaune a d'akinta da yake sunyi hutun makaranta, wayarta ne ta soma ringing bugu biyu ta d'auka Anty Jidda ce ta kirata, ta sanar mata da haihuwar Anty Ameena ta samu d'iya mace ranar labaraba, hawaye taji yana gangaro mata, ta fara shasshekar kuka, Anty Jidda ta ce.

"Dad'i na dake in an kira ki a waya sai kin wa mutum kuka, ni dai ki yi hakuri insha Allah nan da kwana biyu zamu je Kano"

"Shi kenan Anty in kunje ki gaidata"

"Zata ji insha Allah, ya naki jikin?"

"Da sauki, k'afa ta ce dai ta kunbura"

"To Allah ya kara sauki ya rabaku lafiya"

"Ameen nagode"

Sai suka yi sallama. Nan take Zainab ta kira Umma ta gaisheta ta yi mata barka, haka ta kuma kiran ita Anty Ameena ta yi mata barka.

A ranar suna yarinya taci sunan Nana Khadija, haka suka ci suna suka gama babu Zainab, a ranar taci kukan kewar 'yan uwanta, ta san da tana gida da da ita za'a yi wannan suna, da kyar Khalil ya lallasheta.

******

Ranar Juma'a da misalin k'arfe tara na dare ta fara nak'uda gadan-gadan, cikin tashin hankali Khalil ya d'auketa sai asibiti, nan suka kaita d'akin haihuwa da misalin sha d'ayan dare ta haifo 'yarta mace kyakkyawa mai kama da ita, Khalil ba k'aramar murna ya yi ba. Haka suka kwana a asibiti, da sassafe Zainab ta kira Anty Jidda ta gaya mata cike da murna taje ta sanarwasu Umma, ba yabo ba fallasa haka dai suka ce Allah ya raya, Anty Jidda hakan bai mata dad'i ba jiki a sab'ule tabar falon, haka ta shiga kiran dangi tana sanar musu, kowa dai da irin yadda ya nuna murnarsa, wasu sunyi Addu'a wasu ko ajikinsu. Anty Ameena ce da Anty Binta ne kawai suka danyi murna sosai da Inna Kulu. Umma ta kira Zainab ta ce ta shirya kayanta gasu Anty

Jidda nan a kan hanya zasu dawo da ita gida, ba musu ta aminci. Khalil haka bai masa dad'i ba amma amma yadda suka nuna kamar sun hakura ne, bai mai dasu gida ba ya barsu a asibiti, yaje gida ya had'a mata kayanta dana Baby ya kwaso su, ya kawo asibiti dan yasan da wuya suce zasu gidan Isu. Ya kira gida ya sanar da su Baba Husain, sun yi murna suma ba yabo ba fallasa sannan suka yiwa yarinya Addu'a.

Da misalin k'arfe goma na safe su Anty Binta sun iso, Khalil ya yi musu iso har d'akin da Zainab take, yaji dad'in yanda suka amsa masa gaisuwarsa, nan suka had'a kayanta driver ya sanya a mota, Zainab sai murna take yi yau taga 'yan uwanta, Khalil ya amsa yarinyar ya yi mata hud'uba da suna *ASMA'UL USNAH*, hakan ba k'aramin dad'i Zainab taji ba, bata yi tsammanin zai sanya sunsn Mahaifiyarta ba, haka ta bangaren su Anty Jidda sunyi farin ciki sosai, a iya yau da suka ga Khalil sunji sun aminta da shi a yadda suka ga yana bama Zainab kulawa cikin so da kauna. Haka ya ciro kud'i dubu saba'in ya bawa Anty Jidda ya ce.

"Dubu talatin na ragon suna su siya a can, a bawa Zainab dubu sha biyar na hidimar da zata yi, dubu Ashirin da biyar kuma a siya kayan abinci na taron suna"

Daga Anty Jidda har Anty Binta sunyi matuk'ar mamaki, nan take suka ji suna son Khalil. Cikin farin ciki da annashuwa suka kama haryar Kaduna, Zainab har kuka Sai da ta yi saboda bata son ta yi nesa da Khalil, haka shima sai da ya fidda kwalla saboda damuwar rabuwa da matarsa. Cikin farin ciki suka isa Kaduna, nan da nan dangi suka cika gida anzo ganin Zainab da 'yarta, yadda suka ganta cikin kyawun kamala sai duk suka mai da gulmarsu. Umma ba k'aramin farin ciki ta yi ba yadda su Anty Jidda suka bata labarin Khalil.

Ba su k'ara cinkewa da lamarin ba sai ranar suna da su Yaya Ismail suka tambaye ta sunan yarinya, sai ta ce musu sunan Umma ce *Asma'u*. Abin ya basu mamaki amma sai suka basar, tunda duk cikinsu ba wanda ya yiwa Umma karan sanya sunanta. Umma ko a ranar dariya da murna take yi kamar gonar auduga. Anyi suna an watse kowa cike da mamakin yaada aka kashe kud'i a wajen sunan, anyi taro kamar dama anyi murna da bikin nata.

*******     *******

*Bayan sati biyu*

Khalil shi da Nuhu suka shirya zuwa Kaduna Dan ganin Husna, cike da fargaba da tunanin yanda za a karb'esu suke har suka isa gidan. Suka yi parking a waje, sun gaisa da mai gadi suka shaida masa kansu, ya shiga ciki ya sanar dasu Umma, nan take Umma ta kira Baffa a waya ta shaida masa zuwan su Khalil d'in, ya yi mata umarnin da Zainab ta fita waje can su gaisa yaga 'yarsa amma karsu kuskura su shiga masa cikin gida. Cikin rashin jin dad'i Umma ta sanar da Zainab abin da Baffanta ya ce, cikin damuwa ta mik'e ta fita can kofar gidan rik'e da Husna a hannunta, suka gaisa cikin nutsuwa kana Zainab ta ba su hakuri bisa rashin shigar dasu cikin gidan, ta shaida musu umarni ne daga Baffa. Basu wani damuba saboda dana sunyi tunanin hakan, farin ciki su ma sun samu ganinta. Nan suka karb'i Husna suka koma cikin mota suka zauna Zainab na tsaye daga gefen mota suna hira sosai, suna cikin haka ne Baffa ya

dawo da sauri su Khalil suka fito suka je wurin motar Baffa sun risina suna gaishe shi ko kallon inda suke bai yi ba balle yasan suna gurin, mai gadi ya bud'e masa k'ofa ya shiga cikin gidan da sauri ya bud'e su da hayak'in mota, jiki ba k'arfi suka tashi suka koma cikin mota Khalil ya ciro kud'i masu dan kauri ya bawa Zainab kana suka yiwa nuna sallama suka wuce. Zainab hawaye taji yana saukar mata a kuncinta ta share tare da girgiza kai ta shiga cikin gida.

Baffa ta samu a cikin falon gidan yana kai kawo, Umma na zaune kan kujera ta zabga tagumi, yadda ta gansu sai jikinta ya yi sanyi. Dago ido Baffa ya yi rai bace cikin masifa ya ce.

"Mai ya kawo wannan 'yan iskan gidana? bana gargad'e ki akan kar naga k'afarsu a gidan nan ba, to bari kiji yadda na tsanesu haka na tsani mutuwa ta, dan haka ai kin isa da kanki, maza ki had'a kayanki ki koma inda kika fito tunda munyi miki gatan da ya kamata muyi miki kuma kin gama wanka karashe ne dama"

Kuka ta fara yi tana ba shi hakuri amma fir yak'i, Umma na zaune ta kasa cewa komai saboda ita ya fara zazzagawa masifar dan ta ba shi hakuri dole yasa ta k'i cewa komai. Tsawa ya daka mata mai k'arfi wanda sai da hanjin cikinta ya kad'a, hatta Husna dake barci sai da ta farko da gigitaccen kuka, jikin ta na rawa ta shiga d'akinta. Waya ta d'auka ta shiga kiran Khalil, bugu d'aya ya d'auka cikin kuka sosai take masa magana, hankalinsa ya yi matuk'ar tashi ya fara tambayar ta ko lafiya? Cikin kukan ta gaya masa abin da take ciki, katse wayar ya yi ya juya cikin Kunar zuciya ya cewa Nuhu daya juya kan motar zuwa gidan su Zainab, cike da damuwa Nuhu ya juya wanda a lokacin sun kusa fita cikin garin Kaduna, Khalil ya gaya masa halin da ake ciki, haka suka koma jugum jugum kamar anyi musu mutuwa.

Ko da suka isa sun sameta a waje ta fito da kayanta duka, Husna tana bayanta, Anty Jidda ce a gefen ta tana bata hakuri da maganganu masu dad'i, sun gaida da Anty Jidda kana suka sanya kayan a mota, Zainab ta shiga gida ta yi sallama da Umma. Umma ta yi mata nasiha da Addu'a da kuma shawarwari a kan yadda zata kula da kanta da 'yarta, da kuka suka rabu sannan ta fito ta shiga mota sai Zaria.

Haka rayuwa ya cigaba da guda na da dad'i ba dad'i har tsawon wani lokaci...

******

Husna na da shekara d'aya wanda a lokacin tana tafiya har Zainab ta yaye ta saboda karatu, Khalil ya samo mata wata tsohuwa tana taya ta kula da Husba yana biyanta, lokacin shi kuma ya kammala karatunsa an turashi service a garin Gombe, ba yadda ya so ba dole ya tafi ya barsu, Zainab ta masha masa zata koma cikin makaranta saboda karatunsu ya yi zafi dan tana matakin Karshe, haka ya barta ta koma tare da duk kayan da take buk'ata ba yadda yaso ba, sai ya rufe gidan nasu.

*****

Kwanci tashi ba wuya a wurin Allah Khalil ya kammala service d'insa wanda a dai-dai wannan lokacin Zainab sun kammala exam na k'arshe har sun gama project da komai, jiran sakamako

suke tare da shirin zuwa service. Khalil ya koma Kano ya gyara gidansa na gado wanda iyayensa suka bar masa da niyyar zai sanya Zainab a ciki su cigaba da rayuwa. Kwatsam sai ga Yaya Aliyu da Anty Binta da kuma Anty Jidda sun zo cikin makarantar da babbar mota na kwashe kaya, dama suna waya da ita sun san ta gama karatun gaba d'aya, Baffa ne ya aiko su dasu tafi da ita. Zainab ta yi farin ciki sosai da ganinsu amma da taji sakon Baffa sai ta fara kuka ita sam ba zata bisu ba, su barta da mijinta tunda ai Baffa da kansa ne ya koreta.
Nan su Anty Jidda suka shiga lallashinta da yake Yaya Aliyu yana jiransu a waje bai san wainar da suke toyawa ba, da kyar suka shawo kanta ta yarda amma da sharad'in sai mijinta ya yarda. Nan suka amince da batunta ko a zuciyarsu sun san Khalil ba zai ki ta tafi gida ba, tana kiransa bugu d'aya ya d'auka ta shaida masa abin da ke faruwa, cikin damuwa ya amince ba yadda zai yi dan yana kyautata zaton da wuya iyayenta basu raba musu auren ba, cikin rashin jin dad'i dukansu suka yi sallama. Nan ta shaida musu ya amince, ba tare da bata lokaci ba suka kwashe mata kayanta duka sannan suka kama hanyan Kaduna.

A gida Baffa yasa an gyara mata d'akinta, ko da suka isa a nan suka dire mata kayanta, taga tarba mai kyau fiye da zuwanta lokacin data haihu, kowa ya sakin mata fuska a nata haba-haba da ita, hatta Husna kowa yana sonta saboda akwaita da surutu da kuma wayau dan lokacin tana da shekara biyu da watanni.

Bayan wata biyu da zuwanta gida ta fara service d'inta a Kaduna wanda da taimakon su Yaya Ismail ne ta samu a nan saboda basu son ta yi nesa da gida. Hakan ya sanya ta farin ciki, sai dai inta tuna da mijinta tana kewarsa cike da burin son ganinsa, sauk'in ta a kullun suna waya, wanda a lokacin ya samu aiki a wani banki a nan cikin Kano yana ta gudanar da aikinsa cikin lumana da kewar matarsa.

******

Bayan shekara d'aya Zainab da Khalil basu sanya juna a ido ba yana son zuwa amma yana shakkar abin da 'yan uwanta za suyi masa, sai dai duk k'arshen wata yana turo mata kud'i ta account tare da aika mata surutu dana Husna.
Husna ta kara wayo da magana sosai wanda a lokacin Zainab ta fara yiwa Khalil maganar a sanya ta a makaranta, sai dai ya ce ta kara hakuri ta bari sai ya zo tukunna sai suyi maganar.

A wata ranar Azabar Khalil ya kira Zainab ya shaida mata gashi nan zuwa, farin cikin a gunta baya misaltuwa a wannan rana, ta shiga kicin ta soma girke-girke na tarbansa mai aikinsu tana taya ta, Anty Jidda harda mata tsiya, dan tun dawowarta ba wanda ya koma damuwa da zancen mijinta hakan ne yasa ta saki jiki take ganin duk sun huce akan fushin da suka d'auka a kansu, dan duk suna d'aukar Husna harma su fita da ita don suyi mata siyayya, suna nuna mata kulawa da soyayya.

Khalil ya kira Nuhu danya rakashi zuwa kaduna amma ya shaida masa baya gari yana Bauchi, da yake can ya koma ya samu aiki a wani company. Khalil bai ji dadi ba haka dai ya tunkari Kaduna shi kad'ai cike da fargaba da damuwa.

Ko da ya isa, Zainab ta fito suka gaisa cike da farin cikin ganin junansu tare da tsantsan kauna mai cike da kewa, tace ya jirata a waje zata dawo, Khalil dai cike yake da fargaba a ganinsa kila ma yau Baffa ya hana ta shiga da shi cikin gidan. Bayan mintuna sai gata rik'e da Husna a hannunta ta mata kwalliya ta sanya mata kaya 'yan kanti riga da dogon wando, ga kitso da aka yi mata wanda yasha bit da yake Husnah akwai suma, da sauri ya amsheta cike da farin ciki wanda har hak'oransa sai da suka bayyana dan murna, ya shiga yi mata wasa amma taki sakin jiki, amma daya bata sweet tuni ta saki jiki yana mata wasa har da kyalkyata dariya.

*Rahma ce*
[10/19, 7:36 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 17 ~ 18_*

Zainab tana kallonsu cike da murna tana taya su dariyar, ta ce su shiga ciki ba musu suka shiga yana biye da ita a baya, wani falo ta kai shi ba komai a ciki sai babban dadduma da aka shinfida da wasu k'ananan kujeru a chan gefe, sai tv da sauran kayan kallo, da alama dai d'akin saukar bak'i ne, abinci ne a jere kala-kala a kan daddumar, suka ya zauna suka shiga hirar yaushe gamo, ta zuba masa abinci a plate ya fara ci tare da santi tana masa dariya, haka ya ci tare da Husna ita ma Zainab tana taya su ci. Inka gansu sai sun baka sha'awa kasantuwar suna cikin farin ciki da annashuwa, ga shi ko wannan su cikin ado.

Bayan sun d'auki dogon lokaci a haka kafin nan suka kammala cin abincin duk sun koshi sosai, suka cigaba da hira na rabin sa'a tare da tsantsar soyayya, dan Husna ta b'ingire ta yi barci, sun motsa sha'awarsu sosai da tsantsar buk'atar juna, jin kwankwasa kofar falon ne yasa suka dawo hayyacinsu, da sauri Zainab ta isa k'ofar ta bud'e, abin da Khalil ya iya ji shi ne.

"Kuzo falo Baffa na magana"

Nan take taji gabanta ya fad'i tare da amsawa da to, ta dawo jikinta a sanyaye, ta shaida masa, shi ma fad'uwa gabansa ya yi amma sai ya boye damuwarsa da cewa su tafi kiran Baffa.

Abin da basu sani ba tun lokacin da Zainab ta shaidawa su Anty Jidda zuwan Khalil, Yaya Aliyu ya kira 'yan uwansa ya shaida musu, duk suka d'auki damarar zuwa gidan a ranar da Khalil zai zo, bayan zuwan Khalil ba dad'ewa da shigarsu falo Yaya Ismail yazo shigo kaduna ba tare da iyalinsa ba, Anty Binta ma tazo duk sun had'u a falo.

Da isarsu Zainab falo suka yi sallama a tare suka shiga, bugun zuciyarsu ne ya k'aru lokacin da

suka ga duk family sun had'u, kallon juna suka yi tare da ajiyar zuciya suka isa cikin felon suka zauna a k'asa daga gefe, Khalil cikin girmamawa kansa a k'asa ya gaishesu, suka amsa kamar ba wani abu a ransu, hakan ya yiwa Khalil da Zainab dad'i har suka k'ara gyara zama, Baffa ne ya yi gyaran murya ya fara magana.

"To abin da ya had'amu a nan shi ne kan batun auren su Zainab, wanda aka d'aura musu shi a makaranta shekara uku kenan daya wuce, to ba wai ina son mu maimaita maganar bane domin kowa a nan yasan da faruwar hakan, ga Zainab a gida ta kammala karatunta sannan ga igiyar aure akan ta, yanzu kai wannan yaro meya makomar auren ku?"

Cikin mutuwar jiki da tsoro mai had'e da damuwa Khalil ya fara magana cikin rawar murya.

"Baffa na zo da niyyar tafiya da su gidana ne da iyaye na suka bar min yana Kano, dan a yanzu na samu aiki a nan shi ne dalilin zuwa na"

Falon ya yi tsit na wani lokaci daga k'arar fanka sai k'aran bugun zuciyarsu, Baffa ya ce.

"Ka zo d'aukar Husna ne ko me kake nufi?"

Khalil cikin mutuwar jiki ya ce.

"Zainab da Husna na zo d'auka"

Baffa ya yi murmushin takaici yana kallonsa.

"To yaro bari kaji, a yau zan nuna maka iyakarka, Zainab dai jini na ce sannan kuma bada miyauna kuka yi auren nan ba, dan haka yau nake so kafin kabar gidan nan ka rubuta mata takardan saki, dan auren da kuka yi na makaranta kuma ya k'are tunda kun gama karatun, yanzu ina so ta yi rayuwa a kan ikona saboda a gidana take"

Cikin tashin hankali Khalil ya dago kai yana kallon Baffa haka ita ma Zainab, kuka ta soma yi mara sauti wanda shi kuma Khalil ya shiga magiya da bada hakuri, nan Baffa ya k'ara shaida musu maganarsa tare da mik'ewa ya bar falon, Yaya Ismail ne da Yaya Aliyu suka d'aura kan inda Baffa ya tsaya, ta inda suke shiga ba tanan suke fita ba, Anty Binta da Jidda kuwa kamar ruwa ya cinyesu suna gudun su yi magana su Aliyu su rufesu da masifa. Umma ma bin bayan Baffa ta yi cike da damuwa tabar falon. Khalil sunkuyar da kai ya yi k'asa hawaye mai zafi yana fita a idonsa, cin mutunci babu wanda su Yaya Ismail ba su yi masa ba, Zainab tun tana kuka mara sauti har sai da ya fito fili, Yaya Ismail yavyi kanta kamar zai bigeta, da gudu ta fad'a d'akinta tana gunjin kuka, takarda da bairo Yaya Aliyu ya mik'a masa da gargad'in in basu rabu a nan ba to kotu zai raba su, cikin kuka mai k'una Khalil ya amsa ya rubuta mata saki d'aya, ya mika masa ya amsa tare da fadan.

"Alhamdulillahi! zaka iya tashi ka kama gabanka sha-sha-sha"

Khalil ya d'ago jajayen idonsa ya ce.

"Nagode amma ba zan iya tafiya ba tare da 'yata ba"

Wani dogon tsaki Yaya Ismail yaja tare da cewa.

"Aikin banza dama ai bamu buk'atar ta ka d'auketa Ku tafi mutumin banza"

Yana gama fadin haka ya wuce d'akin Zainab a fusace, ya sameta kwance bisa gado tana kuka, ko kallonta baiyi ba ya d'auki Husna da take barci ya fito, da sauri Zainab tabi bayansa tana kuka da k'arfi tare da surutun karsu rabata da 'yarta, yana isa kusa da Khalil ya mik'a masa Husna ya amsa tare da kukan bak'in ciki, Anty Binta ne ta koma Zainab da take ta tirje-tirje zuwa amso 'yarta, wani wawan mari Yaya Aliyu ya sauke mata tare da daka mata tsawa, dole yasa ta shiga nutsuwarta tare da gungunin kuka, Anty Jidda saboda bak'in ciki barin falon ta yi tana kuka mai cika da tashin hankali, Anty Binta ita ma kuka take yi mara sauti tare da lallashin Zainab.

Khalil ya ce.

"Nagode sosai da duk kanin abin da kuka yi min, sannan ban zargeku da komai ba face dama nasan akwai rana irin ta yau da zata faru, dan tabbas laifi nane kuma na d'auka amma Ku sani k'addara ce"

Ya kai dubansa ga Zainab ya cigaba da cewa.

"Ki daina kuka in sun raba mu a zahiri a bad'ini bamu rabu ba saboda zuciyarmu tana tare, ko kad'an banji raguwar sonki a raina ba, ki cigaba da hakuri wannan ma wata jarabawa ce, a yanzu da hankali ya shige ni ba zan iya sanya ki ki bujirewa iyayanki ba sai ma k'ara miki k'arfin gwiwa da zanyi kan ki yi musu biyayya, na barki har abada, kar kiyi tunanin zaki sake ganina ko k'afata a cikin gidanku, sai dai ba zan iya cire miki tunanina ba, da zan iya da na goge miki shafin tunani na a kwakwalwarki yadda zaki yi rayuwar jin dad'i nan gaba, kash amma ba zan iya hakan ba dan wannan yin Allah ne ban isa na canza shi ba, ki sanya a ranki kin barni har abada domin dama rabon Husna ce ya had'a aurenmu, kuma Alhamdulillahi mun sameta ta hanyar halal ba ta hanyar zina ba, na tafi Allah ya hada fuskokinmu a aljanna"

Ya fita rungume da Husna ba tare da ya kuma juyowa ba, Anty Binta ta bi bayansa da kayan Husna tana hawaye, ya shiga mota tare da ajiye Husna kujerar kusa da shi, ya kwantar da sit d'in yadda zata ji dad'in barci, dama barci take duk hayaniyar da aka yi bata farka ba, Anty Binta ta sanya masa kayan a sit d'in baya ta yi masa fatan alkhairi ta shiga gida. Shiganta ke da wuya Zainab ta yi kukan kura zata fita da gudu saboda taji tashin motar Khalil ya wuce, Anty Binta ta tare ta, wani ihu ta saki mai k'ara wanda duk gidan sai da suka ji shi, su Yaya Ismail kuwa sun firgita sosai, sank'arewa ta yi jikin Anty Binta alamar ta suma, cike da tashin hankali Anty Binta

ta kwantar da ita a k'asa, ruwa suka yayyafa mata ta farfad'o amma bata cikin hayyacinta. Da sauri suka nufa asibiti da ita. Sai da ta kwana biyu bata dawo hayyacinta ba, a kwana na uku ne ta dawo dai dai cike da k'unci da damuwa hawaye ne ke fita idonta ba tare da sauti kuka ba, su Baffa sunyi nadamar hukuncin da suka yanke mata a kan raba ta da Khalil, satin ta d'aya aka sallameta tare da magunguna.

Tun daga wannan lokacin Zainab na fara rayuwar kunci da zaman *Kad'aici*. Ta fita sabgar kowa sai abin da ya shafe ta take yi, bata magana sai ya kama, haka cin abincinta ya ragu, walwala da dariya ya yi k'aura a rayuwarta, tun su Umma suna lalla shi da mita har sun zuba mata ido tare da yi mata Addu'a.

*****

A b'angaren Khalil kuwa, yana hanya yana kuka har ya isa kano, direct gidan Baba Husain ya zarce, ya iske su basa nan ashe kakarsa ce ta rasu suna gidan mahaifiyar Babanshi, cikin damuwa ya isa gidan ya iske wannan tashin hankali, haka aka yi mata wanka tare da kaita makwancinta.

Bayan anyi sadakar bakwai kowa ya watse, Khalil ya samu Baba Husain, ya ba shi labarin abin da ya faru lokacin daya je Kaduna, Baba Husain bai ji dad'i ba amma sai ya ce.

"Ai sunyi dai-dai tunda dama bada yawunmu kuka yi auren ba, dan haka kaje ka cigaba da rayuwa da 'yar taka sai ka yi k'ok'arin sama mata wata uwar wacce zata rik'e ta"

Daga wannan maganar bai sake cewa komai ba, Khalil ya yi masa godiya da sallama, d'akinsa ya shiga ya hada kayansa gaba d'aya ya fita dasu ya sanya a mota tare da kayan Husna ya ce masu Baba Husain zai koma gidansa, ba musu suka amince dan dama sun ce sun cire hannunsu akansa, ya yi duk abin da ya yi ra'ayi duniya ce baza su takura masa ba.

Haka ya soma rayuwa daga shi sai Husna acikin gidan ya sata a makaranta shi yake kaita ya d'aukota, wannan dalilin ne yasa ya fara samun sab'ani a office dinsu saboda yawan latti da yake yi.

Wata rana ya dawo daga aiki ya shirya Husna suka tafi wajen wasan yara, sun jima agun kana ya d'auketa suka shiga wani shopping complex dan ya yi musu siyayya, suna zagawa yana d'aukar wanda yake so yana sawa a basket, wata mata 'yar matashiya ce ta shigo yin siyayya, ta d'auki kwando ta soma zagawa har gurin dasu Khalil suke, abin mamaki Husna tana ganinta ta kama mata zani, tana sonyin kuka alamar shagob'a dan ta d'auketa, matar ta kalli Husna sai ta fincike zaninta, sai Husna ta fashe da kuka, Khalil da ya yi gaba sai ya jiyo kukanta da sauri ya biyo layin daya bari duk tunaninsa tana biye da shi a baya, ita kuma matar ganin Khalil ya doso su sai taji gabanta ya fad'i zuciyarta na harbawa da sauri- da sauri hakanan taji diran son Khalil lokaci d'aya, kafin ya k'araso ta yi sauri ta d'auketa tana jijjigata, ikon Allah kuwa sai Husna ta lafe a jikinta ta yi shuru tare ajiyar zuciya. Ko da ya k'araso mamaki ne ya cika shi bai ce komai ba, sai sannu da ya cewa matar ya mik'a hannu zai amshe ta amma tak'i zuwa sai ta

k'ara lab'e a jikin matar, abin sai ya kuma ba shi mamaki, ya yi ya yi tazo gunsa sai ta k'i, dole ya hakura yaje ya gama siyayyarsa ya biya kud'in sai ya kai mota kafin ya dawo ciki, dai-dai ita ma matar ta gama nata siyayyar Khalil ya biya mata tare da yi mata godiya da rik'on Husna, Matar ita ma godiya ta yi masa sannan suka fito tare, Khalil ya tambayeta ina zata?, Sai ta gaya masa ya ce ta shiga ya rage mata hanya, haka ta shiga zuciyarta fari kal dan murna, zuna hanya ba mai cewa kowa komai, harya kai ta k'ofar gida lokacin Husna ta yi barci, ta kwantar masa da ita a sit d'in data ta shi ta d'auki siyayyarta ta yi mata godiya, sannan ta buk'aci daya bata number sa, kamar ba zai bata ba amma daga bisani ya bata.

Tun daga wannan lokacin   wannan matar mai suna Habiba wacce akafi sani da Haj. Habee tasa Khalil gaba da kira, tun yana kin d'auka har ya soma saki jiki da ita suka fara sabawa, sai dai baya jin sonta ko kad'an a ransa, sai dai akwai fahimtar juna a tsakaninsu sosai, Habeeba ta nace masa har sai da ya amince zai aureta amma bisa sharad'i d'aya, in zata rik'e masa 'yarsa da amana marainiya, bai gaya mata labarinsa ba kawai dai tasan wanda ya kamata ta sani, cike da zumud'i ta amince.

Habiba d'iya ce ga Alhaji umar wanda ya rasu da dad'ewa, ta yi karatunta digree a bannin kasuwanci, ta yi aure da yaro daya mai suna Nura Allah ya yiwa mijinta rasuwa bisa hatsarin mota da ya yi, ya bar mata dukiya ba laifi wanda daga nan ta shiga rayuwar zaman kanta tana kuma kasuwancin kaya gari-gari, bayan mutuwar mijinta ta samu wasu neman amma taki yin aure saboda tana cin duniyarta da tsiinke har zuwa yanzu da ta hadu da Khalil taji tana sonsa kuma da aure, mutane da dama sunyi mamaki sosai da aurenta da Khalil saboda ya kasance mata shi wasu suna ganin ma zata girme masa, kawai dai tana da jiki mai kyau da kuma k'arin shan magani da mayuwan gyaran jiki.

Biki wata guda aka sanya har ya zo aka d'aura, ta tare a gidansa tare da d'anta Nura, daga nan kuma kulawar Husna ya koma wurin Haj. Habee wacce suke kira da Momy, zuwanta gidan ba dad'ewa tasa Khalil ya kawo mai gad'i da mai taya ta aikin gida Jimmai, da farko ita ke kai Husna makaranta ta d'auko ta, daga bisani mai aikinsu jimmai ta cigaba da kaita tana d'aukota hakan yasa Husna ta saba da mai aikinsu sosai da kuma Baba mai gadi, da farko Momy ta yi mata riko na amana daga bidani kishi da yadda Khalil kewa Husna yasa ta fara jin haushi tare da zugan da aminiyarta Haj. Uwani ke mata, ta fara zallawa Husna ba tare da sanin Khalil ba, sai Nura ne d'an so ko da ya girma bata daina sangarta shi ba.

******

A Kaduna kuwa Zainab ta cigaba da rayuwar k'unshi da *kad'aici*, duk iya kulawa tana samu amma sam tak'i komawa yadda take da, ana cikin haka ne su Baffa suka sanya ranar aurenta da yaya Al'amin. Yaya Al'amin ya yi farin ciki sosai da haka ta bangaren Zainab kuwa fad'e ma bata baki ne, dan bata so sai dai ta d'auki alkawarin zata yi biyayya ko dan ta gyara kuskuren da ta yi a baya. Biki wata d'aya aka sanya, nan da nan lokaci ya yi aka d'aura auren Zainab da Al'amin, an kai ta gidansu Inna Kulu wanda yake Malali, part d'inta daban haka suka ci amarci cikin rashin sakin jiki da juna, Al'amin ya yi iya k'ok'arinsa amma abu ya ci tura sai dai lallab'ata ya cigaba da yi, suna zaman hakuri duka.

*********

Bayan shekara 3 Zainab na d'auke da juna biyu haihuwa yau ko gobe, wata rana tafiya ya kama Al'amin garin Enugu kan aikinsa, ya yi sallama da kowa ya tafi. Tun safe da tafiyarsa Zainab take nak'uda sai yamma ta haihu Yaro Namiji mai kama da ubansa sak, dangi da abokan arziki ana ta zuwa musu barka da yake bata dawo gida ba.

Cikin tsakiyar dare aka yiwa Abba Iro waya ya d'auka, mummunar sako aka isar masa bai k'arasa saurare ba ya saki salati, nan da nan cikin daren Abba ya fara kiran 'yan uwa, cike da tashin hankali kan asubahi gidan ya soma taruwa da dangi makusanta, Zainab na sashinta tare da Anty Binta basu san wainar da ake toyawa ba sunata barci. Bayan sallar Asuba gida ya cika da 'yan uwa da abokan arziki, kuma dai-dai lokacin an shigo da gawar yaya Al'amin wanda duk jini ya lullube fuskarsa nan gida ya hautsine da koke koke, hayaniya ya soma yawa Anty Binta tana daki bisa dadduma ta idar da sallah ta mik'e cikin sauri dan ganin ko a cikin gidan ne ake hayaniyar, koda ta fita ta yi arba da mumunar tashin hankali da kuka ta koma part din Zainab, a hargishe Zainab ta tashi tana tambayar lafiya? kuka ne yaci k'arfinta, Anty Jidda ce ta shigo a guje tana rusar kuka ita ma, Zainab kamar an tsikareta ta mik'e, fita harabar kigan ta yi taga cikowar maza sosai a gidan bata damu da rashin mayafi a jikinta ba ta doshi inda suke, lokacin an gama masa sutura fuskarsa ne bude an fito da shi babban falon gidan mata da maza zagaye da gawarsa sai kuka mara sauti da suke yi tare da yi mata Addu'a, haka Zainab ta kusa cikin falon abin da ta gani ne ya razanata, baya ta yi a sume da sauri wanda suke kusa da ita suka tare ta. Aka yayyafa mata ruwa ta farfad'o, kallon kowa take d'ai d'ai cike da tashin hankali, idonta akan gawar Al'amin ya tsaya, hakan ya tabbata ba mafarki take yi ba ta matsa kusa da shi ta k'urawa fuskarsa ido, Addu'a ta shiga jero masa wanda a lokacin ta bawa kowa mamaki, bayan ta gama iyaye dama sunyi masa Addu'a aka d'auke shi sai makwancinsa.

Zainab ta nima kuka ta rasa sai dai bin mutune da take da ido sai ajiyar zuciya take yi, ashe ma kuka _Rahma ce_ domin kuwa Zainab ta shaida haka a wannan lokaci, ta zama tamka kurma kamar gunki bata iya motsi mai k'arfi, domin a tsorace take bata iya cewa uffan bata san tasha ruwa ba balle abinci, da kyar ake matsa mata ta kurba ruwa wani ma sai an kamata an mata d'ure.

Tana cikin wannan yanayin har tsawon mako d'aya da rasuwar Al'amin kuma ya yi dai-dai da kwanan yaronsu a duniya, a kayi sadakar bakwai tare da rad'in sunan yaro suka sanya masa Muhammad Al'amin, yaci sunan babansa. Al'amin ya tafi ga kuma sabon Al'amin.

*********

*Bayan sadakan arba'in*

Iyayen Zainab suka tafi da ita gida, aka gyara mata d'akinta ta cigaba da zama a nan tare da renon yaronta, sai a yanzu ne take iya kuka, kowa sai ya kwanta amma banda ita domin kwana

take tana sallah da kuka, barci b'arawo ke sace ta. Duk ta lalace ta yi duhu, bata iya cin abinci sosai, duk family suna tausaya mata, sam ba ta yi rayuwar auren jin dad'i ba, na farko sai a hankali wannan ma gashi ya rasu. A wannan lokacin su Baffa da Yaya Ismail da Aliyu suka yi dana sanin rabata da Khalil, a yanzu suna matuk'ar tausayinta kuma suna son suga sunyi mata abin da zai sanya ta farin ciki.

*Rahma ce*
[10/20, 11:10 AM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 19 ~ 20_*

*A Kano*
Husna har ta saba da rayuwar *kad'aici* da k'unci, a makaranta kullun ita ce cikin k'azanta ana kyararta, gata da k'ok'ari amma bata samu mai tallafa mata ba, kullun Khalil yana fama da aiki, kuma a yadda Momy take nuna masa Husna bata kukan maraici.

*****
*Sadiq Aliyu mai kanti*

Ya kammala karatunsa daya fita kasar India b'angaren engineering, ya dawo gida Nigeria cike da zumud'in ginin iyayensa. Ko da ya sauka a gida a part d'in Umma ya dira wato kakarsa, nan da nan gida ya hautsine da murna sai farin cikin dawowarsa su ke yi har zuwa dare, Sadiq yana zaune gefen Umma yake cewa.

"Umma ni banga Anty Zainab bane? Ga shi har Anty Binta tazo, ita kuma taki zuwa kuma nasan uncle Al'amin ba zai hanata zuwa ba"

Umma murmushi ta yi ta ce.

"Kaje d'akinta tana ciki tasan ka dawo ai"

Mamaki ne ya mamaye shi. "Umma dagaske kike yi? wai ko dai tsufa ne ya saki makuwa"

Hawaye yaga ya gangaro mata ta ce. "Allah ya yiwa Al'amin rasuwa wata biyu da suka wuce"

Zmmbur ya mik'e kafin ya kai ga jefa mata wani tambayar ta mik'e ta shige d'akinta. Tashin hankali ne ya ziyarce shi, d'akin Anty Zainab ya nufa ya iske ta kan sallaya zaune tana jan carbi, da sauri ya isa gareta yana mai zubda kwalla, rungumeta ya yi yana fitar da hawaye mai zafi, ita

ma nan ta b'arke da nata kukan sun kai lokaci mai tsawo a haka, Anty Jidda ce ta shigo rik'e da little Al'amin a hannunta yayi barci, tsayawa ta yi tana kallonsu cike da tausayawa ta yi gyaran murya.

"Kai Sadiq tashi ka wuce d'akinka dare ya yi"

Juyawa ya yi da jajayen idonsa. "Ummi dama ashe uncle Al'amin ya rasu shi ne baku gaya min ba?"

K'arasowa ta yi ciki ta kwantar da little Al'amin sannan ta dawo kuwa da Sadiq ta dafa kansa, lallashinsa ta yi da nasiha mai kwantar da zuciya kana ta umarce shi daya wuce d'akinsa, ba musu ya wuce cike da tunanin uncle d'insa da irin shakuwar da suka yi.
Ta koma wurin Zainab ta bata baki sosai har ta lallabata ta kwanta kana ta jawo mata k'ofa ta rufe sannan ta wuce part d'insu.

Tun daga wannan rana Sadiq yake zama d'akin Anty Zee da haka ne ta d'an saki jiki suyi hira, su Umma sunji dad'i sosai da sauyawar Zainab tunda har falo tana fitowa ko da ba hira take yi ba sai dai ta zauna shuru, in kuwa ta yi magana tofa da Sadiq ne, Da wowarsa ya sauya gidan gaba daya. Sadiq bai san cewa Zainab ta auri Khalil ba balle harda yarinya tsakaninsu, a saninsa dai cewa Al'amin ne farkon Mijinta kasantuwar body's school ya yi a secondary sannan daga dawowarsa Abbansa ya turashi k'asar India can ya yi digree d'insa.

***
Bayan dawowarsa da wata hud'u ya fara service garin Kano a ma'aikatar matatan man fetur. Ya had'a kayansa gaba d'aya ya wuce Kano ya sauka gidan Yaya Ismail, ya samu tarba mai kyau da kulawa wajen Anty Ameena, ya fara zuwa aiki sai yamma yake dawowa. Kasantuwar shi mutum ne daya saba rayuwan *kad'aici* tun tasowarsa, sam bai jin dad'in zama a gidan, tuni ya sanya a fara masa cigiyar gida a wani area, aiko aka yi sa'a  ya samu gida plat shi kad'ai mai kyau, ya kira mahaifinsa ya sanar da shi amma fir yak'i saboda bavzai raba musu zumunci ba, sai dai dole ya cigaba da zama a gidan Yaya Ismail d'in tunda yana gamawa gida zai dawo, bai so haka ba ya kira mahaifiyarsa Anty Jidda ya sanar mata ita ma bata so haka ba amma da ya dinga mata magayi ta amince zata shawo kan Abban nasa.

Shuru shuru sunyi banza da shi akan maganar, aiko ya bugo sammako sai Kaduna part din Umma ya dira ya kai kukansa wurinta kasantuwar Umma mai son jikokinta ne aiko ta amince, nan da nan ta kira Aliyu ta shaida masa a yiwa Sadiq abin da yake so, dole ba musu ya yarda ya tura masa kud'i masu yawa ta account dinsa. Kafin ya tafi sai da ya kwana d'aya ya gana da Anty Zainab da little Al'amin.

Washe gari da sassafe ya wuce Kano cike da farin ciki, ko da ya isa gidan daya kama haya ya fara zuwa ya sanya aka yi masa fenti da gyare gyare sai yamma lis ya isa gidan Yaya Ismail a gajiye, Anty Ameena ta tarbeshi da abinci kala-kala, ya sanar mata da zai koma wani gida, ta nuna masa ai Umma ta kirasu ta sanar musu, Ta cigaba da cewa.

"Haba Sadiq kamar munyi maka laifi, meyasa ka zab'i ka zauna kai kad'ai, ga 'yan uwanka Khadija da Kamal, kuma kasan Khadija ba zata ji dad'i ba yadda kuka saba"

_Da yake ta kara haihuwa yaro namiji aka sanya masa Kamal shekarunsa biyu kenan._

"Anty karki damu insha Allah zan rik'a zuwa akai-akai, ni baku min komai ba, tun farkon tashina da rayuwar *kad'aici* na taso tun daga jss har zuwa digree d'ina, dan haka ba komai Allah"

Nan dai suka cigaba da tattaunawa.

Bayan kwana biyu ya tattara inasa inasa ya koma sharad'a da zama, ba yanda su Yaya Ismail suka yi sai hakuri.

Koma wansa sharad'a yaji dad'in area saboda unguwar ba hayaniya ba cikowar mutane, kwanan sa biyu da komawa ya yi arba da lamarin Husna, wata rana yana zaune a harabar gidan yana shan iskar hantsi, yana danna wayarsa da alama chart yake yi, ihun kuka ya soma ji gabansa ne ya fad'i, ya toshe kunnuwansa saboda kukan ya yi yawa ya tashi ya leka waje ko a can kukan yake zuwa gunsa, ko da ya leka ba kowa, ya dawo ya zauna naya sauraren kukan da haka ne har ya shaida mak'otansa ne kukan yake zuwa gunsa, ya yi tsaki.

"Wannan wani irin kuka ne sai kace ana yanka shi"

Duk sai yaji zaman gurin ya gundureshi, tashi ya yi ya wuce cikin d'akinsa cike da k'unan rai.

A b'angaren Momy kuwa, Husna ta kwana da zazzab'i wanda hakan ya haifar mata yin fitsarin kwance, da yake Dady baya nan ya yi wani tafiya shiyasa ta samu damar dukanta, lokacin data tsandara ihu ashe ruwan sanyi ta kwara mata a jiki, sannan tabi ta da duka da wayar wuta, sai da ta gaji dan kanta kana ta rabu da ita, jikinta na rawa da bakinta abin tausayi, kukan ma sai hawaye take yi da fidda nishi mai k'arfi, d'aki ta korata ta shiga sannan ta sanya mai aikinta ta wanke kayan fitsarin. Baba mai gadi sai da ya yi kwalla da Allah wadaran Momy, haka ma ta bangaren Jimmai mai aiki.

******

Tun daga wannan lokacin Sadiq ya fara jin kukan Husna ba sauyi, kullun kukanta kalansa daban ba safiya ba rana ba dare, ya kasa tantance mace ce ko namiji, shi dai ya shaida muryan yaro ne yake ji ba babba ba. Tun abin baya damunsa ya dauke shi ba komai bane yana ta'allak'a abin da k'ila yaron baya jin magana ne, daga bisani ya fara damuwa da yawan dukan.

Wata rana ya fito da shirin zuwa wajen aiki ya fito da motarsa ya yi parking, ya rufe gate kana ya koma mota, ya fara tafiya, dai dai lokacin da zai gota gate din su Husna, yaga ta fito a guje kamar an biyota sanye da uniform ajikinta na makaranta, sai ya tafiya a hankali yana bin bayan

ta, mamaki ne ya cika shi sai ya fara tunanin ko dai dama ita ce ake yawan duka? sai ya kauda tunaninsa da cewa.

'Haba dai k'ila yaran gidan suna da yawa'

Da haka ya shashantar da lamarin ya kama gabansa.

*******

*A Kaduna*

Anty Zainab ta d'an saki jiki yanzu tana harkokinta sai dai ba kamar da ba, little Al'amin ya yi bul bul abinsa yanata k'ara wayo kamanninsa da babansa yana kara bayyana, yaron ya yi farin jiki sosai kowa na sonsa wataran ma baya yini a gunta sai wurin Anty Jidda da Umma yake yini, hakan na yiwa Zainab dad'i saboda tana samun damar yin ibada sosai.
Ta wajen su Baffa mai kanti kuwa kasuwancinsu yana ta hab'aka kasantuwar yawan kyauta ga talaka da suke.

Anty Binta har yanzu Allah bai bata haihuwa ba, magani ba wanda basa nima amma har yanzu shuru, Alhamdillah ta yi dacen sirikai duk da hakan suna nuna mata so ba wanda ya canza mata akan rashin haihuwar. Zahra kanwar Sadiq tana wajenta tare da samun gata sosai da kulawa fiye ma da wajen mahaifiyarta Anty Jidda.

Abba Iro da Inna Kulu suna rayuwar rashin jin dad'i da kewar mutuwar d'ansu tilo d'aya Al'amin, kullun cikin yi masa Addu'a suke yi, hakan ne yasa Inna Kulu ta karb'o d'iyar k'anwarta daga k'auye mai suna Kausar wacce bata wuce sa'ar Khadija ba d'iyar Yaya Ismail, sun sanyata a makaranta tana zuwa, hankalinsu ya d'an kwanta saboda suna ganinta a gabansu.

******

*A Kano*

Sadiq yawan kukan Husna ya fara sanya shi cikin damuwa. Wata rana ya yi wanki yana shanya ta bayan gidan yaji ana ta kwalawa Husna kira, tunani ya shiga yi.

'Ko dai wannan yarinyar dana gani ita ce Husna?'

Murmushi ya sub'uce masa tare da tambayar kansa.

'Wai meyasa na damu da rayuwar mutanan gidan nan ne?'

Bai k'arasa tunaninsa ba yaji an fara dukanta tare da manya manyan zagi, haushi ne ya cikashi ya rasa meye dalilin dayasa wannan matar ke dukan yaranta kamar jakai, haka ya gama

shanyan a  gaugauce yabar gurin, yana shiga d'akinsa ya zauna, kukan Husna ya fara masa yawo a kwakwalwa, haka ya yini cikin damuwa. A ranar ne ya gasgata kukanta ne kullun yake ji, naya cewa.

"Ashe dama mace ce ba namiji ba? to meyesa kullun ake dukanta?"

Bai da amsa haka ya tashi ya shirya ya bar unguwa cike da takaici yana dana sanin zamansa unguwar, wanda har zuciyarsa ya fara tunanin barin area ya koma wani gurin. Wani b'angare na zuciyarsa ya hane shi, haka dai ya cigaba da zama tunda saura masa watanni yabar garin gaba d'aya.

****

Rayuwa ya cigaba da tafiya wanda a yanzu shekarun Husna 7 cikin na 8, a yanzu Sadiq tausayin Husna ya gama maye zuciyarsa kullun tunaninsa ya zai yi ya taimake ta, wanda daga bisani ya gane Momy ba ita ce ta haifeta ba, kuma mahaifinta bai san da wannan tuggun da Momy ke mata ba. Kullun da tunaninta yake kwana yake wayar gari.

Ya kammala service d'insa amma sam baya burrin yabar Husna cikin wannan rayuwa yana son ya taimaki rayuwar ta, ana cikin haka ne ma'aikatar suka rik'e shi dan sun ji dad'in aiki dashi, farin ciki ne ya kamashi ya kira gida ya sanar musu, suma murna suka yi masa tare da fatan alkhairi. Da hakane ya cigaba da zama a Kano, wanda har ya fara magana da Husnah ranar data fita siyo chewing gum, yana son ya jawota a jikinsa dan su saba...

_Wannan shi ne silar shigar Husna cikin rayuwar kad'aici, wanda yake haifar mata da matsaloli sosai nan gama_

*******    *******

** *CIGABAN LABARI* **

_Bayan sati d'aya_

Kamar yadda Dr. Ismail ya buk'aci Momy ta dawo da Husna, haka ta shirya ta kaita. Zaune taje a gaban Likita, Dr. Ismail yaji dad'in yadda yaga Husna ta sauya kamar ba ita ba, da alama tana samun abinci sosai, maganin daya bata ran nan ya d'auko ya bawa Husna ta sha, ikon Allah yau bata yi garda man sha ba, sannan ya k'ara yiwa Momy bayani kamar na baya kana ya sallamesu da bayanin ba sai sun k'ara zuwa ba, yadda aka bata magananin ya wadatar ba sai ta kuma sha ba, cike da farin ciki Momy ta isa gida.

********

Husna ce zaune wajen Baba mai gadi yana koya mata karatun Al-Qur'ani, ya ji ana knocking k'ofa ya mike da sauri yaje ya bud'e k'ofar, Sadiq ya gaishe shi kana yad'an sosa k'eya ya ce.

"Dama na zo duba Husna ce"

Da sauri Baba ya k'arasa fitowa wajen gaba d'aya ya rufe k'ofar

"Taro lafiya kake nimanta? hala kai dan uwanta ne dan naga kuna yanayi"

"A'a ni mak'ocinku ne, ran nan naganta taje siyan abu can shagon sama shi ne muka yi magana da ita, a tak'aice dai naga kwana biyu ban ganta ba shi ne na zo tambaya"

Sadiq ya yi maganar yana murmushi. Baba shima ya yi murmyshi.

"Ikon Allah ashe kaine mai gidan nan"

Yayi amfani da hannunsa yana nuna gidan, Sadiq ya gyada masa kai alamar eh, Baba ya lek'a ya kira Husna.

"Ai gata nan ma muna karatu da ita ne"

"Allah sarki"

Husna ta fito, tana ganin Sadiq ta washe baki, fararan hak'oranta da take famfara sune suka bayyana, gefen kumatunta suka lotsa, shima murmushin ya yi mata tare da cewa.

"My Husna"

Ya kama mata hannu suka gaisa ya ciga da cewa.

"Ban ganki ba kwana biyu shi ne na zo dubaki"

Husna ta yi dariya ta ce.

"Uncle zaka rika kaini makaranta ko ka siya min biskit, kaga Momyna bata bani sai ta rik'a dukana, Abbana kuma kullun sai dare yake dawowa bana ganinsa har inyi barci, Momy tana ta cin zalina ai Allah sai ya sakamin ko Uncle"

Sadiq ya b'ata rai ya ce.

"Momin naki kike cewa haka, to mun b'ata ma"

Nan da nan ta yi rau rau da ido tana son yin kuka.

"Allah unclear duka na take yi, kar kayi fushi dani kaji"

Ta k'arasa maganar tana matsar kwalla, Baba mai gadi yana gefe ya d'auko bancinsa ya aje a bakin gate d'in ta waje ya zauba, ya ce.

"Yaro rabu da ita kasan shirmen yaro"

Sadiq ya yi ajiyar zuciya yayi ya zauna gefen Baba yana cewa.

"Kasan kuma da wuya yaro ya rik'a fad'ar magana haka kawai ba tare da kamshin gaskiya aciki ba"

"hakane kuma, dan tabbas gaskiya ta gaya maka"

Sadiq ya gyara zama dan ya samu abin da yake so.

"Baba kana nufin dagaske ne abin da take tafad'a?"

"Kwarai kuwa da gaske ne, zan iya ce maka shekaru uku cikin na hudu dana fara aiki a gidan nan, wallahi d'ai-d'ai kun rana ne Hajiya bata dukanta, wataran ma fiye da sau biyu take dukanta a rana, amma kuma zan iya ce maka Alhaji har yau bai iya gane haka ba saboda makircinta"

Sadiq sai ya k'ara gyara zama yana saurarensa, Baba ya cigaba da cewa.

"A yanzu haka cutar hauka ta d'aurwa Husna wai an kai ta asibiti ance tana da Matsala a kwakwalwa, ta hada da makircinta ta sanarwa Alhaji yanzu a haka suke d'aukar ta"

Sadiq ya yi salati tare da shiga matsanan cin damuwa, nan dai Baba ya cigaba da ba shi labarin abin da ya sani game da ita ya sanar da shi cewar tabbas ba Momy ta haifeta ba. Ya shiga damuwa sosai wanda har sai da yaji kansa na sarawa, sun d'auki tsawon lokaci suna tattaunawa wanda daga bisani Sadiq ya k'irga dubu goma ya bawa Baba da cewa duk abin da Husna take so game da abinci in ba a bata ba, da kud'in break na makaranta dama sabulun wanki ya rik'a siya yana mata, zai rik'a biyansa duk karshen wata. Sannan ya ciro dubu uku ya ba shi yasa a aljuhunsa, Baba nan ya shiga godiya da sanya masa albarka, hakika ya yaba da hankalin Sadiq, kuma lokaci daya yaji zuciyarsa ta aminta da shi, yana ji a ransa kila wani d'auki ne Allah ya kawowa Husna a saukak'e. Ya jima gun har sai da Sallan Magrib ya gabato sannan ya mik'e ya yiwa Baba sallama, ya kama wa Husna hannu ya ce.

"my Husnee zan tafi, gobe in Allah ya kaimu ki fito da wuri zan sauke ki a makaranta"

Ta gyada masa kai ta ce.

"Zaka siya min kosai da koko, kaga Baba ya dauna bani, kullun haka nake tafiya banci komai,

sai k'awata Khadija ke tsammini abincinta in tazo da shi"

Ta k'arasa maganar da shagwaba kamar za ta yi kuka, bai bata amsa ba ya kalli Baba ya ce.

"Dan Allah ka tabbatar kafin ta tifo ka tanadar mata abin da zata karya da shi in kud'in ya kusa k'arewa kamin magana"

"To yaron Albarka zan sanar maka insha Allah, sai dai ka rik'e amanar yarinyar nan, kasan duniya sai sannu, ba a shaidar mutum, kuma kaga duk abin da ya faru da yarinyar nan ni za'a fara tuhuma"

Sadiq yayi murmushin gefen baki ya ce.

"Jar ka damu Baba insha Allah zaka sameni da rik'on Amana"

Suka k'ara yin sallama kana ya wuce yana dagawa Husna hannu.

*******

Dady daya dawo daga office ya tambayi Momy yadda suka k'arayi da likita kan maganar Husnah, nan ta shiga jero masa bayanin k'arya, damuwa ne ya k'ara shigarsa ya mik'e ba tare da ya k'ara cewa komai ba ya wuce d'akin Husna, ya sameta tana ta sharb'an barci tare da ajiyar zuciya, kwallane ya taru a idonsa ya sauka kan kuncinsa, gefen katifar ya zauna ya rafka tagumi, kallonta yake yi ba tare da yakifta ido ba, tunani mai zurfi ya shiga yi akan aurensa da Zainab wanda dana sani ya gama maye gurbin zuciyarsa, yana tausayawa 'yarsa da halin da take ciki, da basu kauce wa umarnin iyayensu ba da duk haka bai faru ba, tun daga ranar da ya rabu da Zainab jin dad'i da farinciki ya yi k'aura a cikin rayuwarsa, sai k'unci da damuwa mai had'e da rayuwar *Kad'aici* yake ciki, wanda ya gasgata itama Zainab rayuwar da take ciki kenan, domin soyayyar gaskiya sukewa juna. A wannan yanayin kukan badama yake yi sosai, daga k'arshe ya yi Addu'a ya tofa mata tare da fatan Allah yasa suci jarabawar da ya yi musu.

Bayan ya koma sashinsa ya sanarwa Momy zai yi tafiya na tsawon wata shida, an turashi K'asar Manaco dan yin wani kwas a can, ya cibaga da yi mata bayani tare da magiyar taciga ba da rikon amanar Husna har Allah ya dawo da shi lafiya, ta yi murna da tafiyar dan ita ma tana farin cikin freedom din da zata samu akan business d'inta, ta yi masa addu'a da fatan nasara, da kuma alk'awarin rik'on amanar Husna.

*Rahma ce*
[10/21, 7:09 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 21 ~ 22_*

Tunda Dady ya tafi Momy take fita tun safe sai yamma take dawowa, kud'i take bawa Nura ya nima abin da zai ci ko kuma ta sanya Jimmai ta dafa masa indomi amma banda Husna da sai abincin dare kawai take bata.

Husna tana samun kulawa dai dai gwargwado wajen Baba mai gadi yana k'ok'arin cika Alkawarin daya d'aukarwa Sadiq, shi ne kullun yake shiya mata abinci da kuma kud'in break na makaranta, in wankinta sun taru ya siwo omo da sabulu ya baiwa Jimmai ta wanke mata kayan ko ya d'auki kud'i ya bata sai ta ki karb'a domin ai Hajiya tana biyanta. Gaba d'aya Husna ta sauya ko a makaranta Anty Meenah ta yi mamakin sauyawarta, kullun cikin tsafta sannan ta yi kyau ramar da ta yi ya ragu. Hakan yasa ta mai da hankali sosai a karatunta wanda a yanzu kwakwalwarta ya samu raguwar damuwa da tunani. Hatta yaran class d'insu da suke kyamarta sun daina har suna magana yanzu. Abotarsu da Khadija ya kara k'ulluwa sosai kullun suna tare komai nasu d'aya suke yi, wanda har wasu suke musu kallon ko 'yan biyu ne saboda suna yanayi da juna haske kawai Husna tafi Khadija. Sadiq yana duba Husna duk bayan lokaci kamar weekend, hakan yasa suka k'ara shauk'uwa sosai.

********

Bayan wata biyu da tafiyar Dady, ya kama ranar asabar Momy tana gida bata fita ba a ranar, k'awarta Haj. Uwani ta zo suna zaune suna hira, sai ga Husna daga waje ta shigo falon da gudu tana dariya, bata san Momy tana gidan ba, tsawar da Momy ta daka mata ya dawo da hayyacinta jikin ta, sun kunyar da kanta ta yi k'asa nan da nan ta shiga tai ta yin ta, Momy binta da kallo ta yi cike da mamakin yadda ta sauya ta kara girma da kuzari, tambayar kanta ta shiga yi.

'Yaushe na yi saken da yarinyar nan ta tamu freedom haka? 'Anya Doctor ya bani maganin daya dace kuwa?'

Wani b'agare na zuciyarta ta ce.

'Kwarai ya baki ke ce dai ki kai sake, tunda wata biyu kenan baki zama a gida'

Nan da nan fuskarta ya sauya kamar anyi mata mutuwa, take ta gasgata abin da zuciyarta ta raya mata. Mik'ewa ta yi ta zaro wayar wuta, Husna tana gani ta fara ja da baya har sai da ta iske jikin bango tare ta runtse idonta, duka ne ta fara yi mata ta ko ina sai da ta yi mata lilis tana ihu, kafin nan Haj. Uwani ta kwaceta tana cewa.

"Haba Hajiya ai sai ki sanya mak'ota su zage ki, ai a kwai ta inda zaki rik'a hukunta ta ba sai duka ba, kawai ki rik'a rufebta ad'aki kina tura mata abinci yadda haukar zai kamata da kyau, amma wannan ai wahalan da kai ne, k'ila ma garin dukanta ki zubawa kanki"

Wani nannauyar ajiyar zuciya Momy ta yi.

"Wallahi Hajiya banda ina tsoron yadda zan kwashe da Alhaji da sai na kasheta na huta, na tsaneta bana kaunarta"

"To ai kisan mummuk'e kike yi yanzu, tunda kin je gun likita ya miki abin da kike so ai ke ce kuma abu ke hannunki, shawarar dai dana baki farko ita zaki mata ki huta kawai"

"Gaskiya ne kin bani shawara mai kyau, bari ma ki gani tun yanzu zan fara"

Ta kama k'afar Husna tana janta kamar akuya, tun tana kuka a fili har ta koma sai hawaye ke fita da ajiyar zuciya, a haka ta isa da ita d'aki tare ta yi mata barazanar kisa in har ta kuma ganin k'afarta a waje, ido a bud'e cike da tsoro Husna ta amince da dokar ta, nan ta barta tana ta susar jiki tare da matsanancin kuka, haka Momy ta fito falo suka cigaba da hira. Jimmai mai aiki tana kicin, banda kuka babu abin da take yi, tana tausayin Husna, da tana da yadda zata yi da ta raba Husna da wannan muguwar rayuwar, tana aiki tana zancen zuci.

Sadiq ne ya fito da sauri daga gidansa mako guda kenan rabonsa da Husna, sai dai suna gaisawa da Baba time to time yana tambayarsa lafiyarta, yanzu ma kukunta da yaji ne ya kasa sukuni ya fito, ya samu Baba a bakin gate zaune, a gau-gauce suka gaisa ya samu guri ya zauna.

"Wai Baba kamar kukan Husna nake ji tun d'azu?"

Baba ya yi murmushin takaici.

"Eh yau kuma dukan ya juyo, kwanakin nan da yake bata wuni a gida ba zancen duka"

"Wai dan Allah Baba Alhaji baya nan ne? Ai wannan huk'uba ta yi yawa"

"Uhum wannan matar gogaggiyar 'yar duniya ce ni ina ganin ma zata girme Alhajin, kawai dai hukuncin Allah ne mai had'i amma ai tafi k'arfinsa, kuma dan makirci har yau bai san ana yiwa 'yarsa wannan huk'ubar ba, kuma baya nan ya yi tafiya"

Tsaki Sadiq yaja mai cike da tsananin jin haushi.

"Allah ya saka mata"

"Amin"

Bai kuma wata magana ya mik'e cike da damuwa, su ka yi sallama ya koma gida idonsa ya

dawo kwalla, bai sani ba sai dai saukar hawaye ne yaji a kwance kan kuncinsa, yasa hannu ya goge tare da cewa.

"Allah ka kawo wa wannan baiwa taka d'auki"

******

Tun daga wannan ranar Momy ta sauya salo, Husna ko falo Momy bata bari ta fito, in har ta fito to makarantar boko zata, shima sai ta rakata har gate taga ta yi nisa da gida kan take komawa cikin gida ta yi shirin fita, sannan tana k'ok'arin ta dawo da wuri kan a tashe su a makaranta dan ta cigaba da b'oyeta a d'aki, ta yiwa Baba warning sosai akan Husna, har da barazanar zata kore shi in har ya cigaba da shiga huruminta.

Sadiq yana zuwa kullun ya tambaya Baba labarin Husna zancen dai d'aya yake gaya masa, shi ne tana lafiya yanzu ba a barinta tana fitowa waje, hakan ya k'ara sanya shi a damuwa domin yau kusan wata d'aya kenan bai sanyata a idonsa ba, kullun dai Addu'a yake mata. Ya cigaba da zuwa aikinsa kamar yadda ya saba sai dai damuwar yana linke a zuciyarsa. Yana k'ok'arin zuwa gidan Yaya Ismail wanda in ya ga Khadija sai ta rik'a d'auke masa kewar Husna.

******* *******

*Bayan wata biyu*

Ya yi dai-dai da watan Dady Biyar kenan a k'asar Manaco, Sadiq ya samu hutu a wajen aiki na wata d'aya, haka ya shirya ya bama Baba kud'i dubu Ashirin, dubu sha biyar na Husna, dubu biyar ya rik'e, nan ya yi masa godiya ya shiga mota sai Kaduna.

******

*Kaduna*

Yana shiga gida ya wuce d'akin Anty Zainab ya sameta tana karatun wani littafin addini, zama ya yi a k'asa ya sanya kansa a kan cinyarta sai ya fashe da kuka, mamaki da damuwa ne suka cikata.

"Sadiq Llafiya? ko anyi maka wani abu ne?"

Ya dago idonsa da sukyayi ja ya ce.

"Anty na ina farin cikin ganin ki ne sannan kuma ganin ki ya debe min damuwa ta"

"My son damuwar me kake yi?"

Murmushi ya yi tare da mik'ewa tsaye.

"Ni dai tunda na sameku lafiya Alhamdulillah, sannan ba wata damuwa bace nan gaba zan sanar miki"

"Yau dai ina ga da rikici ka dawo, halama ko gaisawa dasu Umma baka yi ba?"

"Wallahi kuwa kamar kin sani ina shigowa naga ba kowa a falon shiyasa na taho nan d'in"

"To maza ka je ku gaisa da su Umma, ni bari na shiga kicin da d'aura maka abin da zaka ci, dan yau tuwo Umma tasa aka yi a gidan, Amminka ma ina ga bata girka komai ba nan ta zo ta ci namu"

"To shi kenan  bari naje na dawo"

Har ya kai bakin k'ofa sai ya juyo da sauri ya ce.

"Anty ina little yake?"

"Yana gun Umma"

Bai k'ara cewa komai ba ya kama gabansa.

*****

Tun ranar da yadawo bai iya fita ko ina yana zaune a gida kullun yana tare da Anty Zainab da little Al'amin, ko kuma ya kunshe a d'aki yana tunanin Husna.

Ranar juma'a, Baffa  ya tara su a falonsa da daddare nan suka gaisa sannan ya d'aura da cewa

"Zainab a kan ki muka yi wannan taron naga zamanki ya yi yawa a gida, shi ne na yanke shawarar bud'e miki pharmacy a nan bakin babban hanya, na sanya an gama miki komai hatta magani anyi oder su an zuba, yanzu bud'ewa ya rage tare da sanya sunan wurin, dan haka yanzu wani suna ya kamata a sanyawa wurin?"

Farin cikinta ne ya bayyana k'arara a fuskarta, cike da murna wanda kowa a gurin ya yi farin ciki, cikin ladabi ta ce.

"Uhum Baffa ina ga a sanyawa wurin sunan Asma'u pharmacy tunda kaga sunan Umma ce"

Murmushi Baffa ya yi wanda ya san ba dalilin sunan Ummanta bane sai dalilin sunan 'yarta ce, Anty Jidda ne ta ce.

"Zainab mai zai hana a sanya Husna Pharmacy ai kamar zaifi"

Kunya ce ta rufe Zainab sai ta sunkuyar da kai k'asa tana wasa da yatsunta, saboda ta fahimci duk sun gano nufinta sai ta ce.

"Uhum Anty Jidda ni dai ba haka nake nufi ba, ko meye ma dai a sanya burina kawai in ga na fara aiki"

Nan duk suka kwashe mata da dariya Baffa ya ce.

"Ai magana ta k'are tunda Antynki ta zab'ar miki"

Umma ma ta goyi bayan haka ko wanne dai ya fad'i albarkacin bakinsa, nan Yaya Aliyu ya kira Yaya Ismail da Anty Binta ya sanar musu tunda su ba ayi taron dasu ba, nan dai taro ya tashi cikin farin ciki kowa yana murna yadda Zainab ta saki jikinta aka yi hira da ita.

******

Bayan mako d'aya, an kammala had'a pharmacy d'in, komai na buk'ata an sanya mata wanda hatta ma'aikatan da zasu yi aiki a gun an samar mata, mutum biyu safe sai cashier d'aya, yamma da dare ma haka, sai ita da za ta yi consulting da safe sai wani Dr Idris daga yamma har dare. Abu dai an tsara shi abin sha'awa, a ranar juma'an aka bud'e wurin tare da yin wata had'add'iyar walima sun gayya to dangi na kusa da abokan arziki an ci an sha duk a cikin gidan, sannan aka d'aura da Addu'a da fatan alkhairi ga Husna Pharmacy. Yaya Ismail da Yaya Aliyu suka hada kudi suka siya mata sabuwar mota. Farin ciki a gun Zainab baya misaltuwa, a wannan ranar kowa ya shaida Zainab na cikin farin cikin, Sadiq shi ne dan jelarta duk in da take yana biye da ita shima cike yake da farin ciki, sai dai inya tuna da Husna sai yaji ba dad'i a ransa, amma ko ba komai sun faran ta masa rai da aka sanya sunan Husna pharmacy, yana burin inya koma Kano ya bata labarin an sanyawa Antynsa sunanta a pharmacy.

An bud'e wuri ya yi kyau, sun gayyato Liverty TV da DITV a wajen domin su yi tallar pharmacy d'in, an washe taro lafiya in da kowa ya tafi cikin Farin ciki.

Ranar monday Zainab ta fara aiki a pharmacy d'in ta, wurin ya yi matuk'ar burgeta harda k'aramin office d'inta na ganawa da marasa lafiya, bayan misalin k'arfe uku na rana Sadiq ya zo d'aukar ta a mota suka wuce gida.

Tun daga wannan ranar Zainab take cikin rarin ciki amma duk da haka tana da damuwa a ranta sai dai ta barwa rabbil izzati, ciniki sai k'aruwa yake tare da samun customers sosai.

******

Ana gobe Sadiq zai koma Kano damuwansa ne ya k'aru, burinsa bai wuce yaje yaga halin da Husna take ciki ba, da daddare yana zaune a d'akin Ammin sa ya ce.

"Ammi haka nan sai naji gabana yana fad'uwa hankalina yana tashi"

"Subhanallahi! meyasa kake jin haka?"

"Ammi wani amana na d'aukarwa kaina wanda yanzu kimanin wata uku kenan ban sanya amanar a idona ba, shiyasa duk naji hankalina a tashe"

Ajiyar zuciya ta yi tare da yin murmushi, tasan duk yadda za ta yi ta matsa masa ya gaya mata ba zai fad'a ba saboda tasan shi mutum ne mai mugun zufin ciki, shawarwari ta shiga ba shi tare da nasiha mai ratsa zuciya da kuma sanin darajar girman Amana, hawaye ne ya soma yi gaba d'aya hankalinsa ya tashi burinsa bai wuce ya ganshi a cikin garin Kano ba, da lallashi Ammi ta lallab'ashi ya wuce d'akinsa cike da damuwa.

Da safe ya shirya tare da yin sallama da mutanan gidan ya kama hanyar Kano, yana isa, kaya kawai ya a jiye ya wuce office, sai yamma lis ya dawo, ya shiga gida ya watsa ruwa kana ya fito ya samu Baba yana alwalar Sallar Magrib, suka gaisa  kana Sadiq ya tambaye shi labarin Husna, murmushi ya yi wanda yafi kuka ciwo.

"Ai sunyi hutun makaranta kusan yau sati uku kenan ban sanyata a ido na ba"

Wuri Sadiq ya samu ya zauna saboda yaji k'afafunsa ba zasu iya d'aukarsa ba yana jinjina maganar Baba.

"To  lafiya bata fito wa?"

"Uhum ina ga lafiyar kenan tunda har yau Alhaji bai dawo ba, kuma tun ran nan data duketa ban kuma jin kukanta ba ina ga abin ya yi sauki ne"

"To wai Baba bata zuwa islamiya ne?"

"Gaskiya da tana zuwa sai Hajiya ta ce yawo take zuwa aiko dole aka cireta, an d'auko mai yi mata karatu a gida, nan ma hajiya tasa Alhaji ya kore shi saboda mugun kissarta"

"Ya salam yanzu haka take zama bata san addini ba, ai tun yanzu ya kamata ace ta fara sanin addini"

"Uhum to yaro bokon ma ai da da hali hanawa zata yi, nan take zuwa nake koya mata dan abin da na sani"

"Allah sarki, Allah ya saka maka da alkhairi"

"Sadiq dani da kai duka Ameen ya rabbi"

Nan suka wuce masallaci dan gabatar da sallah magrib.

*****

Dady ya dawo daga k'asar Manaco, ko da ya dawo Husna ya fara tambaya Momy ta ce

"Tana d'aki kwance ba lafiya mun je asibity an had'a mata magani, kuma ni abin na Husna gaba yake k'arawa, yanzu ko falo bata fitowa kullun tana d'aki, makaranta ma da kyar nake turata tatafi"

Ta k'arasa maganar kamar zata fashe da kuke, zufane ke karyowa Dady duk sanyin AC dake ratsa d'akin, gaba d'aya damuwa ce ya rufe shi, mik'ewa ya yi ba tare da ya ce uffan ba ya isa d'akin, kwance take ta rufa da wani bargo wanda ya yi datti sosai, sunanta ya kira a hankali, da sauri ta yaye bargon ta tashi zaune, sosai ta rame ga wasu kuraje da suka fito mata ajiki kamar k'anzuwa, ido waje kamar zata ruga a guje saboda tsananin tsoro, ganin Dadyn ta ne yasa ta dai-daita girman idonta suka dawo yafda suke, hawaye ne ke fita a idon kamar an bud'e famfo, bakinta na rawa ta ce.

"Dady"

Mutuwar tsaye Dady ya yi tare da k'ura mata ido, tashin hankali ne ke baibaye duk kan tsokar jikinsa ganin yadda Husnah ta fita hayyacin ta, juyawa ya yi ba tare da ya k'arasa inda take ba ya fita cike da masifa a fuskar sa, turaren wuta ne mai sirke da magani ya ziyarci hancinsa tun daga wannan lokacin bai kuma sanin inda kansa yake ba sai farkawa ya yi ya ganshi kwance bisa kan gadonsa, shuru ya yi na tsayin mintuna yana son ya tuna abin da ya faru, amma ya gaza tuna komai illa tunawa da ya yi ya dawo daga tafiya.

Momy ce ta shigo rik'e da tire na abinci ta ajiye ta matsa kusa da gadon sai ta ganshi ya farka, murmushi ta masa kafin ta ce wani abu ya ce.

"Hajiya ya aka yi na ganni a nan ni da ban dad'e da dawowa ba ko wanka banyi ba fa"

Murmushi ta masa mai cike da kissa.

"Haba dai ka ce ka manta, da k'afarka ka zo ka kwanta, ai kusan yanzu awa hud'u da dawowar ka, ka dad'e kana barci ga shi yanzu an kusa kiran Sallah Magrib shiyasa na zo na tasheka ko abinci ka ci"

Mamaki ne k'arara a fuskarsa.

"Awa hud'u fa kika ce?"

"Kwarai kuwa awa hud'u ka yi kana barci"

Mikewa ya yi da sauri ya fad'a bayi danya watsa ruwa. Momy bin shi ta yi da kallon mugunta tana k'issima wani abu a ranta.

_Momy sun je wurin wani boka, ya bata maganin mallaka da wanda zai mantar da Dady Husna, boka ya tabbatar mata da Alhaji na shigowa to karta bari ya d'auki lokaci ba tare da ta turare gidan da wannan turaren maganin. Lokacin kuma daya shiga d'akin Husna shi ne taje da sauri ta sanya maganin a wuta ta gauraye d'akin, Dady yana fitowa ya shak'i maganin, daga nan kuma da kyar ya iya kai kansa d'akinsa ya fad'a gado sai wani barci mai nauyi ya d'auke shi cike da mafarkai barkatai. Wannan shi ne abin da ya faru kafin awa hud'u da suka wuce._

Tun daga wannan ranar Dady baya tambayan lamarin Husna, daya dawo aiki tofa sai barci tunda dama bai dawowa da wuri, Momy burinta ya cika daga nan ta cigaba da abubuwa yanda take so, ta gama sangarta Nura duk abin da yake so taje masa, gaba d'aya baya karatun kirki in banda rashin ji da d'aukar magana babu abin da yake yi.

*****

Sadiq duk ya rame saboda tsananin damuwa, abinci sai ya yi da gaske yake iya ci, ulcer ya yi masa mummunar kamu, gabansa ke yawan fad'uwa duk lokacin daya tuna Husna, tun yana tambayar Baba labarinta har ya yi shuru sa idai su gaisa kawai, lamarinsa yana bawa Baba mamaki saboda ya lura sam baya cikin natsuwa kuma kuzarinsa ya ragu, a zuciyarsa yake cewa.

'Allah mai iko kai kad'ai kasan dalilin shakuwar yaron nan da Husna"

********

Husna sun koma makaranta da safe Jimmai ta shigo d'akin dan ta taimaka mata ta yi wanka tare da shiryata, Momy ce ta shigo d'akin dan ta sanya ta ta yi shirin makaranta, baki bud'e ta tsaya tana kallon Jimmai, ita kuwa Jimmai jikinta ne ya d'auki rawa domin ta tuna da gargadin da ta yi mata akan in har ta kuma shiga d'akin Husna a bakin aikinta, baki na rawa ta ce.

"Hajiya dan Allah ki yi hakuri naga ba tada lafiya ne shiyasa na shigo na taya ki shirya ta"

Bata bari ta k'arasa maganarta ba ta wanke ta da mari, ta ce.

"Zi zaki gayawa na yi hakuri? ai na gargad'e ki akai kuma kika karya min dokata, to ki sani yanzu ba sai anjima ba, ki tattara kayanki ki bar min gidana, matsiyaciya dama irinku baku iya cin arziki ba"

Kuka Jimmai ta fara yi tana yiwa Hajiya magiya, amma ina banda sirfa mata zagi babu abin da take yi, dole Jimmai ta tattara kayanga ta fito cike da k'unar zuciya, bata tsaya bawa Baba mai gadi labari ba tasa kai ta fita. Baba girgiza kai ya yi kawai, yaji duk zaman gidan ya gundure shi,

domin yadda yaga Jimmai, yasan cewa Hajiya ce ta koreta, kuma bai wuce dalilin Husna ba.

*Rahma ce*
[10/23, 3:49 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpad:*@rahmakabir

*_Page 23 ~ 24_*

Husna ta isa makaranta a latti, Anty Meena tana ganinta ta ce ta koma gida sai taji sauki sai ta dawo makaranta, haka tabar class d'insu jiki ba kwari, Khadija duk ta damu da taga kawarta ba lafiya. Husna a nesa da makarantarsu ta samu kan dakali ta zauna ta sanya fuskarta akan cinyanta tana kuka a hankali tare da nishi kad'an-kad'an na masara lafiya. Sadiq ne a cikin mota ya wuce ta da sauri, kamar ance ya duba madubin gefen motarsa sai ya hango yarinya, Sadiq shi mutum ne mai tausayi da taimako, hakanan yaji bazai iya wucewa ba dole ya yi ribas ya dawo kusa da ita ya yi parking, ba tare da ya fito ba ya bude murya yadda zata ji shi ya ce.

"Ke me kike yi a nan baki shiga makarantar ba? ko an koreki kud'in makaranta ne?"

Husna ta ji muryar da ba zata iya mantawa ba ya daki kunnenta, da sauri ta d'ago idonta wanda suke cike fal da hawaye, suka yi ido hudu da sauri Sadiq ya bud'e motar ya fito jikinsa yana rawa, da k'arfi ya furta.

"Husna me kike yi a nan, me yake damunki naga jikinki duk kuraje?"

Haka ya jero mata wannan tambaya wanda bata da amsarsu sai ma kukanta da ya k'aru ta tashi ta rungume shi tana shasshek'ar kuka, Sadiq yaji jikinta ya yi zafi sosai, da sauri ya d'auketa cak sai a cikin mota ya direta kana ya dawo mazaunin driver ya figi motar a guje kamar zai tashi sama. Wani asibiti dake kusa ya kai ta, cikin k'ank'anin lokaci ya yanki kati tare da ba shi damar ya shiga su ga likita, da yake asibitin na kudi ne ba layi, suna shiga suka ga wata matsiyar likita mai zuna Dr. Safiyya, nan ta shiga duba ta tare da rubuta musu gwajin jinin da za ayi mata, nan ya wuce da ita dakin gwajin jini, sun diba jininta suka dauki awa biyu suna gwaje-gwajensu, bayan sun gama suka basu sakamako sannan suka koma gun likita.

"Abin da ke damun Husna malaria da typhoid sai kuma ulcer daya kamata, wannan kurajen kuma k'anzuwa ce wanda kazanta ke kawota"

Dr. Safiyya ce kewa Sadiq wannan bayanin, idonsa ya yi jajir makar zai yi dan damuwa, nan ta basu gado dan sai an kwantar da ita, ya nima alfarman ayi musu treatment d'in yinin ranar in yaso zai rik'a kawota kullun har a gama mata komai, nan likita ta amince tare da kiran Nurse

Ruky ta zo ta karb'i folder d'insu tare da kaisu d'akin da aka kwanatar da su.

An sanya mata drip da duk wani magani daya kamata a bata, Sadiq ya siyo mata moltina tasha daga nan barci ya yi awon gaba da ita, ya nima alfarma gun Nurse Ruky ta kula masa da ita zaijye ya dawo, ba musu ta amince saboda taga yaro mai kyau da kwarjini zuciyarta ta kamu da son sa a lokaci d'aya. Su Ruky anga sweet guy lol😜.

Wurin aikinsa ya wuce ya d'auki uziri kana ya dawo, sai misalin karfe uku ruwan ya k'are sannan suka sallame su tare da umarnin su dawo gobe a cigaba da treating d'inta.

Gidansa ya wuce da ita, bayan sun shiga cikin falonsa ya ce ta zauna a kujera ta jira shi, ba musu ta zauna, d'akinsa ya wuce ya shiga bayi tare da had'a mata ruwan wanka mai zafi ya sanya mata dettol a ciki kana ya fito ya ce ta biyo shi a baya, da farko kamar bazyata bi shi ba saboda tana jin tsoro, da yaga haka sai ya tsaya ya lallasheta haka ta bi shi badan ta so ba, ya shiga da ita tare da nuna mata yadda zata yi wanka ya bata tawul wanda in ta gama zata d'aura, sannan ya nuna mata kayan da zata sanya inta fito, riga da wando fakistan ya siyo mata su tun a hanya kafin su shigo gidan, ta gyada masa kai alamar eh, kana ya fito ya zauna a falo yana jiranta.

Wanka ta yi sosai iya iyawarta, ta fito d'aure da tawul, ta zauna gefen gado, ta goge jikinta sannan ta sanya kayan da Sadiq ya siya mata, sannan ta d'aura d'an kwali ta fito, kallo ya bita da shi dan har kamanninta ya sauya akan na d'azu, murmushi ya yi mata kana ya koma ciki ya gyara ko ina sannan ya fito da mai wanda zata rika shafawa saboda kurajen jikinta ya ce ta shafa, bayan ta shafa sannan ya d'auko ledan take away daya yi musu ya bata nata sannan shima ya d'auki nashi suka faraci. Bayan sun gama ya tashi da sauri ya d'auro alwala ya ce ita ma taje ta yi, ya tayar da sallah harya idar ita ma tana biye da shi duk abin da ya yi shi take ta yi, ba zai iya barinta a gidan ita kad'ai ba shiyasa ya yi sallar la'asar dinsa a gida. Wasa ya fara janta da shi nan da nan ta saki jiki ta fara walwala, sune har kusan k'arfe biyar suna buga game a computer d'insa, jin karar bugun k'ofar gidansa ne ya katse su, ko da ya fita ya bud'e gate din sai ya ci karo da Baba mai gadi, ko gaisawa bai bari sunyi ba ya ce.

"Sadiq ba a ga Husna ba tun d'azu data tafi makaranta, kuma anje makarantan ba a ganta ba shi ne na zo na sanar maka"

Sadiq hankalinsa a tashe ya ce.

"Subhanallahi Baba me kake fad'a haka? Husnar tawace ba a ganta ba? ya salam, ina zuwa bari na sauya kaya na fito"

Sadiq ya koma ciki ba tare da ya jira amsar Baba ba, yana wani murmushi a ransa, ya kunnawa Husna tv kana ya ce ta jira shi zai je ya dawo, key ya d'auka ya kulleta ta baya kana ya fita ya samu Baba.

"Mu je mu bincika ta ko Allah zai sa mu ganta"

Haka kuwa suka shiga zagaye unguwar a k'afa, tare da tambayar mutane harda kwatancen surarta, kowa suka tambaya zancen d'aya ne basu ganta ba, haka suka gama bulayi basu ga wata yarinya mai kama da Husna ba, dole suka juyo gida jugum-jugum hankali tashe. Ta b'angaren Sadiq kuwa a cikin zuciyarsa hankalinsa kwance yake, yana k'issima ko Husna ta yi barci ko k'ila kuma tana wasa, ya yi murmushi a ransa ya ce.

'Baza ku tab'a ganin ta ba kuwa har sai na tabbatar taji sauki sannan zan bayyanata'

A ranar dai Momy tana Addu'ar Allah yasa ta b'ace kenan bazyata dawo ba, a fili kuma harda kukan munafunci, ko da ta zantawa Dady bacewar Husna ya nuna ko a jikinsa bai saima ya ce.

"To ai ita ta sani tunda bata jin magana, wato haukar nata ya tabbata kenan, tunda bata san ta dawo gida ba, to Allah yasa bata yi nisa ba"

Abin da ya iya fad'a kenan ya cigaba da harkokinsa.

*****

Sadiq daya koma gida ya sameta tay i barci ga hawaye ya bushe a kuncinta, alamar ta yi kuka sosai, ya tasheta ra farka a firgice da ta ga shi ne sai ta rungume shi tana son yin kuka, Sadiq ya yi murmushi.

"Yi hakuri my Husna, na yi miki laifi ban dawo da wuri ba ko?"

Cikin shasshek'ar kuka ta ce.

"Ni ka kai ni gida ina tsoro kar Momy ta duke ni"

"Husna yau ba zaki kwana a gida ba, tare da ni zaki kwana har sai kin ji sauk'i zan maidaki gida"

Cike da rashin yarda Husna ta girgiza kai ta ce.

"Uhum ni dai ka mai dani gida karta duke ni"

Sadiq ya shiga lallashinta  da kyar ta yarda zata kwana.

Haka dai ta kwanta bisa gadonsa a d'arare, shi kuma ya kwana a falo kan doguwar kujera zuciyarsa fari k'al ba d'igon damuwa a ciki.

_Ya labarin zai ƙare? Tiryashi! akwai sauran cakwakiya_

*Daga wannan shafin 23-24, na yanke muku kuɗin samun cigabansa har zuwa ƙarshe, a cikin farashi mai sauƙi ta yadda zaku iya siya a sauƙaƙe.*

Don samun cigaban wannan littafin har zuwa ƙarshensa, a biya N100 kacal. A tura ta wannan account number. 👇🏾
Ramatu Muhammad kabir.
Acc no- 0106956864
Diamond bank.
A turo shaidar biya ta wannan number 07036993733.

Ko a turo katin MTN N100 ta wannan number 07036993733.

*Rahma ce*
[10/24, 8:02 PM] Rahma Kabir🌺: *KAƊAICI*

© *Rahma Kabir*

*Wattpdad:*@rahmakabir

*_Page 25 ~ 26_*

*Bayan kwana Uku*

Husna ta gama amsar treatment d'inta, ta ji sauƙi sosai k'urajen jikinta duk sun soma mutuwa kad'an ne suka rage, ta yi kyau, har d'an k'iba ta yi, hasken fatarta ya fito, ta saki jiki sosai da Sadiq sai dai lokaci zuwa lokaci tana yi masa maganar ya mai da ta gida, haka yake fita aikinsa da safe, da rana ya dawo ya kawo mata abinci in sun ci sai ya koma, zuwa yamma ya dawo, ba zai sake fita ba sai wata safiyar.

Momy ta saduda da Husna ta b'ace, Dady ya sanya a nemota amma har yau shuru, har gidan radio ya sanya a sanar cewar.

"Yarinya ƴar kimanin shekara takwas mai suna Husna, ta b'ace sanye da uniform d'in karanta a jikinta tana da matsalar kwakwalwa, ba tada hankali sosai, sannan siririya ce fara mai yawan suma a kan ta"

Haka suka yi ta yad'a sanarwa, wanda Sadiq ya saurara a radio motarsa, murmushi kawai ya yi ya cigaba da harkokinsa

*******     *******

*Mako d'aya*

Da b'atar Husna amma ba amo ba labari, a b'angaren Sadiq kuwa yana cike da farin ciki sosai yadda ta sauya ta yi kumari sannan sun k'ara shak'uwa sosai, uniform d'in da ya wanke mata ta sanya tare da rataya jakarta, tana dariya ta ce.

"Uncle yau zani makaranta na ga k'awata kuma yau zan koma gidanmu ko?"

Sadiq ya yi Murmushi na rashin farin cikin rabuwarsu.

"Eh yau zaki koma amma fa kar ki gayawa ko a nan gidan kika zauna kin ji, in kika fad'a zan d'auko sojoji su kama ki kuma su d'aureki su bawa zaki ya cinye ki"

Husna ta zaro ido waje tare da toshe bakinta cike da tsoro ta ce.

"Wallahi ba zan fad'a ba Uncle, dan Allah karka sa su kama ni"

Dariya ce taso kuɓuce masa amma sai ya gimtse.

"Ai in baki fad'a ba, ba zasu kamaki ba"

Ta d'ago kai suka had'a ido, gira ya d'aga mata.

"Yes ko zaki fad'a?"

Da sauri ta girgiza kai.

"Ba zan fad'a ba"

"Good girl zo mu tafi ko"

Haka suka fito suka shiga mota suka wuce, bayan sun ƙarasa in da ya d'auketa ran nan, a nan ya ajiye ta sannan ya bata naira d'ari ya ce ta shiga makaranta, a kan idonsa ta shiga kana ya wuce office.

Cike da mamaki Anty Meena ta ga Husna, ta san ance ta b'ace kuma ko yau an sanar a Assembly, da sauri ta kira headmaster ta sanar masa, kan ace miye duk Malaman makarantar sun taru a kan Husna suna faɗar albarkacin bakinsu, Number Dady suka kira suka sanar da shi halin da ake ciki, da sauri ya bar gurin aiki ya zo yaga abin mamaki, suna had'a ido da shi ta fara ja da baya hawaye na fita a idonta, hankalinsa ne ya tashi, a yanzu ne yake jin wani iri a jikinsa, cikin sanyin jiki ya ce.

"Husnahhh"

Da gudu ta ruga ta rungemshi tana kuka, an kira ƴan sanda sun yi mata tambayar duniya amma taƙi ce musu komai, domin ta tuna zancen da Sadiq ya gaya mata, shiyasa taƙi magana haka aka sallamesu ba tare da wani bayani ba.

Dady gida ya wuce da ita, Baba mai gadi yana ganinsu ya gaishe da Alhaji tare da nuna farin ciki sosai na ganin Husna, bayan sun shiga ciki Momy cike da tashin hankali ta tarbe su sai ta fara wani rik'eta irin tana cikin farin ciki da ganin ta, Husna dai gum ta yi yana tsoron kar ta yi mata wani muguntar, nan Dady ya gama abin da zai yi ya koma office, yana fita Momy ta kama kunnenta tana ja.

"Dan ubanki ina kake je? kina k'aramarki kin fara yawon ta zubar ko, wallahi sai na yi maganin ki, iye ji yadda kika canza, daga ɓacewa har ƙiba kika yi, ko ma dai aljanu ne suka d'aukeki ne?"

Husna kunnanta ya fara mata zafi saboda Momy da k'arfi ta rik'e tana jaa, da ta ga ba sarki sai Allah sai ta mamayeta ta ganna mata cizo a hannu, da sauri Momy ta sake ta tana yarfe hannu tare da jifarta da mugun kallo irin zaki ci ubanki, Husna tana ganin haka sai ta ruga d'aki da gudu tana haki. Tsoro da mamaki ne ya cika Momy tana tunanin wani mataki zata d'auka, d'aki ta bita ta daka mata tsawa, Husna ta sauko daga gado tana kama jikinta, Momy ta ɗaga hannu zata kai mata duka Husna ta saki wani irin razanan nan k'ara wanda ya kaɗa hantar cikin Momy, idanun Husna suka sauya kala zuwa ja kuma sun fiffito waje tare da gunji kamar wata zakanya, Momy tsoro ya gama rufe ta, ba arziki ta fita daga d'akin a sittin tana waige, tana fita Husna ta dawo dai-dai sai ta saki dariya tana kyalkyalewa, bayan ta gama ta haye gado ta kwanta barci, ba ita ta farka ba sai ƙarfe biyun rana.

Husna ta fito falo ta samu Momy zaune a falo tana cin abinci a plate ga juice da cup a gefe, tana ganin Husna gaban ya faɗi sai ta yi saurin kauda kanta ta cigaba da cin abincinta, Husna tana ganin abinci cikinta ya soma kuka, nan take fuskarta ya sauya ta gwalo ido waje wanda suka sauya zuwa ja, sai ta saki murmushi ta tunkaro wurin Momy, tana isa ta sanya hannu ya fizge plate ɗin tana cewa cikin wani irin murya.

"Muguwa kawo shi nan ai Abbana ya siyo"

Momy sakin baki ta yi tana kallonta jikinta babu in da baya ɓari, ta kasa kallon fuskar Husna sai sunne kai take, Husna ta sheƙe da dariya ta aje plate ɗin a ƙasa ta ɗauki juice da cup ɗin ta aje gefe ta zauna ta tankwashe ƙafa ta fara cin abinci hankalinta kwance, Momy ta zuba mata ido ta kasa cewa komai zai zare ido take kamar maƙaryaciya.

"Tashi ki bani guri kafin in illata idanunku muguwar Mata kawai, kina kallonta sai kace mayya"

Cewar Husna ta ɗago kai tana kallon Momy tare da danƙara mata harara.

Momy ta miƙe a zabure ta kama hanyar bedroom ɗinta tana waigen Husna cike da tsantsar

tsoro har ta shige ɗaki, haka ta jiyo dariyar Husna kamar wata ƙatuwar mace, Momy taji fitsari ya kamata da gudu ta faɗa toilet tana haki.

******

Tun daga wannan ranar Momy ta soma tsoron Husna ko tsawa Momy ta daka mata, ita ma zata rama da tsawa mai cike da firgitarwa. Ba arziki Momy ta koma gun boka ta yi masa bayani, sai ya ce iskanci ne kawai amma ba wani abu, domin shi dai ya yi bincike bai ga komai ba, sai ya bata wani ƙullun magani da zata turare ɗakin Husna da shi. Haka dai Momy ta dawo gida jiki a sab'ule, ta samo rushin wuta ta sanya wannan maganin da boka ya bata ta nufi d'akin Husna, ta shiga tana rik'e da kaskon wutan yana fidda hayak'i, Husna tana zaune ta ɗago kai, suna haɗa ido, Momy ta ji gabanta ya fad'i, cikin kakkausar murya Husna ta ce.

"Me kike yi a nan? ki fita min da k'azantar nan tun kafin in illata ki muguwa azzaluma"

Cikin tsoro Momy ta fita daga d'akin jiki na rawa, taje ta kashe wutan ta dawo falo ta zauna a kujera tare da rafka tagumi, Dady ne ya shigo ya sameta a haka sai ya samu wuri ya zauna.

"Hajiya lafiya kike zaune shuru?"

Kwalla ya sauka a kuncinta.

"Ni fa Alhaji tun dawowar Husna sati biyu kenan na kasa gane kanta, kamar an chanza mana ita fa"

Nan ta shiga ba shi labarin k'arya da gaskiya, Dady ya yi murmushi kawai ya mik'e tare da cewa.

"Haba Habeeba ke da kika fi kowa sanin Husna ba tada lafiyar kwakwalwa, shi ne zaki tayar da hankalinki, kawai Addu'a zamu cigaba da yi mata, ni zan shiga ciki in watsa ruwa"

Bai jira me zata ce masa ya wuce abin sa, Momy ta bi bayansa da harara tana jin haushin yadda ya ƙi nuna kulawarsa a kan maganarta, Husna ta fito falon tana yatsine fuska, ta kalli Momy.

"Ƙarata kika kai gun Abba ko? to ko zaki kwana dubu ne kina gaya masa babu wani action da zai ɗauka, mu zuba dani da ke, shaiɗaniya kawai mara tsoron Allah"

"Husna ni kike gayawa haka?"

"An gaya miki ɗin mai bin boka"

Ta yi maganar cike da tsiwa tana murguda mata baki tare ta jan guntun tsaki. Sai ta fice da gudu tana dariya, Momy ta bita da kallo cike da mamaki da tsoro, ta rasa gane kan Husna

shakka take a kan anya ba a sauyata ba kuwa?. Husna tana fita ta tsaya ta saki wani atishawa mai ƙarfi kana ta dawo asalinta ta wuce gun Baba mai gadi.

Tun daga wannan lokacin Husna ta samu freedom, sai dai an saketa sakaka ba wani kwab'a saboda yanzu Momy tsoranta take ji sosai, bata iya yi mata maganar komai, shi kuma Dady aikinsa ya sanya a gaba, ba ruwansa da lamarin lafiyar Husna domin asirin da Momy ta yi masa tana nan a jikinsa, yanzu tana fita wurin Baba su yi hira, wataran ma da Sadiq suke hirarsu, Dady da Momy dai sun zubawa Husna ido ba mai iya katab'us a kanta.

******* ******

*A Kaduna*

Husna pharmacy ya bunk'asa sosai har bayar da sarin magani suke yi, hankalin Zainab ya kwanta har wani k'iba ta yi, daga nan kuma sai manema suka yi mata ca, amma sam tak'i amincewa, kowa dai yana iya k'okarinsa wajen ya samu zuciyarta amma tak'i bari, a ciki harda Dr. Idris ya nuna yana sonta amma tak'i, ko da su Baffa suka yi mata magana sai dai ta ce su ta ya ta da Addu'a, dole suke hak'ura saboda basa son takura ta, Addu'a suke mata da fatan samun miji nagari. A zuciyar Zainab kuwa burinta bai wuce Khalil ya dawo gareta ba, tana tsananin kewar ƴarta Husna, lokuta da dama tana kashe lokaci ta zauna tana tunanin rayuwar da suka yi a baya, duk farin cikin da take ciki a yanzu bai kai farin cikin da za a ce ta wayi gari ta ga Khalil da ƴarta ba.

*Rahma ce*
[10/25, 10:16 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 27 ~ 28_*

*Bayan kwana biyu*

Momy tana zaune a falo Husna ta fito ta samu Momy tana amsa waya, bayan ta gama ta miƙe da sauri ta nufi ɗakinta, Husna ta miƙe tabi bayanta tana yin wani shu'umin murmushi.

"Zanga yadda zaki fita yau"

Ta ce, ta isa ɗakin taga Momy bata nan tana toilet, da sauri ta cire key dake jikin ƙofa ta fito ta jawo ƙofar ta sa key ta rufe ta baya, kana ta bar key ɗin a ciki ta yi gaban a binta tana dariya, taje ta can bayan window Momy ta tsaya dan ta san ƴila ta leƙo ta nan. Momy ta fito daga toilet ta shiga shiryawa sauri-sauri, bayan ta natsa ta yafa gyale ta ɗauki makullun mota tayo hanyar ƙofarta, ta kama handle ɗin ƙofar ta ja sai ta ji a kulle yake gam ta duba key baya jiki, ta ƙara sanya ƙarfinta ta ja sai ta ji fa a kulle yake sai ta shiga niman makullin ɗakin, ta yi nimar duniya bata ganshi ba, Husna ta ji ɓuruntu ya yi yawa daga cikin ɗakin sai ta kyalkyale da dariya, Momy ta ji dariyar sai ta yi saurin buɗe windon suka haɗa ido, Husna ta sauya idonta ya koma

hararagarki ta zaro su waje kana ta kama gefen bakinta da hannu biyu ta wage bakin ta zazzago harshenta tana yararin miyau, Momy tana ganin haka ta saki labule ta shiga kiran sunan Allah, ta yi mugun tsorota, a ganinta ba Husna bace tana ganin Aljana ce ta yi suffarta, Husna ta saki abin da ta yi ta kwashe da dariya, Momy ta kuma buɗe labule sai taga Husna ta dawo dai-dai, Husna ta shiga nuna ta tana dariya.

"Yeeee na bawa Momy tsolo, ba kin ce zaki fita ba to ba zan bari ki je ko ina ba, muguwa kawai"

Ta ƙare maganar tana murguɗa baki sai ta bar wurin windon ta wuce ɗakinta, tana isa ta fada gado barci mai nauyi ya yi gaba da ita. Haka Momy ta yini a ɗaki kuma ikon Allah gidan ba kowa daga ita sai Husna, ko ta yi ihu ba mai jinta, haka ta zauna gefen gado tana cika tana batsewa iya ƙuluwa ta yi, ƙarshe haka barci ya ɗauketa mai nauyi har tsawon wani lokaci.

Dady ya dawo gida da misalin ƙarfe shida na yamma, ya samu falon ba kowa sai kawai ya doshi ɗakin Momy, ya samu a rufe yake ta waje.

"Ohhh ita kuma Hajiya ina taje haka bata sanar min ba"

Ya yi maganar a zuci yana buɗe ƙofar da key, da sauri Momy ta taso ta dawo kusa da ƙofar don ganin wanda ya buɗe ta dan ta jima da farkawa, ta yi alƙawari yau sai ta zane Husna ko da zata bata tsoro, da mamaki sai ta yi kicibis da Dady suna kallon juna da mamaki.

"Hajiya ya na ga dakinki a rufe ta baya kuma kina ciki? harda na yi zaton ko kin fita ne"

Momy bata iya ba shi amsa ba ta fashe da kukan baƙin ciki tare da bin gefensa ta isa falo tana kwalawa Husna kira a hargitse, Dady ya biyo bayanta yana tambayarta ko lafiya? bata amsa ba sai da taga fitowar Husna, idon nan nata cike yake fal da barci alamun kiran Momy ce ya farkar da ita. Momy ta zauna cike da jin haushi ta ce tana nuna Husna.

"Ka ga shegiyar data rufeni a ɗaki tun misalin ƙarfe biyun rana, har zuwa yanzu daka buɗe ni"

Ta kwashe komai ta gaya masa, Dady ya tari numfashinta.

"Anya Husna zata iya rufe mini ɗaki? Du du du kwaya nawa take? Shekarunta takwas har da zata iya aikata haka? Zo nan Mamana ki faɗa min gaskiya, Ke ce kika rufewa Mominki ƙofa?"

Husna ta matsa gaban Dady tana murza ido cike da shagwaɓa, ta girgiza kai alamar a'a, ya cigaba da tambayarta ta tana ba shi amsa da kai taƙi ta yi magana, Dady ya kai dubansa ga Momy.

"Hajiya sai dai in ke ce kika manta kika santa key ta baya kika rufe kanki, ya kamata ki cire Husna a sabgarki saboda ba tada hankali, kwakwalwarta bata aiki balle harta san ta yadda zata rufe miki ɗaki"

Yana gama faɗar haka ya miƙe ya wuce ciki, Momy kamar ta ɗaura hannu a kai ta yi ihu, a yau ta yi nadamar ɗaurawa Husna cutar hauka, tunda duk abin da take yi mata ba wanda zai yarda saboda ba tada hankali, hawaye ne ya shiga bin kuncinta tana kallon Husna kamar ta tashi ta kasheta, sai dai babu halin yin haka, Husna ta kalleta ta yi mata gwalo tana karkaɗa jikinta tana dariya, haka ta juya zuwa ɗakinta tana muguɗawa Momy ɗan ƙaramin mazaunanta. Momy ta cije leɓe tana jin ƙuna a ranta, takaici da baƙin ciki ya gama rufeta, ta rasa ta wace hanya zata bi ta hukunta Husna.

*******

Haka Momy ta cigaba da zama da Husna tana yi mata iskancin da ranta ya ke so, gaba ɗaya ta ji duniyar ya yi mata zafi, duk wasu dubaru kanta ya kulle baya kawo mata haske, duk a abin da ta shiryawa Husna tofa sai ta lalata mata shi, haka rayuwa ta yiwa Momy zafi, daga ƙarshe sai ta tattara lamarin Husna ta sanya a gefe ta dai na shiga lamarinta, abinci kuwa dole ta girka ta kai mata har ɗaki in ba haka ba a ranar sai Husna ta ja mata asara, haka rayuwa ta yi ta gudana a wannan gidan, da daɗi ba daɗi har zuwa tsawon lokaci.

****** **** *******

*BAYAN SHEKARA HUD'U*

Husna ta shiga matakin secondary school tana jss 1, da yake makarantarsu akwai secondary nan ta cigaba da karatu. Ta k'ara girma da wayo sai dai kuma zuwa yanzu surutunta ya ragu sai ta koma shuru-shuru, saboda yanzu komai ita ke yiwa kanta tun bata iya ba har ta soma sabawa da hakan, rayuwa ita kad'ai take yi a cikin gidan ba mai kula ta ko shiga tsabgarta, a in da take samun kulawa daga gun Sadiq sai Baba mai gadi, a makaranta kuwa sun k'ara shak'uwa da Khadija ajinsu yanzu ma d'aya, komai na su d'aya, da yake yanzu ta yi wayo bata zuwa da k'azanta kullun tana k'ok'arin tsaftace jikinta, bata fiye fita yawo ba iya karta bakin gate, kwata-kwata bata san komai game da Addini ba, Baba ke k'ok'arin koya mata shima sai ya yi dagaske ne take iya d'aukan karatun, dan bata samu foundation mai kyau ba.

******* *******

*Kaduna*

Anty Zainab zaune suke a falo suna hira da Umma da Anty Jidda, hira suke sosai sai ga wani yaro an aiko shi daga waje ana sallama da Zainab, cikin fushi ta ce.

"Ka je ka ce bata nan"

Yaro ya fito jiki a sab'ule.

"Haba Zainab meyasa kike haka ne, ki fita ki ga ko waye mana wulaƙanci babu kyau, kuma ai

ba zaki zauna haka ba tare da aure ba, ni bani son shirme"

Cewar Umma, Zainab ta b'ata fuska tana jin haushi.

"Umma ni dai ku yi hak'uri ba zan fita ba, ku kyale ni da zancen auren nan, ba yanzu ba"

Anty Jidda ta yi caraf ta ce.

"Aiko baki isa ba, aure wajibi ne ki yi shi, ai zama haka bai dace dake ba tunda da kuruciyarki, ni da za ki ji shawarata ma ki amincewa Dr. Idris ya fito ku yi aure kawai, tunda kinga shi saurayi ne yana sonki sosai, kuma auren ki biyu amma duk da haka ya ce ya amince"

Zainab lokaci d'aya ta ji zuciyarta ta dagule har hakan ya nuna a fuskarta, nan ta tuno da Khalil da Husna abar ƙaunarta, hawaye ya fara fita a idonta, jikin Anty Jidda ya yi sanyi Umma ma haka, Zainab ta ce cikin kuka.

"Anty Jidda a kullun aka min zancen aure ana tada min da tsohon mikin dake manne a zuciyata, kina ganin zan iya wani aure a yanzu bayan auren Khalil da marigayi yaya Al'amin? wallahi ba zan iya ba, in dai Khalil yana raye to ina nan ina jiransa sai dai in yaƙi karb'ata a karo na biyu, shi ne zanyi haƙuri in auri wani"

Kuka ne ya ci k'arfinta ta mik'e da sauri tabar falon cike da k'unar zuciya

"Ikon Allah, to Allah ya kawo miki mafita Zainab, lamarinki ni yanzu har tsoro yake bani, amma ta yaya zaki sanya ran k'ara ganin Khalil? bayan alƙawari ya yi ba shi ba gidan nan, in da zai zo ai da tuni ya zo, Allah kad'ai yasan rayuwar da suke ciki yanzu, ohh ko wani hali takwarata take ciki Allah kad'ai masani"

Cewar Umma, ta ji bugun zuciyarta ya k'atu, wani hawaye mai zafi ya fito daga idonta, ta kuma cewa.

"Wallahi da Husna nake kwana nake tashi a raina, a kullun ina tunanin ya rayuwarta take ciki? ban san cewa yarinyar ta shiga zuciyata ba sai bayan barinta gidan nan, Allah kasa tana rayuwar jin daɗi"

Anty Jidda da idonta ya kawo kwalla ta amsa da Ameen.

Nan suka cigaba da hira har tsawon wani lokaci, kiran sallan la'asar ne ya tada su ko wanne ya nufi ɗakinsa.

******** ********

*Kano*

Da safe Husna ta yi shirin makaranta ta fito da sauri dan ta kusa latti, karo taci da mutum a bakin k'ofar da zai sadata da waje, yaya Nura ne a tsaye fuskarsa tamau ba alamar annuri, ya girma shima dan ya kai sheraka ashirin da biyu, ya ce cikin tsawa.

"Dan ubanki baki gani ne zaki bangaje ni, mahaukaciyar banza dana wofi"

Husna ta murgud'a masa baki.

"Eh d'in ba kai bane ka tsaya a anya kuma ni ba mahaukaciya ba ce"

"Ni kike gayawa haka?"

Sai ya d'aga hannu zai gaura mata mari, Husna gaba d'aya ta runtse ido ta k'ank'ame tana jiran saukar marin, Nura ya tuna wani abu sai ya girgiza kai ya sauke hannunsa ya fasa marinta yana murmushin mugunta.

"Soon zan yi maganin ki"

Ya yi kwafa sannan ya matsa ta wuce tana masa gwalo, dariya ta ba shi ya ce.

"Zaki shigo hannuna wallahi sai na rufe bakin rashin kunyar nan"

Ya fara k'issima abin da yake shiryawa a kanta, ya yi dariya kana ya wuce cikin d'akinsa ya kwanta, saboda yau baya sha'awar zuwa makaranta dan shi karatun baya gabansa sai shaye-shaye da biye-biyen 'yan mata.

Husna ta isa makaranta suka had'u da Khadija suna hira.

"Husna in mun yi hutun makaranta a Kaduna zanyi hutuna gurin kakanni na, in gaya miki akwai wata ƙanuwar Abbana mai kirki inna je d'akinta nake sauka tana siyo min kayan dad'i da yawa kuma har office d'inta tana zuwa dani, yaron ta little Al'amin mai kyau wallahi in ta wasa da shi"

Husnah ta yi rau-rau da ido kamar zata yi kuka.

"Kin ji dad'i, ni Dadina bai tab'a kai ni ko ina ba kullun ina gida, da Dady zai yarda dana biki mu yi hutun tare"

"Aiko dana ji dad'i, kin ga sai Anty Zainab ta rik'a fita damu tana siya mana kayan dad'i, kuma wallahi zata so ki saboda tana da son yara sosai"

"Uhum ai Dady ba zai bari ba, baya siya min komai yanzu bana ganin shi sai weekend kuma ya dai na wasa dani, yanzu Uncle kad'ai yake so na sai Baba mai gadi"

Ta k'arasa maganar kwalla na fitowa daga idonta, Khadija ta jinjina maganar duk jikinta ya yi sanyi.

"Ki daina kuka ai Allah zai saka miki, nima kin ga yaya Sadiq d'inmu wallahi ina son shi saboda yana siyo min kayan dad'i da kayan wasa, a nan Kano yake aiki, duk weekend yana zuwa gidanmu"

Nan dai su kai ta hiransu gwanin sha'awa har aka tashe su makaranta.

********    *********

Bayan sun gama exam din k'arshen zangon jss 1, su Khadija suka tafi Hutu Kaduna, Husna taso ta bisu amma bata ga fuska gun Dady ba balle ta masa maganar, ga shi Uncle Sadiq d'inta shima ya tafi hutu wurin iyayensa a Kaduna, kuma sai ya yi sati biyu zai dawo, haka ta cigaba da zama shuru ko wurin Baba bata fitowa, daga falo sai kitchen kullun tana d'aki, wani lokaci ta yi kuka mai isar ta, wani lokacin kuma ta rik'a yin surutu ita kad'ai kamar mahaukaciyar gaske har barci ya sace ta saboda ƙuncin *KAƊAICI.*

**********

*Kaduna*

Khadija sun fara Hutu mai cike da jin dad'i da farin ciki, duk suna falo gaba d'aya banda iyayensu maza, Khadija ta soma basu labarin k'awarta Husna da ta so ta biyo su, nan da nan Zainab ta ji zuciyarta ya harba da k'arfi, a'uzubillahi ta rik'a karantawa a zuciyar ta, Khadija ta cigaba da basu labarin yadda Husna ke wahala a gidansu. A duk hutun da zasu zo Kaduna Khadija sai ta yi hiran Husna, sai dai abin mamaki takan yi hirarta ba tare da ambaton sunanta ba, sai dai ta ce k'awata sunan da take kiranta kenan, kuma ikon Allah ba wanda ya damu da yaji sunan ƙawarta ta a tunaninsu duk shirmen Khadija ce, haka take surutunta ba mai kulata har ta gaji ta yi shuru, lokacin barci ya yi kowa ya kama gabansa.

Zainab ce kwance a kan gado tana ta juyi damuwa ce fal a zuciyarta, ta tashi ta zauna ta duba gefenta na dama Khadija ce kwanta sai barci take yi, gefen haguntа little Al'amin ne da Kamal k'anin Khadija, d'aga kanta ta yi sama hawaye mai zafi yana fitowa da idonta tana zancen zuci.

'Ko wani hali Husna take ciki? Allah kad'ai ya sani, Khalil meyasa zaka min haka, ban tab'a tunanin zaka yi nesa dani irin haka ba, ka tafi ka barni da guba azuciyata wanda har yau ban samu ganinta ba. Allah ka bayyana min su na yi tozali da su kafin nabar duniya'

Ta shafa a fuskarta tare da mik'ewa ta shiga toilet ta d'auro alwala, ta fito ta shiga gabatar da

sallar nafila har gabanin sallan Asuba, ana kira ta mike ta gabatar da sallar Asuba, ta yi Addu'a ta mik'e ta hau gado, nan take wani nannauyar barci ya d'auketa mai dad'i.
[10/26, 8:01 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 29 ~ 30_*

*Bayan Shekara biyu*

Shekaru sun ja kwanaki sun shud'e, haka Husna ta cigaba da zama a cikin wannan rayuwa na *Kad'aici*, karatunsu ya yi nisa, a yanzu sun kammala final exam na jss 3 zasu shiga ss1, shekararta sha hud'u a duniya, ta kara tsawo da girma sosai, sai kuma ta kara wayo, kyawunta ya dad'a fitowa sosai, ta soma k'irgen dangi natsuwa ya shigeta, duk wani tsalle-tsalle yanzu bata yin shi, shuru shurun ta ya k'aru, magana sai ya zama dole take yinsa, amma kuma ikon Allah in dai da Uncle Sadiq ne, hira take da shi sosai kamar ba ita ba, shakuwar su ya k'aru sosai duk wani abin da ya shafeta shi yake mata.

Da safe tana kwance bisa gado, barci take mai cike da mafarkai barkatai, fitsari ya matseta ya k'ulle mata mara sosai, da sauri ta farka ta fad'a bayi, ta tsuguna ta yi da tsarki, mik'ewar da zata yi sai taga jini baje a k'asa, ido ta zaro waje kamar zasu fad'o k'asa saboda tsananin tsoro, pant d'inta ta duba sai ta ga ya jike da jini, a razane ta cire shi ta jefar gefe, ta fito ta sanya wani pant d'in, ta fito falo cikin sauri ta tadda Momy zaune tana karanta wani littafi, jikinta yana rawa ta isa gun Momy, ta ce cikin rawar murya.

"Momy, Momy  jini a jikina"

Ta fara kiciniyar d'aga siket dinta dan ta nanuwa Momy pant d'inta da shima ya k'ara baci da jini, wani mugun kallo Momy ta bita da shi.

"Dan ubanki ni sa'ar yinki ce, to ba jini ba ko da tsokar jikinki ne bai shafeni ba, kima mutu mana sai me, tsakani na dake bamu sulhu har abada, idan kin mance wahalar da kika bani a baya to ni ban mance ba. Husna na tsaneki bana kaunar ganinki a gidan nan, maza b'ace min da gani tun kafin in harzuk'a inyi watsa-watsa dake a nan, wawiya jaka"

Jikin ta yana rawa ta matasa nesa da ita, ta shiga rera kuka kamar ranta zai fita, Momy tashi ma ta yi ta barta a nan falo ta kowa d'aki cike da jin haushinta. Husna ta tsaya shuru tana nazarin mafita, ta ga ba sarki sai Allah, da azama ta fita waje bata ga Baba mai gadi ba, baya bakin gate da sauri ta bud'e k'ofar ta nufi gidan Uncle Sadiq d'inta, ta yi sa'a k'ofar gidan a bud'e yake tana turawa taga ya bud'e a sittin ta shiga, k'ofar falon ma a bud'e ta samu ta kutsa kai ta shige, zaune yake a falo kan cushing yana danna system d'insa, ganinta ya yi ta fad'o d'akin a guje ba sallama tana haki kamar an korota, ta kara fashewa da sabon kuka, a firgice ya aje system d'in ya taso cikin sauri ya shiga tambayar ta ko lafiya? Ta kara sautin kukan ba sassauci, hankalin Sadiq ya k'ara tashi dan a iya saninsa da ita bata yin kuka irin haka sai in wani abun ya tsananta, kuma rabon da yaga kukanta irin haka tun tana k'arama da Momy take dukanta, ya k'ara rikicewa ya ce cikin damuwa.

"Haba Husna ki gaya min me aka yi miki ko wani ne ya rasu? Gaba daya duk kin tayar min da hankali"

Husna ta girgiz kai alamar a'a.

"To me aka yi miki? gaya min mana Husnata"

A wannan lokacin sai ta sassauta kukanta ta ce cikin muryar kuka.

"Uncle zan mutu"

"Da a ka yi miki mene?"

Husna bata ba shi amsa ba sai ta shiga kiciniyar daga siket d'inta ta kai shi zuwa gwiwanta, ta zazzago da pant d'inta, Sadiq dai ya zubawa sarautar Allah ido dan ganin wauta da shirmen Husnar.

"kalla ka gani, jini ne a jikina"

Ta ce da rawar murya, bai iya gani ba da sauri ya kauda fuskarsa.

"subhanallahi! Meye haka Husna? maza ki mai da pant din"

Ya yi maganar yana kunshe dariya amma sai da ta kubce ya yi mai isar sa, Husna ta tsayar da kukan ta soma kallonsa sororo baki bud'e, mamaki ne k'arara a fuskarta.

"Uncle dariya kake yi zan mutu ko, mai makon ka yi kuka shi ne zaka rika murna ko"

Nan take Sadiq ya tsanye dariyarsa.

"A'a Husna ba zaki mutu ba akwai sauran lokaci insha Allah, yanzu jirani ina zuwa"

Bai jira me zata ceba ya shiga bed room d'insa, ya hada mata ruwan wanka a toilet, ya lek'o ya kirata ta bi bayansa har toilet din, ya nuna mata ruwa.

"Ga shi nan ki yi wanki mai kyau, ga tawul nan ki d'aura kafin ki fito zanje na siyo miki kaya yanzun nan sai ki jirani in kin gama karki mai da kayan jikinki"

Gyada masa kai kawai ta yi alamar to sai ya fita ya barta ya dauki key mota ya fita cikin sauri.

Harta kammala wanka ta fito bai dawo ba, ta kasa zama a gefen gadon tana tsoron karta b'ata masa zanin gado tunda har yanzu jinin yana d'iga, da sauri ya turo k'ofar bed room d'in ya kutso

kai duk tunanisa bata fito ba, gabansa ne yaji ya fad'i yadda ya ganta daga ita sai tawul, runtse idonsa ya yi na tsayin minti biyu kana ya bud'e a hankali, wani bakon yanayi yaji yana masa yawo a jikinsa, kau da kansa ya yi gefe jikinsa a sanyaye ya ce.

"Har kin fito?"

"Eh"

Ta ce cikin dishewar murya, ya shiga ciro kayan da ya siyo a leda, doguwar jallabiya bak'a, sai riga da wando na Pakistan brown, pant dozin, sai sink'in always guda goma, ba tare da ya kuma kallonta ba ya ce.

"Ga wannan kayan ki zab'a a ciki ki sanya sai kuma wannan shi zaki saka ya tare abun"

Ya bud'e always d'aya ya d'auki pant guda d'aya.

"Ki kalla yadda zaki rik'a sanya always akan pant dinki"

Nan ya gwada mata yadda ake manna always jikin pant, ya mik'a mata.

"ga shi nan ki shirya"

Sai ya barta a nan ya shiga toilet dinsa ya shiga ya gyarawa, sannan ya fesa turaren ba yi, ya dauki pant d'in data cire yasa a bak'ar leda, sannan ya kwaso mata kayanta ya fito dasu falo, wani babban leda ya zuba kayan sannan ya fito waje ya yarda pant d'in a bola kana ya koma bayi ya wanke hannunsa ya fito falo.

Ya sameta zaune tana wasa da yatsun hannunta, bak'ar jallabiya ta sanya ta yane kanta da gyalensa ta yi kyau sosai, wuri ya samu ya zauna yana kallonta fuskarta ta mau ba alamar wasa ya fara mata bayani kamar haka.

"Husna ina so ki bani hankalinki nan da kyau"

Nan ta tattara natsuwarta gaba d'aya tana saurarensa, kanta yana a sunkuye.

"Ina so ki sani wannan jini ba mutuwa za ki yi ba na balaga ce, shi ake kira da jinin Haila wanda mace take soma yinsa lokacin data kai balaga, a turance kuma ana kiransa da Menstruation, ko ace period wato jini ne mace da take yinsa duk karshen wata wasu matan kuma ko fiye da haka, sannan mace takan d'auki kawanaki tana yi kamar kwana uku, hud'u, ko fiye da haka. A musulunce dai inya zarce kwana sha biyar to ya fita daga jinin haila ya koma na ciwo, daga nan sai mace ta yi wanka tsarki ta cigaba da ibada ta nima magani. Dan haka yanzu Sallah, Azumi, da sauran ibadu sun wajaba akanki, an bud'e miki kundin littafinki na rubuta lada da zunubi. Sannan akwai sauye-sauye da zaki gani na halittarki kamar fitar gashi a al'aurenki da hammata,

canzawar murya, breast dinki za suyi girma, feelings akan namiji da sauransu wanda a hankali zaki gane su. Sannan ina so ki sani mistake kad'an sai iya sanyawa kiyi ciki dan mahaifarki ta fara aiki.  Sannan ina gargadinki baki ba wasa da maza ko hannu karki bari namiji ya tab'a miki, Husna dole ki aje wauta da wasa dan kin girma yanzu"

Nan dai ya yi ta koro mata bayani. Jikinta ne ya yi mugun sanyi har kwalla na fita a idonta, ji take kamar ba ita ba dan ta tsinci kanta a sabon ya nayi na rayuwa, ya cigaba da cewa.

"yanzu daga yau da kika fara wannan jinin, ina so ki kasance kina k'irga kwanakin har ranar da jini ya tsaya miki, sai ki zo ki yi wankan tsarki, kuma kin ga yanzu ba zaki yi sallah ba har sai ya tsaya"

Da sauri ta dago kai tana kallonsu da rinannun idonta da suka kode, saboda kuka, Sadiq ya yi murmushi.

"Kwarai ba zaki yi sallah ba sai ya tsaya ko baki san haka ba?"

Husna ta gyad'a masa kai alamar eh bata sani ba.

"Ai dama nasan da wuya ki sani tunda ba islamiya kike zuwa na, na tabbata da kina zuwa da ba zan sha wuyar fahimtar dake ya jinin haila yake ba da hukuncinsa, a gaskiya zan sanya ki makarantar islamiya dan ki fita daga duhun kai, iyayenki sun kasa sauke nauyin da Allah ya basu wannan abu ya jima yana da muna, ina tausayin rayuwar ki Husna wannan dalilin yasa har yanzu na kasa barin gidan nan na fi yarda dana zauna a kano fiye da kaduna cikin ahalina"

Ya kare maganar yana jan k'aramin tsaki, Husna ta cigaba da kuka mara sauti tana tausayin kanta.

"Husna ba kuka zaki yi ba girma ne ya kama ki, kuma tabbas sai kin je islamiya dan naga ko sallah baki damu da ki yi ba kuma hakan babbar illace ga rayuwarki, dan na san ko abin da ake fad'a a cikin Sallah ma baki sani ba"

Nan dai ya yi ta mata nasiha, daga k'arshe ya koma lallashinta har ta yi shuru, ya bata kayanta gaba d'aya har da wanda ya siyo mata ya ce.

"Tashi ki tafi gida kafin animeki"

Husna ta mike tana yi masa godiya kanta a sunkuye, ta kasa hada ido da shi saboda a yau tana jin wani sabon kunyarsa yana ratsata. Sadiq ya bita da murmushi harta fice.

Tana shiga gida d'akinta ta wuce ta shiga ba yi, pant d'in da ta cire d'azun ta d'auka ta sanya aleda taje ta yar a bola, ta dawo ta wanke bayin kana ta fito ta gyara d'akinta ta samu guru ta zauna ta shiga tunanin yadda rayuwarta ta saura a yau kawai, kuka ta yi mai isar ta kana ta

kwanta barci ya yi gaba da ita.

***
Yau take cike kwana hud'u da fara jinin Al'ada, tunda ta tashi bata ga alamar jini ba ta kara jinkirtawa na wani lokaci still ba jini, agogo ta duba taga k'arfe 3 na rana tasan Uncle bai dawo aiki ba, fita k'ofar gida ta yi ta zauna kusa da Baba a kan benci tana jiran dawowar Uncle.

Ba shi ya dawo ba sai karfe Hudu da rabi na yamma, Sadiq yana daga nesa ya hango sai ya fara murmushi ya san zaman da ta yi shi take jira ya dawo, sai da ta bari ya shiga ya yi parking kafin ta bi bayansa, a lokacin Baba ya shiga gida dan ya zaga bayi. Husna tana shiga falo ta samu guri ta zauna tare da gaishe shi, Sadiq ya amsa yana kallonta.

"My Husna ya dai?"

Husna ta yi murmushi tare da sinne kai k'asa.

"Uhum dama abin ne ya dai na zuba tun safiyar yau dana ta shi daga barci ban gani ba"

"Masha Allah yau kwana nawa kenan?"

Husna ta daga kai sama tana cizon yatsarta kamar mai yin tunani.

"Ummm kwana hud'u yau"

"Yauwa kin ga kenan kwana uku ne kwanakin hailarki, yau kwana na hud'u shi ne zaki yi wankar tsarki, sannan zaki rama sallar asuba, azahar, la'asar, tunda baki wanka da wuri ba kuma sallolin sun hau kanki tunda jinin ya d'auke tun kafin su. Daga yanzu duk lokacin da kika gama kina tashi da safe ki yi wankar tsarki kinga sai ki rama sallah asubahi ita kad'ai sai ki cigaba da sauran sallah in lokacinsu ya kama. Sannan ki sani lokutan suna chanzawa wataran zai iya daukewa da rana ko safe ko yamma ko dare kan a kwanta, dan haka sai ki zama mai lura da kyau"

Ta yad'a masa kai alamar ta fahimta, Sadiq ya cigaba da cewa.

"Sannan pantis d'inki ki samu ruwan zafi ki jik'a su sai ki sanya musu omo da gishiri da dettol su yi kamar minti talatin sannan ki wanke su ki shanya a rana suna bushewa, sai ki adana su ki cigaba da amfani da su"

Husna ta d'ago kanta suka had'a ido sai ta sunne kai tana dariya k'asa-k'asa, Sadiq ya dauee fuska.

"Dariyan me kike yi kuma ina miki magana?"

Husna ta sosa keya ta ce cikin muryar shagwaba.

"Uncle ni fa inna cire pant d'in zubar dasu nake yi had'e da always d'in, na d'auka an gama aiki dasu duka"

Dariya ce ta kubuce masa ya shiga kyakyatawa tare da samun wuri ya zauna, dama tun dazu a tsaye yake mata bayani, sai da ya yi mai isarsa kana ya ce.

"My Husna sarkin shirme, ko da yake 'yar fari ce ke ban ganin laifinki"

Husna ta yamutse fuska kamar zata fashe da kuka

"Ni fa Allah na d'auka zubarwa ake yi"

"A'a ba zubarwa ake yi ba, cire always d'in zaki yi sai ki ajiye pant d'in ko ki wanke shi a take in kin cire, sai ki shanya ba sai kin gama tarawa ba kice zaki wanke"

Sai ta mik'e dasauri zata tafi.

"A'a ina zaki kuma? Ai bamu gama magana ba"

"Uncle zan je in ciresu a bola ne tunda ba'a kwashe shararba sai na wanke"

"A'a ki barsu kawai zan siya miki wasu sabbi"

Sai ta dawo ta zauna, nan ya fara mata bayanin yadda ake wankan tsarki kama daga niyya har zuwa karshe, yana yi tana gyad'a kai alamar gamsuwa, ta shi ya yi ya shiga toilet d'insa ya had'a mata ruwa a bokiti kana ya ce ta shiga ta yi.

Minti kusan ashirin ta d'auka tana wanka kafin ta fito ta mai da kayan data cire ta fito falon.

"Ki je gida ki chanza kaya sannan duk ki rama sallar dana gaya miki, gobe in Allah ya kaimu zan siya miki pantis d'in, sannan ki zama cikin shiri inna dawo aiki da yamma zan kai ki makarantar Ahmad Islamic Academy in yi miki register islamiya ki fara zuwa"

Cewar Sadiq yana kallonta, Husna cike da murna ta yi masa godiya ta wuce gida.

*
Washe gari da misalin k'arfe hudu na yamma Sadiq ya kai Husna Ahmad Islamic Academy, ya yi mata register ya biya komai, da yake suna da uniform nan suka gwadata aka bata dai-dai nata har kala biyu, da littafai da komai daya shafi karatunta, yaso ta fara daga aji d'aya amma Malaman suka ce ta yi girma sai dai zasu sanya ta a aji biyu, lokacin zuwa daga ranar asabar zuwa laraba da k'arfe hud'u na yamma zuwa k'arfe shiga a tashi. Nan ya musu sallama suka

koma gida.

Wannan shi ne mafarin komawar Husna makarantar Islamiya, ta maida hankali sosai dan ita ma tana son ta yi karatu sosai. Haka b'angaren boko sun koma hutu ta cigaba da ss1 science class, nan ma ta mai da hankali saboda kullun Uncle Sadiq d'inta yana mata fad'a da nasiha akan ta maida hankali domin karatun da take yi shi ne kadai gatanta.

_Sadiq ya zamewa Husna Uba da Uwa😰_
[10/26, 7:38 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 31 ~ 32_*

*Bayan Mako guda*

Da fara zuwan Husna makarantar islamiya. Tun misalin ƙarfe biyar na yamma Dady yake zaune a farfagiyar gidan bisa kujera yana shan iska tare da karanta jarida, kasantuwar ranar ya kama weekend, ya yi zurfi a cikin karatunsa har garin ya soma duhu alaman sallar magriba ya kawo jiki. Sallamar Husna yaji kamar daga sama, da sauri ya jenye jaridar yana duban inda ya jiyo muryanta, da murmushi a fuskarta ta ƙaraso wurin Dady.

"Dady sannu da hutawa"

Dady ya bita da kallon mamaki, sanye take cikin uniform dƊin islamiya, bai amsa mata ba sai ya je fa mata tambaya.

"Ke yaushe kika fara zuwa islamiya? kuma waye ya sanya ki?"

Husna taji gabanta ya fad'i, ta manta shaf Dady bai san da zancen zuwanta ismaliyya ba, ko Momy ma ganinta ta yi da uniform ta fita bata ce mata komai ba, tunda yanzu ko ta gaisheta bata amsawa. Ta dawo daga gajeran tunani ta sosai kai tana sunne kai ƙasa, nan take dubara ta fad'o mata cikin inda-inda ta ce.

"Ummm Baba mai gadi ne ya sani a islamiyar Ahmad academy"

Mamaki ya kuma bayyana a fuskar Dady.

"Ok, shiga ciki ina zuwa"

Jikinta a sanyaye ta shiga ciki tana tunanin yadda Dady zai kwashe da Baba? Addu'a ta shiga yi Allah yasa Baba ya ce shi ne ya sata.

Tana wucewa Dady yaji kansa ya yi masa nauyi yaji ciwon kai yana ratsa kwanyarsa, da k'arfi ya rik'e kan da hannu biyu, bakinsa na furta.

_"Innalillahi wa inna ilaihir raji'un, la'ilaha illa anta subhanaka innee kuntu minaz zalumin, Allahumma laa sahla illa maa ja'allatahu sahla wa anta taj Alhul husza izaa shi'ita sahlan, astagfirullah wa a dubu ilaiy "_

Ya cigaba da jero duk  addu'an da ya zo bakinsa, a hankali yaji ciwon kan na raguwa yana jin sassauci, ya kai kusan minti goma kafin yaji ciwon kan kamar an ɗauke masa ya daina ciwo, ya sauke wani nannauyar ajiyar zuciya, ya ji jikinsa kamar an cire masa abu mai nauyi, tunanin abin da ya faru ya shiga yi, cikin k'ank'anin lokaci ya tuna, da sauri ya d'aga murya ya kira Baba mai gadi, cikin hanzari da sassarfa ya k'araso tare da risinawa.

"Alhaji ga ni"

"Husna ta ce kaine ka sanya ta a islamiya, hakane?"

Baba mai gadi yaji zufa ya fara tsastsafo masa, hantar cikinsa ya kaɗa, sai da ya had'iye miyau da k'arfi kana ya tattaro natsuwarsa ya ce cike da tsoro.

"Eh Alhaji, ka yi haƙuri na yi laifi, ba komai yasa na sanya ta ba, gani na yi tana da raunin sani game da addini shiyasa, kuma da ina koya mata to yanzu gani na yi ta girma shi ne na ce gwara islamiya za tafi mai da hankali, Alhaji ka min aikin gafara haka ba zai sake faruwa ba"

Nan yaja bakinsa ya yi shuru yana sauraren hukuncin da Dady zai yanke masa. Dady ya sauke ajiyar zuciya, ya ce cike da matsananciyar damuwa.

"Nawa ka kashe?"

"Alhaji ba zan iya tuna nawa na kashe ba domin har uniform su suka bata dan ina ga zai yi dubu goma"

Nan take Dady ya sanya hannu a aljihunsa ya ciro rafar kud'i 'yan dubu-dubu, ya k'irga dubu goma ya mik'a masa, jikin Baba na rawa ya amsa domin duk tunaninsa yau ya bar aiki a gidan kenan, Dady zai kore shi, amma da mamaki sai yaji ya ce.

"Baba nagode da wannan tunani da ka yi daka sanya ta a makaranta, ni ya kamata na yi mata haka amma na kasa, kuma duk banyi wannan tunanin ba, Allah ya saka da alkhairi, sai dai duk lokacin da wani abu ya taso to ka fara sanar min kafin ka aikata shi, zaka iya tafiya"

Cike da farin ciki Baba ya yiwa Alhaji godiya kana ya tafi yana jinjina maganarsa, a farkon saninsa da Alhaji haka yake da kirki da fahimtar mutum, amma daga bisani ya zama mafad'aci mara fara'a, ya shiga tambayar kansa.

'Anya Hajiya bata yi wani mugun abu a kansa ba kuwa?'

Nan dai ya k'arasa bakin gate yana ta zancen zuci.

Haka nan Dady yaji zuciyarsa na yi masa zafi akan rashin bawa Husna kulawarsa, tunani ya shiga yi yana tambayar kansa.

'Yaushe na sauya haka? Ni da nafi kowa k'aunar Husna ta yi karatu amma yanzu na zama mai wofantar da ita, wai ina tunani na yaje ne?'

Hankalinsa ya kuma tashi, wani hawaye mai zafi da rad'ad'i ya fito a idonsa, tunawa da ya yi da Zainab ne yaji gabansa ya yi mummunan fad'uwa, dasauri ya tashi ya shiga cikin falon.

Ko da ya shiga ba kowa a falon d'akin Husna ya shiga ya sameta ta cire uniform ta sanya wani doguwar riga na shadda, tana karanta k'arin da aka yi musu na littafin fiqhu, ta d'ago da sauri dan ganin wanda ya shigo, ganin Dady ne yasa ta washe baki.

"Dady"

Ta ce, sai ya amsa mata fuskarsa cike da fara'a, ya shiga duba d'akin yadda duk komai ya tsofe ba wani canji tun tana k'arama, damuwarsa ce ya k'aru ya shiga tambayar kansa.

'Ina Husna ta samu kayan da take sawa? waye yake siya mata littafai na makaranta? waye yake kula da karatunta?'

Dady ganin yadda k'irjinta suka cicciko da dukiyar fulani, yaji wani mummunar faɗuwan gaba.

'Husna ta girma, wato kenan ta fara jinin al'ada, innalillahi wa inna ilaihir raji'un. Waye ya sanyata akan hanya na sanin menene wannan jinin? ya zata tsarkake jikinta? yaya take gabatar da ibadunta? shin ya take kula da lafiyarta?'

Wannan tambayoyin fal suke a zuciyarsa ya rasa ta ina zai zamu amsar su.

'Wai wani irin sakaci na yi da na wofantar da ɗiyata mai daraja haka? tunda likita ya ce Husna ta samu matsalar  kwakwalwa, nasan ba wani kulawa zata samu a gun Habeeba ba, to wai ko ta warke ne? tun da gashi yadda take a yanzu babu wata alama na hauka'

Husna dai tana ta kallonsa, ya zame mata sabon mutum kamar ba shi ba, dan ta san rabonsa da ya shigo d'akinta tun tana k'arama daya dawo daga wani tafiya, tabbas ba zata manta da wannan ranar ba, mik'ewa ta yi ta matsa kusa da shi ta kama hannunsa, wani irin ajiyar zuciya ya saki yana kallonta cike da tausayawa. Husna ta ce cikin sanyin murya.

"Dady in na yi maka laifi ka yafe min, ba zan k'ara zuwa makarantar ba tunda baka so?"

Ta k'arasa maganar tana matsar kwalla, cikin zafin nama ya jawota jikinsa ya rungumeta da k'arfi kamar zai mai da ta cikinsa yana fad'ar.

"A'a Husna ni ne zan nima gafara a gurinki, ƴata ki yafe min, hak'ik'a a baya na tafka babban kuskure wanda ban san ta yaya na aikata miki haka ba"

Husna ta ƙara fashewa da sabon kuka, kiran sallar magrib ne ya dawo dasu cikin natsuwarsu, Dady ya sake ta ya zaunar da ita gefen gado.

"Ki cigaba da mai da hankalinki ki yi karatu sosai, ba zaki daina zuwa ba nima na yi kuskuren rashin sanya ki a makarantar, ki yi haƙuri kin ji. Babanki yana sonki sosai"

Ya k'arasa maganar yana murmushi, ita ma murmushin ta yi.

"Ni Dady baka min komai ba, kullun Uncle yana ce min in rik'a yi maka addu'a, kuma Dady ina yi, dan Allah kar ka ƙara nesa dani ka ji"

Dady ya katse mata magana da jefa mata tambaya.

"Waye Uncle?"

Husna ta dafe bakinta da sauri, fargaba ne ya taso mata kan sub'ul da bakan da ta yi, murmushi Dady ya yi mata saboda ya lura da yadda yana yin ta ya sauya, sai ya tashi ba tare da ya nuna mata damuwar sa ba ya ce.

"Ki tashi ki yi sallah, ni zan tafi masallaci sai na dawo"

Cike da farinciki ta ta shi.

"Ka dawo lafiya Dadyna"

***
Bayan Dady sun idar da Sallah zama ya yi a masallaci dan jiran sallar isha'i, abin da ya jima bai yi ba kenan, ya shiga yin lazumi, a haka ya faɗa duniyar tunani mai zurfi.

'Waye wannan Uncle da Husna take fad'a? anya Allah ba zai kama ni da laifin sakaci da tarbiyyarki ba Husna? lallai ya zama dole in bibiyi lamuranki, sannan in tashi sosai wajen niman lafiyarta ki. Allah nagode maka daka farkar dani daga dogon barcin dana yi, Allah ka taimake ni bisa komai, ka karemu daga duk kan shrrin shaiɗan, mutum da aljan

'[10/27, 5:37 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 33 ~ 34_*

Cikin dare Dady ya tashi ya zauna yana tunanin rayuwa, ya tashi ya je ya d'auro alwala ya fara gabatar da sallar nafila, sai da ya jero raka'a shida kana ya zauna, ya yi istigfari da lazumi had'e da salatin fiyayyen halitta s.a.w, ya d'auki kusan awa guda kana ya tashi ya koma saman gado, kallon Momy ya yi tana ta faman sharb'an barci abin ta, ya girgiza kai ya koma ya kwanta kamar mai barci, don idonsa k'amas babu alamar barci, ya lumshe su ya fad'a duniyar tunani, abin mamaki sai ya fara tuno farkon dawowar sa daga kasar Manaco da duk abin da ya faru, akan yadda ya sauya lokaci guda tunda ya shak'i turaren wuta da Momy ta sanya a falon, ga yafda Momy ta ke galmazawa Husna akan idonsa baya iya tabuka komai, kuma shima ya daura mata da na shi hukuncin, ya tuna da irin hantarar da yake yi mata, gaba daya duk abin suka dawo masa kamar an sanya masa cassette yana kallo, haka ya dinga tuna komai kamar a film, hawaye masu zafi suke sauka a kuncinsa, damuwa ne fal zuciyarsa cike da tambayar kansa.

'Menene ya same ni? anya ban samu gushewar kwakwalwa ba?'

Addu'a ya shiga jerowa da hamdala ga Allah da ya warware masa komai cikin sauk'i ya dawo cikin hankalinsa, ya d'aura aniyar bin komai a hankali har sai ya fahimci komai da abubuwan da suke tafiya a gidan, sai ya gyara kwanciyarsa ya kwanta, bai jima ba barci ya yi awon gaba dashi.

*******

*Washe gari*

Sadiq ne ya fito daga gidansa ya k'araso kusa da Baba da yake zaune a kan benci a waje yana saurаron radio, wuri ya samu ya zauna suka gaisa, Baba ya ce.

"Sadiq kamar kasan ina nemanka fa"

"Allah ko Baba, to gani, da fatan dai lafiya?"

"Lafiya lau, kai ma kasan in na ce ina nemanka to baya wuce zancen Husna, in gaya maka jiya Alhaji yana zaune a cikin gida yana shan iska sai ga Husna ta dawo daga kamaranta ya ganta, hmm ai in gaya maka zuciyata ta tsinke dana ji muryar Alhaji yana kira na"

Nan ya kwashe duk yadda suka yi da Alhaji ya gayawa Sadiq, wani farin ciki ne ya lullub'e shi yana fad'in.

"Alhamdulillah! na yi farin ciki da jin wannan labari, ban yi zaton zamu kwashe da shi da sauki haka ba, kuma Husna ta yi hankali da ba ta ce nine na sata ba"

"Kwarai wallahi ta yi tunani akai"

Cewar Baba yana kiciniyar ciro kud'in daga aljihunsa.

"Kaga kud'in ma ban aje su da nisa ba, dan nasan zamu had'u, da baka fito ba, da har gida zaka ganni na mako maka sallama"

Ya k'arasa maganar yana yar dariya, shima Sadiq dariya ya yi.

"Haba Baba ai ba sai ka zo ba, gani ma Allah ya jeho maka ni kamar daga sama, dan haka ka rik'e wannan kud'in halak malak na bar baka su"

Bana ya kara washe baki yana dariya.

"Anya Sadiq ayi haka? naga kud'in da yawa fa, ko dubu biyu ka bani ya wadatar dani sai ka rik'e sauran, nagode"

Murmushi Sadiq ya yi wanda daka gani kasan yana cike da farin ciki.

"Ai Baba ka wuce haka a guna tunda kaima kana iya k'ok'arinka wajen taimakawa Husna, dan haka ni da kai duk munyi tarayya acikin hidimarta"

Godiya Baba ya yi masa sosai yana jin jina karamci irin na Sadiq, a cikin ransa ya ce.

'Ashe ana samun yayan masu kud'i haka wanda basa kyamar talaka, gaba d'aya rayuwar Sadiq taa burgeni ga ilimi duk ya had'a boko dana Arabi, ga tausayi da girmama na gaba da shi, ga kuma natsuwa da karamci, ga kyau da kud'i duk ya had'a, lallai iyayensa sun kasance mutanan kirki, madalla da zuri'a irin tasu, Allah ka k'ara had'amu da mutanan kwarai'

Sai ya ji Sadiq na amsa masa da

"Amin Baba"

Da mamaki Baba ya kalle shi ashe zancen zuci ne ya fito fili, dariya ya yi masa suka cigaba da hira.

Husna sun taso makaranta, haka ta gangaro gida, tana tafiya  cike da natsuwa, ta samu Sadiq a bakin gate nan ta tsaya suka gaisa, daga nan hira ta barke tsakaninsu na zancen karatunta, yana tambayarta wasu daga cikin littafanta tana ba shi amsa, wanda bata sani ba ya gaya mata tare da yi mata bayani.

Tun daga nesa Dady ya hango su yana Allah-Allah ya k'araso yaga da waye take magana, basu ga zuwansa ba saboda sunyi nisa cikin hirarsu, mai gadi ne ya hango shi kafin ya k'araso ya shiga ciki da sauri ya bud'e masa gate, da sauri Dady ya shiga da gudu ya yi parking, Husna taji gabanta ya yi mummunar fad'uwa, duk tunaninta Dady yana cikin gida shiyasa ta sakankance

suna ta hira, yau ce rana ta farko daya fara ganinsu tare da Sadiq, Dady ya fito wajen fuskarsa kamar anyi masa mutuwa a murtuke, shi dai Sadiq ko d'ar a zuciyarsa na fargaba bai ji ba sai ma wani k'arfin guwa da yaji, cikin natsuwa ya risina ya ce.

"Dady ina yini"

Dady ya amsa masa dak'ile, Husna tana ganin haka hantar cikinta ya kad'a, ta bud'e baki zata yi magana kenan, ya fara magana cikin kakkausar murya.

"Me kikeyi a nan? makarantar kenan? ko kuwa abin da aka koya miki kenan in kin dawo ki tsaya bakin gate kina surutu?"

Husna ta sunne kai kasa ta kasa furta komai, banda hawaye da suka cika mata ido kamar zasu subo, tsawa ya daka mata.

"Maza ki wuce ciki kafin in b'allaki"

Jiki na b'ari ta shiga cikin gida. Mugun kallo ya dannawa Sadiq kana ya nuna sa da yatsa.

"Karna sake ganinka a k'ofar gidan nan"

Bai sake furta komai ba ya wuce ciki. Sadiq ya yi murmushi ya girgiza kai, farin ciki ne fal cikinsa domin wannan action d'in da Dady ya nuna, ya tabbata masa da ya dawo cikin hayyacinsa, Baba ne ya matso kusa da shi yana ba shi baki.

"Kayi hakuri nasan rashin sani ne yasa shi yi maka haka, dan da ashe ya san ko kai waye ga Husna da ba zai yi maka haka ba"

"Karka damu Baba lokaci zai bayyana haka"

Haka ya tashi suki yi sallama da Baba ya shige gida hankalinsa kwance.

Dady yana kutsa kai cikin falo ya shiga kwalawa Husna kira, tun daga d'aki ta b'arke da kuka jikinta na rawa domin yau ta sadak'ar zata sha d'an banzan dukan data dad'e bata sha ba, haka ta fito kamar kwai ya fashe mata a ciki, Dady ji ya yi duk tausayinta ya kamashi amma sai ya danne ya fara mata fad'a ta in da yake shiga ba tanan yake fita ba, cikin sauri Momy ta fito falon dan ganin me ke faruwa.

"Alhaji lafiya? me ya faru ne?"

Cewar Momy. Dady ya ce cikin fada.

"Ta dawo daga makaranta mai makon ta shiga gida sai ta tsaya a waje tana magana da wani

yaro"

Momy taja tsaki.

"Dama a kan wannan sha-sha-shar kake tada jijiyoyin wuya, ai in dai wannan ce zata ai kata abin da yafi haka, makarantar munafunci take zuwa ai, wacce take da hauka taya zata fahimci karatu"

Mamaki ne fal zuciyan Dady yana kallon Momy, amma sai ya dake bai nuna ba, ta cigaba da cewa.

"Ai Kaine baka sani ba, haukan nata iskanci ya sanya mata na bin maza, yanzu haka in ka shure k'afa ka fita da safe itama fita take yi sai lokacin da taga dama take dawowa"

Dady yaji Zuciyarsa ta yi masa nauyi, saboda jin zafin furucin Momy akan Husna, sai ya fara kai kawo bugun zuciyarsa ya fara bugawa da sauri da sauri, tuni idanun sa suka yi ja kamar jan karwashi, tashin hankali ne ya ziyarceshi lokacin da Momy take aibata masa 'ya tare da karairayi da mugun sharri da takewa Husnaht, mummunar tsanar Momy yaji a ransa, ya dafe kansa ya samu guri ya zauna ba tare da ya furta komai, ba saboda azabar da zuciyarsa yake masa a wannan lokacin.

Ai Momy sai ta samu damar k'ara zugashi dan a tunaninta tuggun da ta had'awa Husna ya samu gurbi a zuciyarbDady, dan tas an asirin da ta yi masa yana nan a jikinsa, kukan Husna ya k'aru tana fad'in.

"Wallahi Dady ni ba mahaukaciya ba ce da hankali na, sannan ni bana yawo ban bin maza, Momy sharri take min, wallahi ban aikata komai ba, Dady ka yarda dani"

Ta k'arasa maganar tana zubda hawaye mai rad'ad'i, nan take Husna taji ta k'ara tsanar Momy, duk tunanin ta k'iyayyar da Momy ke yi mata bai kai haka ba, har yanzu Dady bai iya cewa komai ba, Momy ce ta yi tsarab ta ce.

"Rufe min baki mahaukaciya, ni zaki gayawa ina miki sharri, yaushe kika fara girma da zaki min rashin kunya, lallai na yarda bin maza da kika fara idonki ya bud'e"

Dady ya runshe idonsa  yana jin wani yaji mai rad'ad'i a ciki, da kyar ya iya had'iye miyan ya furta.

"Hajiya ya isa haka, rabu da ita zan d'auki mataki"

Yayi hakan ne domin kar ya nunawa Momy yana cikin hayyacinsa don yaji dad'in gano gaskiya, tunda ya furta haka ya mik'e cike da sanyin jiki ya wuce falonsa. Momy ta yi dariyar mugunta.

"Dad'an kika gani, ba kin ce ke mara kunya ba, wallahi sai na zama ajalinki shinanniya kawai"

Ai bata k'arasa rufe baki ba Husna ta yi super ta shak'o wuyanta, idonta kamar zasu yo waje cikin kakkausar muyar mai firgitarwa Husna ta ce.

"Ko ki zama ajalina ko ni na zama ajakinki, sai na sabautaki na nakasaki tunda kike zalunta ta, wallahil Azeem sai kin wulakanta a rayuwarki, kuma sai na zama silar ajalin yaronki, Azzaluma mashirkiya, duk abin da kike yi muna biye dake saura k'iris mu fallasaki"

Momy k'ara ta saki mai k'arfi amma ina babu mai jin ta, haka take ta gurnani tana niman kwacewa amma ina Husna tak'i sakinta, sai da ta fara kakari shirin mutuwa kana ta saketa taja baya, Husna d'akinta ta wuce ba tare da ta juyowa ba, da gudu Momy ta fad'a d'akinta tare da sanya key tana mai da numfashi da kyar, idon nan nata kamar zasu fad'o kasa saboda tsoro.

Shi ko Dady bai san abin da ke faruwa ba saboda ya lula duniyar tunani, tsanar Momy ne ke kai komo a zuciyarsa, duk maganganun ta ba wanda ya yi tasiri a zuciyarsa face k'aryata ta da yake yi kan sharrin da ta d'aurawa Husna, kiran sallar Magrib ne ya dawo da shi daga duniyar tunanin da ya lula, cikin azama ya shiga bayi ya d'auro alwala kana ya fita zuwa masallaci.

A b'angaren Husna kuwa, kwanciya ta yi kamar mai barci sai da ta yi minti goma kana ta tashi zaune tana k'ok'arin tuna abin da ya faru, jikinta duk ya mata nauyi, ga ciwon kai da take ji, tashi ta yi da kyar ta fad'a bayi ta d'auro alwala kana ta fito ta gabatar da sallah.

Momy kuwa ta kasa fitowa ko falo, Dady bai dawo ba sai da suka yi sallar Isha'i, ya dawo rik'e da leda a hannunsa, kafin ya shigo sai da ya biya wani shop na ostrich dake bakin titi ya siyo meat pie da burger tare da yoghurt, d'akin Husna ya ya fara isa ya tura ya ganta zaune kan sallaya tana karatun Al'Qurni, farin ciki ne ya ziyarce shi sai ya yi mata sallama ta amsa a nutse tare da dago kai, leda ya mik'a mata ta amaa tare da yi masa godiya, ya ce.

"Ki ci yanzu sannan in zaki kwanta ki rufe d'aki ki kashe fitila, sai da safe"

Cikin ladabi ta ce.

"To Dady Allah ya samu alkhairi"

"Ameen"

Ya wuce sashensa bai bi ta kan Momy ba, yana shiga ya sanya key a kofarsa, wuri ya samu ya zauna sai da ya ci meat pie da yoghurt d'in kafin ya hau kan system ya fara aikin sa. Momy kuwa ko da taji Dady shuru bata damu ba  sai ma gado data kwanta tana tunanin ta ina zata bullowa Husna, domin tana kara bata tsorata.

Husna ta kammala komai ta yi shirin barci, ta sanya doguwar riga mai guntun hannu tsayinta ya kawo mata gwiwa, ta sanya hula tare da kakkab'e shinfid'arta ta gyara, ji ta yi anyi nocking k'ofarta, cikin sauri ta isa ta bud'e duk tunanin ta ko Dady ne, sai taga Yaya Nura ne, cikin d'aure fuska ta ce.

"Malam lafiya?"

Murmushi ya yi mata wanda bai kai zuciya ba.

"Kalau"

Ya ce yana binta da kallo yana had'iye yawu tare da kafawa kirjinta ido, ganin ya ta sata a gaba yana kallonta sai ta ja tsaki zata rufe k'ofa, dakatar da ita ya yi.

"Husna na dawo a gajiye ne, dan Allah ki dafa min pipton da kayan kamshi ki kawo min d'aki, yunwa nake ji, kuma na duba abincin da Momy ta dafa ba zan iya ci ba"

Husna taja tsaki ta ja.

"Ai dole ka rage min murya, in kuma rashin mutumcinka ya tashi ka karta min baka nuna ka sanni"

"My sis ki yi hakuri duk wasa ne ai, ki je ki had'a min ina jiran ki"

To kawai ta ce masa ta wuce kitchen fuska daure, Nura ya bita da kallo yana lashe lebensa na kasa, tare da kashe ido daya yana wani shu'umin dariya ya juya zuwa dakinsa.
[10/28, 6:31 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 35 ~ 36_*

Bayan ta gama dafawa d'akinta ta koma ta sanya hijab kana ta d'auki jug d'in data zuba Lipton din ta wuce d'akin da sauri dan ta fara jin barci.

Tura k'ofar ta yi ta shiga da sallama, ganinsa ta yi daga shi sai gajeren wando da singilet, kauda kai ta yi ta ajiye akan karamin wani table.

"Gashi nan sai da safe"

"Tsaya na gama sha mana Husna"

Ta isa wurin k'ofa ta ce.

"Banda lokacin tsayawa"

"Kai my sis, to bari na baki wani abu dana siya miki"

Sai ya mik'e ya d'auko wani akwatin sarkan d'an kunne ya mik'a mata, ta kawo hannu zata amsa sai ya tsafke hannun tare da jawota da k'arfi ta fad'a k'irjinsa, zaro ido ta yi alamar tsoro, cikin masifa ta ce.

"Meye haka yaya Nura?"

Ya k'ank'ameta ya fara shafa mata baya, kiciniyar kwacewa take yi amma ya rik'e ta da duk iya k'arfinsa, sai ya jefata kan gadonsa ya fad'a kanta, kuka ta soma tana fad'ar.

"Me zaka min? wallahi ka sake ni, na shiga uku na, Dady ka zo ka ceceni karya kashe ni"

Bakinta ya toshe da hannu d'aya yana fad'in.

"Tun kina k'arama nake hak'onki, ina ta jiran rana irin ta yau da zan mallaki jikinki, shiyasa nake sassautawa da cin zalinki, saboda in jaki a jikina yadda zaki yarda dani, dan haka yau zan d'auke abin da za ki yiwa wani d'a namiji tak'ama da shi nan gaba"

Kuka take yi mai tsanani tana son cire hannunsa dake kan bakinta, ta samu sa'ar ganna masa cizo a yatsarsa,  da sauri ya cire hannunsa yana yarfewa.

"Ni kika ciza wallahi yau saina rama ta in da ba k ida k'arfin ramawa"

Ya cire mata hijab, tare da hular kanta, damben kwace kanta ta soma yi, ta mamaye shi ta kuma ganna masa cizo a damtsensa, wani k'aramin k'ara ya saki tare da rik'e wurin, wani k'arfi taji ya zo mata ta hankad'a shi ya fad'i ta baya ya bige kansa, da sauri ta mik'e tana k'ok'arin isa k'ofa ta fita, k'afarta ya kama ya jawota da k'arfi ta fad'i a k'asa ta bige kanta da wani table da yake gefe, wani wawan k'ara ta saki mai k'arfi har sau biyu.

B'angaren Sadiq kuwa, yana kwance bisa gadonsa ji ya yi duniyan ya yi masa k'unci, gaba d'aya yaji hankalinsa a tashe, mik'ewa ya yi daga kwancen da yake ya fito falo, kai komo yake yi ya rasa meke masa dad'i, Husna ce ta fad'o masa arai sai yaji gabansa ya fad'i, Addu'a yake jerowa na niman tsari daga duk abin k'i, sai ya zauna ya tashi ya rasa sukuni, har fita farfajiyan gidansa ya yi yana k'ok'arin ya fita waje, sai ya tuna yanzu wurin sha d'ayan dare ba kowa a waje, yana k'ok'arin shiga falonsa ne yaji wannan k'arar da Husna ta yi har sau biyu, gabansa ne ya cigaba da fad'uwa yana sauraren ko zai kuma jin k'arar da sanin ta ina ya fito, minti biyar ya k'ara yaji shuru sai ya wuce d'akinsa ya koma ya kwanta cike da damuwa cunkushe a zuciyarsa, yana karanto Addu'o'i har barci ya yi gaba da shi.

Dady yana aikinsa bisa system ganin lokaci ya ja ya rufe, ya yi shirin barci yana k'ok'arin kwantawa ne ya jiyo ihun Husna har sau biyu, cike da tashin hankali ya fito falon, d'akinta ya shiga yaga wayam bata ciki, dube-dube ya fara yi a falo, Momy kuwa tana jin wannan k'arar sai

ta k'ara lafewa akan gado cike da tsoro dan ba zata iya fitowa ba.

Dady gunjin kukanta yake ji daga nesa, haka ya soma bin ta in da yake jin kukan, da yake d'akin Nura yana da ga ciki sosai, har Dady ya isa ba kin k'ofar d'akin da azama ya tura k'ofar ya shiga da sauri, ganinta kwance a k'asa Nura yana jan k'afarta zai kai ta bisa gadonsa, wani wawan tsafka Dady ya kai masa ya shak'o wuyansa kana ya zuba masa lafiyayyun mari har uku yana la'antarsa, wani k'arfi Husna ta ji da sauri ta mik'e ta b'oye a bayan Dady tana kuka mai ban tausayi, juyowa Dady ya yi ya rungumeta ya kama hannunta suka fito falo, Nura kuwa jikinsa ne ya mutu da haushin Dady ya b'ata masa show, ga kuma zafin marin da ya yi masa, gunguni yake yi tare da dafe kuncinsa ya biyo bayansu.

Dady ya soma masifa bakinsa har kunfa yake yi, Husna kuwa kakkarwa ne jikinta yake yi da fitar hakawayen wahala, Momy ta ji hayani ya yi yawa ta fito falo a tsorace, mamaki ne ya maka ta, ta shiga tambayar Alhaji abin da ya faru, nan ya ce.

"Ga shi nan ki tambaye shi"

Ya nuna in da Nura yake, cike da tsageranci Nura ya fara magana.

"Momy karki yarda dasu sharri suka kulla min, wannan yarinyar ne fa"

Ya nuna in da Husna take, ya cigaba da cewa.

"Tta ce ta biyo ni har d'aki wai in taimaketa in yi amfani da ita wai feelings ne ke damunta, ni kuma nak'i yarda shi ne muka soma kokawa da ita, sai na gaura mata mari ta yi k'ara shi ne Dady ya zo ya ganmu, ya mareni har sau uku yana zagina"

Kan Dady ne ya d'aure yadda Nura ya samu damar shirya wannan k'arya a cikin mintuna kad'an, jin gina kansa ya yi da jikin kujera ya lumshe ido saboda rad'ad'in da zuciyarsa yake yi masa.

Momy ne ta yi tsarab ta ce.

"Ai dama Alhaji na fad'a maka yarinyar nan ta dad'e da fara bin maza, wato ma iskancin bai tsaya a waje ba sai kin zo har cikin gida kin yi da d'an uwanki, anya ma haukan nan da kike yi ba na zina bace kawai, ko kuma kila ta zina aka haifoki, kinyo gado wurin uwarki"

Wani yunkuri Dady ya yi da k'arfi ya mik'e, lafiyayyan mari ya sakarwa Momy kuga d'aya wanda ta kusa fad'i k'asa, yana kallonta cikin ido, bai iya furta komai ba ya finciki hannun Husna ya kaita d'akinsa yasa key ya rufe, sai da ya dai-daita natsuwarsa sannan ya danne fushinsa dan ya dawo ya bawa Momy hakuri, dan ya cire mata zargin har yanzu bai cikin hayacinsa.

Ta b'angaren Momy kuwa mamaki ne ya cika ta, ta  fara tunanin kashinta ya bushe, dan alamu

sun nuna asiri ya karye, ya dawo ya same su a tsaye sunyi cirko-cirko, tsayawa shima ya yi ya ce.

"Hajiya ki yi hakuri ban san sanda na mare ki ba, kai kuma jeka d'aki zan d'auki mataki akan ta, ai ban san cewa ta zama haka ba sai yau, na yi tunanin kaine ka nima b'ata mata rayuwa ashe itace me son b'ata ka, tunda ita ta jima da lalacewa karku damu zan d'auki tsastsauren mataki a kanta"

Farin ciki ne ya cika Momy da jin kamalansa, har wani ajiyar zuciya ta saki mai cike da murna, hankalinta ya k'ara kwanciya ta ce a ranta.

'Boka aikin ka na kyau'

Dady yana gama jawabinsa ya wuce sashensa ya barsu nan tsaye. Ita ma Momy d'aki ta wuce ta ce ma Nura ya je ya kwanta da safe za su yi magana. Shima ya wuce ya kulle k'ofa yana farin cikin yadda duk suka yarda da sharrin daya kullawa Husna.

Dady yana isa falonsa ya rufe d'akin da key, in da Husna ta zauna ya nufa, cike da tsoro ta mik'e tana kallonsa, yadda yaga ta tsorata sai ya bud'e mata hannu alamar ta je ta shiga, da sauri ta isa ta rungume shi ta fara sabon kuka mai tsuma zuciya, shima duk dauriyarsa sai da ya fidda kwalla, janye jikinsa ya yi ya zaunar da ita kan kujara shima ya zauna kusa da ita, ya nima da ta fad'a masa gaskiyat abin da ya faru, haka ta labarta masa yafda suka yi tana kuka, murmushin takaici ya yi ya ce.

"Karki damu ko kad'an ban yarda da abin da suke fad'a ba, nasan baza ki aikata haka ba, kuma yau na tabbatar ba kida haukar komai sharri ne kawai"

Murmushin jin dad'i ta yi fuskarta kwance da hawaye, shima murmushin ya yi mata ya ce.

"Daga yau a nan d'akin zaki rik'a kwana, zan kwaso miki kayan ki gaba d'aya ki rik'a barci a nan"

Sannan ya d'aura da yi mata fad'a da nasiha, farin ciki ya cika ta wanda har sai da ya nuna a fuskarta.

'Yau ni ce Dady kewa nasiha, ashe dama yana sona'

Wannan zancen duk a zuciya take fad'a, a fili kuma godiya ta yi masa, Dady yana mamaki da yawan godiyarta, ya mike ya shiga toilet ya had'a mata ruwan wanka kana ya ce ta shiga ta yi wanka dan ta gasa jikinta. Sai ya fita ya je d'akinta ya kwaso mata kayanta duk na amfani ya kulle k'ofan, ya dawo ya shiga jera mata a waldrop d'insa ya aje wanda suka rage a gefe cikin jaka, mamakin kayan da take dasu ya shiga yi, gasu masu kyau da tsada kuma ya san ba shi ne ya siya mata ba,

'To wai duk a ina ta samu wannan kayan?'

Tambaya ya kewa zuciyarsa wanda ba shi da amsar su sai in ya zurfafa bincikensa. Ko da ta fito ta ga Dady yana ta aikin adana mata kaya sai farin ciki ya rufe ta, wasu kaya marasa nauyi ta sanya kana ya ce ta kwanta a godonsa, ya rufe ta da bargo ya mata sai da safe. Sannan shima ya d'auki wani extra bargonsa ya fita falonsa ya kwanta bisa doguwar kujera.

*******

*Washe gari da asuba*

Da zai fita sallar asubahi ya kulke ta a d'akin ya fito ya wuce masallaci, bayan sun idar Dady ya samu Baba mai gadi a kan bencinsa shima ya zauna, mamaki ne ya cika Baba ya gaishe da Alhaji shima ya amsa cikin fara'a, Baba ya ce.

"Alhaji in ce dai lafiya, dan bamu taba zama irin haka da kai ba?"

Gajeran murmushi Dady ya yi ya ce.

"Hakane, magana za mu yi, kuma ai dani da kai duk daya muke a wurin Allah face wanda yafi wani imani"

"Kwarai kuwa Alhaji, amma wasu masu kud'i irin ka ba kowa ke da wannan fahimtar ba"

"Kowa da irin rayuwarsa, Allah dai yasa mu dace. Ameen"

Nan Baba ya tattara tsuwarsa kansa a sunkuyar alamar girmamawa ya ce.

"Alhaji ina saurarenka"

Dady ya nisa ya soma magana.

"Ina niman wata alfarma ce a gunka, Husna zata rik'a yini a gunka inna fita aiki, da safe zan aje mata uniform d'in islamiyarta a wurinka, in ta dawo boko zan baka kud'i ka siya mata abincin da zata ci, sannan in lokacin zuwa islamiya ya yi ta shirya ta a je na bokon a nan, in ta sawo daga islamiya to sai ta jira ni a nan wurinka har sai na dawo sai mu shiga ciki tare"

Mamaki ne ya cika Baba amma sai ya danne, cikin fara'a ya ce.

"Ai ba damuwa Alhaji, Husna na d'auketa jika a guna, ada na yi mata haka balle yanzu"

Dady ya yi masa godiya kana ya mik'e ya shiga ciki, hamdala Baba ya yi ya ce.

"Allah ka k'ara karkato zuciyar Alhaji ya cigaba da gane gaskiya"

***

Dady ne cikin shirin fita aiki, Husna ta shirya ita ma ya ce ta jira shi a waje, ya nufi d'akin Momy, yana isa yaji tana magana da k'arfi kamar tana fad'a, tsayawa ya yi yana sauraren abin da take cewa, shuru yaji ta yi, har ya yi yunk'urin shiga sai yaji muryan Nura na cewa.

"Wallahi Momy sha'awarta ya dameni shiyasa har na kira ta don in aiwatar mata, kuma ko a yanzu ban jenye ba"

"Haba Son na ce maka karka yi haka dan zaka b'ata min aiki na, saboda yanzu Alhaji zai sa ido sosai akai, kuma kaga yadda na yi asirin rabasu ga shi yana k'ok'arin karyewa, d'an tuggu da nake had'awa da shi, shi ne kesa asirin na dad'a tasiri a gunsa, dan haka karka sake k'ok'arin yi mata fyade so nake tabar gidan nan, kaga sai muce haukar data ke yi ne ya yi tasiri a hanka harta fita ba'a sani ba, ni wallahi Husnar ma tsoro take bani, ina tunanin ko na maidata gun likita ya k'ara mata wasu maganin sanya haukar da ya bata da tana k'arama, amma ban san ya zanyi ba dan ina tsoronta"

Nan ta cigaba da jero muguntat da ta shukawa Husna, da azaban da ta bata tun da tana k'arama, dariyar mugunta Nura ya yi ya ce.

"Yo ai Momy kin fini mugunta wallahi, ji yadda kike ta lissafo abin da kika aika ta mata wanda ban da labarinsu, ni fa Momy ina so ki bar min ita kawai na cigaba da shanawa da ita"

"Dan ubanka ko kunyata ba ka ji kake wannan maganar, ka fita can waje ka yi iskancinka amma banda 'yar mazinaciyar nan"

Runshe ido Dady ya yi yana fitar da hawaye mai zafi, ji ya yi kamar ta watsa masa wuta a zuciya da kallamar 'yar mazinaciya. Maganganunta sun firgitashi sosai, ya yi dana sanin aurenta tare da la'antar ta a zuciyarsa.

A kankali ya jenye jikinsa ya wuce d'akinsa, sai da ya dai-daita natsuwarsa kana ya fara tunanin ta ina zai bullowa lamarin nan, dole sai ya yi hakuri yabi abin ta yadda Momy ba zata gane yana hayyacinsa ba gudun karta koma ta k'ara shirya masa wani sihirin, kyakkyawan tsaro zai cigaba da bawa Husna, jin motsin an bud'e k'ofa ne ya farka firgigit daga dogon tunanin da ya yi, Husna ce ta shigo tana yi masa murmushi ta ce.

"Dady zanyi latti fa"

Tashi ya yi da sauri ya ce.

"Ohh sorry my dear mu je"

Ko da suka fito falon ba kowa, Dady ya bama Baba mai gadi kayan Husna da kuma kud'i masu kauri wanda zai rik'a siya mata abinci. Kana ya bud'e masa gate ya fita da mota, d'aukar Husna ya yi suka je wurin cin abinci, ya yi musu take away, dan ya yi alwashin ko ruwa Momy ta ba shi ba zai kara sha ba balle abinci. Sauketa ya yi a makaranta ta shiga kana ya wuce office cike da damuwa.
[10/28, 6:34 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 37 ~ 38_*

Tun daga wannan rana Dady ya sanyawa Husna ido sosai, duk in da yake a cikin gida tofa suna tare, in zai fita ya turavta wurin Baba mai gadi, in ya dawo kuma su shiga ciki tare, kwata-kwata ya daina cin abincin Momy Hatta Husna ya hana ta ci, ya cika fridge d'in d'akinta da drinks da fruits. Da safe su fita su Karya a restaurant, da rana ya ci a ofiice Husna kuma Baba ya siya mata, da yamma kuma ya yi musu take away. Wannan sauyi da Dady ya yi yana matuk'ar damun Momy, amma a fuska Dady bai sauya mata ba ko ta tambaye shi me yasa baya ci, ya ce shi bai damu da cin abinci ba saboda baya jin dad'in bakinsa, ko da Husna ta daina ci bata damu ba cewa ta yi tafi nono fari.

Momy ko ta je turakar Dady ba halin sakewa saboda Husna na ciki, haka zata yi ta mita.

"Nifa ana shiga hakk'ina tunda yanzu ka mai do mai kama da mayun nan d'akin ka to sai dai ka rik'a kwana d'akina"

Shi dai ba um ba um-um, sai ya ce mata zai zo, dana fita ya sanya key ya rufe d'akin ya yi kwanciyarsa a dogon kujera. Haka zata kwata tana masifa da mita ita kad'ai har barci da sace ta. Momy ta rasa ta ina zata bullo masa, ko ta zo zata masa magana ya had'e giran sama dana k'asa ya sha kunu, dole ta hakura ta mai da maganar ta domin yanzu ta soma shakkarsa.

Tunani ta soma na zuwa wurin boka, amma kota tambayi Dady fita sai ya hanata, inta matsa masa ya ce a bakin aurenta, dole ta koma ta zauna tunda tana son mijinta. Kawarta Haj. Uwani ta kira ta zayyana mata halin da take ciki nan ta ce.

"Kin ga ki lallab'ashi dan wallahi in kika bari ya kub'uce miki tofa kin rasa shi kenan, dan haka ni zanje wurin boka ya duba mana lamarin duk abin da ya ce, ko ya bani zan kawo miki sai ki k'ara gwada wani sa'a"

Cikin farin ciki da shawarar da ta bata suka yi sallama.

******

*Washe gari*

Sai ga Haj. Uwani ta zo, haka suka k'ule a d'aki, ta bata wani kullin magani har uku tare da bayanin d'aya zata sanya masa a abinci d'aya kuma a ruwan sha, d'aya kuma ta yi hayaki, duka maganin ana so a yisu a lokaci d'aya, nan Hajiya ta shiga zullumi ta ce.

"To ya zanyi ni da ya daina cin abincina, ko ruwa na ba shi sai ya ce ya gode yanzu ya sha a d'akinsa, wallahi Khalil ya sauya fa fiye da tunaninki"

Murmushi ta yi mata ta ce.

"Haba Haj. Habee duk kin wani susuce, ya kamata ki gwada kissarki mana, ki lallabashi ya ci, wallahi a take a nan zaki sha mamaki"

"To shi kenan zanyi k'ok'arin haka, amma ni kwarjini yake min dama kin sanshi ba mai fara'a bane, to yanzu ya dad'a gimtse fuska ko hira bama yi, rabon da mu kwana tare na manta"

Nan Haj. Uwani ta cigaba da bata shawarwari, har sai da Momy taji ta gamsu sannan suka yi sallma ta tafi.

Da yamma Husna ta dawo daga islamiya ta zauna wurin Baba tare da ce masa.

"Baba bari na shiga gidan Uncle Sadiq na dawo yanzu"

"A'a fa Husna kin san Alhaji ya bani amanarki, kuma ran nan ya nuna baya so kina hurd'a da shi, bana so ya dawo yaga baki nan, dan ya kusan dawowa, raina da naki duk zai b'aci"

"Dan Allah Baba ka bari na shiga, yau kusan sati buyu bamu had'u ba zan je na gaishe shi ne na dawo ka ji"

Ta k'are maganar da shagwaba kamar za ta yi kuka.

"To 'yar Baba dan Allah kar ki dad'e ki dawo yanzu"

"To Baba"

Ta ce cike da murna ta mik'e da sauri ta shige gidan, ta yi sa'a gate d'in a bud'e yake, haka ta kutsa kai cikin falonsa shima a bud'e ta samu, ta shiga kwada sallama amma ba Wanda ya amsa, sai kawai ta wuce bedroom dan ta duba shi, a nan ta same shi yana kwance bisa gadonsa cikin bargo, da sauri ta k'arasa bakin gadon ta zauna ta ce.
"Laaa Uncle barci kake yi? ka tashi na zo gaishe ka"

Shuru taji ba amsa, sai ta fara tunanin ya za ta yi ta tashe shi, shi ko Sadiq yana jinta lumshe ido ya yi saboda zazzabin dake damunsa, kusa da fuskarta ta matsa ta shiga kiran sunansa a hankali.

"Uncle, Uncle, Uncle"

Ta kira shi har sau uku, a hankali ya bud'e idonsa cikin sarkewan murya tsan k'asa ya ce.

"My Husnaaa"

Ji ta yi tsigar jikinta ya ta shi, nan da nan ta ji bak'on yanayi a jikinta, kallon kallo suka yi na tsayin minti uku, ta bud'e baki za ta yi magana ya tashi da kyar ya zauna yana fad'ar.

"Wash Allah na"

"Uncle me yake damunsa kamar ba kada lafiya ko?"

Murmushin k'arfi hali ya yi mata ya ce.

"Kaina ke min ciwo da d'an zazzab'i"

"subhanallahi! Sannu uncle"

Ta ce kamar zata yi kuka.

"Kar ki zubar da hawayenki naji sauki, yanzu ta shi ki shiga bayi ki had'a min ruwan wanka, kila in na yi zan ji k'arfi a jiki"

Kan ya rufe baki har ta mike ta isa bayi ba tare da ta ce masa komai ba, ruwa ta had'a masa mai zafi kana ta fito ta same shi tsaye daga ci sai gajeran wando da singilet dama a haka ya kwanta, kallo d'aya ta masa taji cigar jikinta yana ta shi da sauri ta kauda kai ta ce.

"Ga ruwan can na had'a maka"

To kawai ya ce mata ya shiga bayi, bakin Waldrop d'insa ta tsaya ta bud'e, kananan kaya ta ciro masa ta aje kan gafen miro, gadonsa ta kakkab'e ta gyara kana ta share d'akin ta sanya turaren wuta a bona, dan Sadiq gaskiya yana da tsafta ga son kamshi shiyasa gidansa kullun tsaf kamar mai mata, ta fita falo shima ta gyara ko ina.

Sadiq ya fito sanye da kayan da ta fito masa dasu, sai ya ga ta gyara ko ina, motsinta yaji a kitchen a she ruwan tea take dafa masa, can ya isketa ya tsaya yana kallonta cike da kulawa, ji ta yi kamar ana kallonta, ta gama had'a komai ta d'auki cup d'in ta juyo karaf suka yi ido hudu, murmushi ya sakar mata mai cike da ma'anoni da yawa, ya juyawa ya isa falo ya zauna, tsayawa ta yi tana tunano murmushin da ya yi mata, haka nan sai taji tana jin kunyarsa. Dole ta fito falo ta mik'a masa ya amsa ya soma sha dan dama yana jin yunwa. Husna da k'arfin hali ta ce.

"Uncle me zan d'aura maka wanda zaka ci yanzu?"

Murmushi ya yi dai-dai lokacin da ya aje cup d'in hannunsa.

"Haba my Husna kin sha aiki sosai, wannan ma da kika bani nagode kwarai, shiga ciki ki d'auko min wayata"

To ta ce masa tare da ta shi ta wuce ciki, ta d'auko masa taba shi. Sadiq abokinsa ya kira mai suna Yasir ya ce ya zo gidansa yana son ganinsa yanzu.

Cikin farin ciki Ya sir ya ce masa gashi nan zuwa.

Yasir abokinsa ne na gurin aiki, tunda yaga Sadiq yake shige masa dan yana burge shi saboda natsuwarsa, shi kuma Sadiq baya son mutane miskili ne, haka yake basar da Yasir shi kuma ya kasa fushi da abin da yake masa, a haka har suka d'an saba amma duk da haka Sadiq yaki sakin jikinsa, saboda shi tun tashinsa bai da wani aboki kullun cikin *kad'aici* yake, ko a school sai dai abokan karatu amma bai da Amini.

Ta b'angaren Baba kuwa Dady ya dawo da wuri, tafiyar Husna baifi da minti goma ba ya dawo, suka gaisa Dady ya shiga tambayarsa

"Ina Husnah?"

Cike da tsoro da fargaba ya ce.

"Ta ce min zata gidan k'awarta yanzu zata dawo"

Dady ya gimtse fuska.

"Yaushe ta soma yawo haka har wata k'awa gareta, lallai Husna, mai yasa ma ka barta ta tafi?"

"Ka yi hakuri yanzu zata dawo"

Tsaki ya yi bai ce komai ba, ya fita k'ofar gida ya zauna kan bancin da Baba ke zama dan yaga ta ina zata b'ullo, tun yana danna waya yana yi naya duban hanya, harya hakura da danna wayar ya sanya a aljihu dan abin ya soma damunsa, domin kusan awa d'aya kenan da dawowarsa ba Husna ba labarinta, lokaci zuwa lokaci yake yin tsaki, duk wani annurin fuskarsa ya d'auke, Baba kuwa matsananciyar damuwa ya shiga bai so faruwan wannan lamarin ba, yana gudun abin da zai faru.
Yasir ne ya yi parking motarsa k'ofar gidan Sadiq, ya d'agawa su Dady hannu tare da sallama dan babu nisa tsakaninsu. Baba yaji gabansa ya kuma fad'uwa, domin har an soma shirye-shiryen  kiran sallar magrib.

Da sallama Yasir ya shiga falon cike da fara'a a fuskarsa, Sadiq ya amsa masa, ya kai dubansa ga Husna da take wasa a system d'in Sadiq ya ce.

"Yan mata ba magana"

Da murmushi ta ce.

"Ina wuni"

Ya amsa cike da kulawa, ya kai dubansa ga Sadiq.

"Amma dai wannan sister d'inka ce ko? dan kun yi bala'in kama"

"Haba Yasir ba wani kama da muka yi"

"Hmmm ai dama kai ba zaka gani ba, amma wallahi kuna kama sosai, ko ita ce sister d'inka Zahra?"

"Kai fa ka fiye surutu, ba wannan nake so mu yi magana akai ba, me makon ka tambayeni dalilin kiranka da na yi, amma ka tsaya kana bincike kan abin da ba ruwanka. To asibiti nake so ka kaini dan ban da lafiya, wallahi tunda na baro office nake kwance sai da Husna ta zo ta taya ni shiryawa"

"Ayya sannu, Allah ya baka lafiya, to mu tafi daga nan sai mu tsaya a masallaci mu yi sallah"

"Ok, Husna tashi ki je gida kar Dady ya dawo fa"

Ai yana ambaton Dady taji gabanta ya fad'i, tama manta da gargad'in da Baba ya yi mata sai yanzu ta tuna.
[10/29, 2:12 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 39 ~ 40_*

Da sauri ta mik'e tana cewa cike da damuwa.

"Allah yasa bai dawo ba kuwa"

Yasir ya bita da kallo ya juya yana kallon Sadiq.

"Abokina gaskiya ina ciki da k'anwarka ta yi min, ko da dai bata gama girma ba na san yanzu bata wuce 16yrs ba"

Harararsa Sadiq ya yi.

"My Husna bata son tuzuru sai saurayi matashi amma kai ka mata tsufa"

"Tafd'i jam amma fa ka samoni, ai dani da kai duk tuzuran ne, ni dai pls ina kamu zan jirata harta girma, gata mai kyau ta dace da sunanta"

Tsaki Sadiq ya yi.

"Kaifa matsalata da kai surutu, ban ma san meyasa na kiraka ba, da Emanuel na kira hankalina kwance"

"Haba aboki kana sona ne ka kirani ai dan nafi Ema a gunka"

Sadiq ya yi murmushi tare da fita, Husna na biye dasu ya rufe d'aki yana k'ok'arin bud'e motarsa yasir ya ce.

"Kai da mota nazo fa yana waje"

"Au nafa manta kana da mota"

"Ai dole ka manta tunda ba damuwa kayi da munatane ba, na zo gunka ma kana niman mini wulakancin da ka sab"

Dukan wasa Sadiq ya kai masa.

"Yasir mai da wuk'ar, mu tafi"

Sadiq ya fara fitowa da murmushi a fuskarsa Husna na bayansa, sai Yasir daya fito karshe yana rufe gidan.

Kamar ance Dady ya kallesu, ganin su ya yi tare da Husna wanda ita tuni ta daskare a gun tana rawar jiki, Sadiq da bai kulaba yana cewa.

"Husna sai da safe"

Jin shurun data yi masa ne yasa shi ya waiwayo, abin da ya gani ne ya tashi hankalinsa. Wani mugun kallo Dady ke ma Sadiq, cikin tsawa ya ce mata.

"Zo nan"

Jikinta na b'ari ta k'arasa tana kuka, wani mari lafiyayye Dady ya sakar mata a fuska, ya juya wurin Baba ya ce cikin fada.

"Haka ake rik'on Amana, yarda da na yi da kai yasa na barta gunka ta rik'a zama, amma da haka zaka saka min, dama na dad'e ina tunanin ta ina Husna take samu kud'in siyan kayan data ke sawa da wasu abubuwan, ashe ta wannan hanyar take samunsu, yanzu Husna duk kamewarki ta wannan hanyar zaki saka min ko? Dama abin da Hajiya ke fad'a kina yawo dagaske ne? ko da yake banga laifinki ba laifi ne dana sake ki sakaka babu wani kulawa, a yau nake dana sani akan haihuwarki da auren da na yi bisa kuskure, tunda muka yi aure da mahaifiyarki muka tsinci kanmu a cikin matsala da tashin hankali, har na rabu da ita ban kuma samun farin ciki ba. Ina kyautata zaton shi ne zai yi ajalina, dan dana ga irin wannan rana gwara mutuwata kuma...."

Wani irin kwarewa yayi, numfashinsa ya sark'e tare da fidda kwalla mai zafi, bakinsa ne ya soma fidda jini tare da dafe kirjinsa, yana k'ok'arin fad'uwa Baba yaje da sauri ya kama shi, ihu Husna ta saki wanda ya yi dai-dai da faduwar ta k'asa a sume.

Sadiq ya yi kan Dady, Yasir kuma wajen Husna ya nufa. Da taimakon mutane suka sanya su a motar Yasir, da gudu Sadiq ya figi motar kamar zai tashi sama, ji ya yi ya warke ba wani ciwo dake damunsa. Sun isa Ummulkhairi hospital, aka turasu emagency, Doctor uku suka dukufa kan Dady, Husna Doctor biyu suke kanta, tun Magrib suke abu d'aya sai kusan k'arfe takwas likitocin suka fito tare da yarfe zufa. Su Sadiq suka tare su da tambaya, d'aya daga ciki ya ce.

"Ku kwantar da hankalinku, mun shawo kan matsalar dan yanzu barci yake yi, ku sameni a office"

Haka suka bi bayansa, Sadiq na tsaye dan ya kasa zama, Baba da Yasir suka zauna kan kujerun da ke kallon likita, likita shima yana zaune kan nasa kujerar tare da goge zufar dake fuskarsa da farin hankacif, ya nisa ya soma magana.

"Bincikenmu ya nuna Alhaji yana da damuwa a zuciyarsa wanda yake k'ok'arin haifar masa da ciwon zuciya, yanzu dai yana barci insha Allah zuwa wani lokaci zai farka"

Nan ya rubuta magani ya ce suje su siya a nan cikin pharmacy na asibitin, sannan kuma zai cigaba da zama a asibiti yana amsar treatment har zuwa lokacin da yaji sauki, suka yi godiya Yasir ya karb'a takardar ya ce su Sadiq su wuce gun Dady.

Likitocin da suka duba Husna sun fito tare da yima su Sadiq bayanin cewa.

"An shawo kan matsalarta, kawai firgici ne amma nan da wani lokaci zata farfad'o"

Suka rubuta magani su je su siya, Sadiq da Baba suka musu godiya sannan suka tafi.

B'angaren Momy kuwa, ta ci ado tai kyau kamar ba ita ba, sai kamshi da shek'i take yi, ta yi wani uban d'aurin dankwali ta dawo kamar yarinya, girki ta shiryawa Dady kusan kala uku tare da drink kala biyu, ta shirya a dinning ta gama barbad'esu da maganin da Haj. Uwani ta kawo

mata, zama ta yi a falo tana kallon TV domin jiran dawowar Dady, lokacin da taji k'arar motarsa da ya yi parking sai wani jin dad'i take yi, shi kuma dama ya koma waje ya tsaya yana jiran dawowar Husna, jin shuru bai shigo ba sai ta yi tunanin k'ila yana magana da wani a wajen ne, shuru-shuru har aka yi sallar isha'i ba Dady ba dalilinsa, sai ta yi tunanin yana masallaci k'ila tun sallar magrib.

Shurun taji ya yi yawa sai ta fara damuwa ga shi har k'arfe goma, sai ta sanya gyale ta lek'o dan ta tambayi mai gadi, shima taga baya nan ta shiga kwala masa kira amma taji shuru, gabanta ne taji ya fad'i ta fita k'ofar gida shuru ba mutane sai motoci da suke wucewa d'ai-d'ai, tsoro ne ya ziyarce ta ta koma gida da sauri, cikin tashin hankali ta tsinci kanta tana cewa.

"Wayyo na shiga uku in yau Alhaji bai ci abincin nan ba, ai na yi asara kenan, ga shi duka maganin na zuba a ciki, tunda dama sawa d'aya ne, na bani ya zan yi"

Haka ta yi ta zaman jiran dawowarsa har kusan sha d'aya da rabi na dare amma shuru. Nura ne ya shigo gidan a bige yasha giya ya yi tatil sai wari ke tashi a jikinsa, da sauri Momy ta tarbesa ya kusan fad'i, ta ce.

"Kai Son daga ina haka? Wai bana hana ka shaye shayen nan ba"

Surutai yake mata barkatai mara ma'ana, haka ta tallabe shi ta kai shi d'aki ya kwanta, ita kuka ta koma falo ta cigaba da zaman jiran Dady, a haka barci ya sace ta, sai sanyin asubahi ne ya tashe ta, ta tashi cikin rawar sanyi ta nufi d'aki.

Da gari ya waye Momy ta farka cike da damuwa, wanka ta yi ta dawo falo, d'akin Dady taje sai ta ji shi a rufe, mamaki da tsoro ne suka kamata, tambayar kanta ta shiga yi.

'To ina yaje tun jiya bai dawo ba? kuwa ga duk kan alamu Husna ma bata nan, wai meke faruwa ne?'

Haka ta isa wurin dinning ta bud'e abincin da ta yi duk sunyi sanyi, d'auka ta yi ta mai da kicin da aniyar ba zata zubar ba, zata d'umama masa sai ya ci dole, dan baza ta yi asara ba.
[10/29, 6:32 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 41 ~ 42_*

*A asibiti*

Dady bai farka ba sai misalin k'arfe takwas na safe, Sadiq na gefensa yana danna waya, ajiyar zuciya Dady ya yi wanda yasa Sadiq ya d'ago kai, ido suka had'a sai Dady ya mai da ido ya lumshe su, da sauri Sadiq yaje ya kira likita. Baba shi yana zaune wurin Husna, Yasir kuma tun d'azu ya tafi saboda zai tafi aiki wanda shi Sadiq ya bayar da excuse d'insa. Tare da likita Sadiq ya dawo, likita ya shiga duba Dady tare da 'yan rubuce-rubuce kana ya ce.

"Alhamdulillah jiki ya samu, dan haka ku kula da abin da zai rik'a b'ata masa rai"

Likita ya fita can sai ga nurses sun shigo suka sanya masa drip da allurai, duk Dady na kallonsu ba um ba um-um, bayan sun gama suka fita, Sadiq komawa ya yi ya zauna yana masa sannu, Dady sai ya kauda kansa gefe alamar bai son maganarsa. Sadiq ya ta shi ya koma d'akin da aka kwantar da Husna, ya samu Baba ya nasar masa Dady ya tashi har da yadda su ka yi da likita, Baba ya yi hamdala ya ce.

"Ga jikata har yanzu bata farka ba, sai motsi kawai take yi"

"Insha Allah Baba zata farka, ya ka mata su had'a mana d'aki daya, sai kai ka je gida ka sanarwa Hajiya, ka samu damar watsa ruwa ka huta, zuwa anjima sai ka dawo"

Baba ya yi murmushin k'arfin hali.

"Ina naga hutu Sadiqu, zan dai je na gayawa Hajiya in ya so sai na dawo"

"To shi kenan nan Baba"

Sai ya ta shi ya tafi shi kuma Sadiq ya je gun likita ya nima alfarmar a had'a Dady da Husna a d'aki d'aya saboda su samu sauk'in jinyarsu, Da farko likita bai so haka ba amma daga bisani ya amince. Cikin k'ank'anin lokaci aka had'a musu d'aki, gadon Dady yana chan gefe hannun dama Husna tana gefen hannun hagu, da yake d'akin da fad'i, Dady juyowa ya yi yana kallon Husna da ke kwance, hawaye ya gangaro masa, ya bud'e baki da kyar ya cewa Sadiq.

"Ta farka kuwa?"

Cikin damuwa ya na shi amsa da.

"Barci take yi"

Dady ya yi ajiyar zuciya tare da lumshe ido.

*******

Baba Mai gadi ya isa gida, ya samu Momy a birkice ya sanar mata Alhaji ba lafiya da Husna, duk a asibiti suka kwana, cike da tashin hankali ta dafe kirji.

"Na shiga uku meya samesu?"

Baba bai iya mata bayani ba sai juyawa ya yi ya bata guri, da sauri ta biyo shi tana cewa ya gaya mata in kuma ba zai fad'i ba ya gaya mata sunan asibitin, cike da damuwa ya ce.

"Ni ma can zan koma yanzu, a Ummulkhairi Hospital aka kwantar dasu"

Bata ce masa komai ba ta koma cikin falo ta shiga kicin ta had'a abincin da ta dumama na jiya wanda take jiran Dady ya dawo ta matsa masa ya ci, aiko shi ta sanya a kwando har biyu ta fito dasu nik'i-nik'i, ta isa wajen gate ta tari mai napep ya d'auketa sai asibiti.

Baba ya samu har an had'a su d'aki d'aya, gadon Dady ya matsa ya yi masa sannu, Dady ya gyad'a masa kai alamar yauwa, Sadiq ne ya tashi ya ce.

"Dady me zaka ci a kawo maka?"

Ya girgiza kai alamar a'a, bai kuma tambayarsa ba yasa kai ya fita Baba ya cigaba da zama a wurinsu, Sadiq gida ya koma ya watsa ruwa saboda jikinsa ba k'arfi ga kuma rashin barci na jiya, kuma har yanzu jikinsa baya masa dad'i, cikin sauri ya shirya ya wuce wani restaurant ya yi musu take away ya koma asibiti.

Momy ta shiga asibitin da kaya a hannunta da tambaya ta isa d'akin su Dady, da sallama ta shiga, wani irin motsi Husna ta yi ta bud'e ido kamar zasu fito waje saboda girmansu, duk ba wanda ya lura da haka, Momy ta ajiye kwandon Dady yana binta da kallo, a fuskar kamar mutuniyar kirki, gaishe shi ta yi ya amsa da gyad'a kai ba tare da ya ce komai ba. Wani irin ihu Husna ta saki mai ban firgici, duk wanda yake kusa da dakinsu yaji wannan ihun mai cike da ban tsoro, ai Momy da gudu ta je gefen gadon Dady jikinta na rawa ta k'ank'ame kamar wacce take jiran saukar bulala, Baba salati ya shiga yi, shiko Dady wani mugun fad'uwan gaba ya yi wanda sai da ya tashi ya zauna, likitoci har biyu suka fad'o d'akin a guje domin ganin me ke faruwa.

A dai-dai wannan lokacin Sadiq ya k'araso d'akin, ganin kowa ya yi cirko-cirko a tsaye, zama Husna ta yi kamar ita ce, kwayar idon ta kamar zai fad'o k'asa, tana wani irin gurnani, takai dubanta gun Momy wacce ta kasa had'a ido da ita, Husna ta yi dariya mai cike da ma'ana ta ce cikin kakkausar murya.

"Habiba ki d'auki abin da kika shigo da shi ki fita daga cikin d'akin nan, da fatan kin gane me nake nufi"

Momy ta yi tsuru-tsuru tana kallon ta, daga likitocin har Sadiq, Baba, Dady sun shiga rud'ani tare da tsorata da yanabyin Husnar, cike da izza ta diro daga kan gadon ta tsaya kem, hannu ta d'aga tana nuna Momy dasu.

"Kin d'auka ban ganin ki ne, kin aika an amso miki magani ko, kin kuma zuba a cikin abinci dan Khalil ya ci ko?"

Ta k'arasa maganar tana murmushi tare da girgiza kai, ta cigaba da cewa.

"Na gaya miki had'uwa ta dake ba zai yi kyau ba, mashirkiya kawai, kin takuwara Husna kin sanya mata cutar hauka, kin gallaza mata, kin muzguna mata, kin kuma raba ta da mahaifinta

mai sonta, kin shiga tsakaninsu, daga k'arshe kin had'a mata sharrin zina, k'aramar yarinyar da bata wuce shekaru sha shida ba, tunda Khalil ya aure ki ya baki amanarta tun tana shekara uku kike cin zalinta, kike mata tuggu da k'eta, wallahi ba zamu yarda ba tunda kika tab'a mana Husna, mu muna sonta kuma sai mun wulakan taki"

Kuka Momy ta fara yi tana cewa.

"Wallahi sharri kike min, Alhaji karka yarda da maganarta karya take yi"

Wani irin zabura Husna ta yi ta isa gurin Momy kamar walk'iya, ta damk'i wuyan Momy ta matse iya k'arfinta, da sauri Likitocin da Sadiq suka yi kansu, da kyar suka b'anb'are hannun Husna a wiyan Momy, suka mai da ta kan gado suka danne ta, tana wani irin gunjin kuka.

"Ku barni na kasheta kamar yanda taso kashe mana Husna, sai mun rama mata, ku sake ni ku sake ni"

Nan Sadiq da Baba suka shiga tofa mata Addu'a, suma likitocin da yake Musulmai ne suka shiga tofa mata har sai da ta tafi, kafin nan Husna ta yi atishawa mai k'arfi ta ta shi tana kallon kowa dai-dai, ita kuma Momy durk'ushewa ta yi tana mai da numfashi tare da tari mai k'arfi, da taga Husna ta ta shi zaune ba arziki ta mik'e da sauri cike da borin kunya ta d'auki kwandon abincin da ta zo da shi ta fita jiki ba kwari, ko sai anjima ta kasa furtawa, duk suka bita da kallo kowa da abin da yake sak'awa a zuciyarsa.

Sadiq ya matsa mata maclean a akan brush d'in da ya siyo musu, ya kai ta bayi ya fito ya bata wuri, ta wanke baki tare da d'auro alwala ta fito, ta gabatar da sallar da ake binta, bayan ta idar ta koma kan gado ta zauna tare jingina bayanta a jikin pillow.

Nan likita ya d'aura ta kan magani, Sadiq ya mik'a mata cup din tea da ya had'a mata tare da take away na abincin da ya siyo musu. Dady bin Sadiq ya yi da kallon mamaki, nan take yaji ya kwanta masa a rai, yana jin haushin kansa daya yanke musu hukunci ba tare da bincike ba, tabbas zuciyarsa na gaya masa Sadiq yaron kirki ne. Baba yana gefe yana kallonta cike da tausayawa akan ciwon da yake damunta.
[10/30, 3:43 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 43 ~ 44_*

*Bayan kwana biyu*

Su Dady sun ji sauki sosai, dan sun samu kulawa mai kyau a gurin likitoci tare da kulawar Sadiq da Baba, kwanan su biyu aka sallame su.

Bayan sun isa gida, Dady ya wuce sashinsa, sai da ya watsa ruwa kana ya fito ya sanya kaya marasa nauyi, ya umarci Husna ita ma taje ta yi wanka ta canza kaya, falo ya zauna ya kunna tv yana kallon tashar al-jazeera, fanka na juyawa a hankali iska na kad'a shi, hakanan ya tsinci

kansa cikin nishad'i, bayan wani lokaci sai ga Husna sanye cikin doguwar riga na shadda wanda ya kamata daga sama, fuskarta fayau ba kwalliya amma duk da haka bai hana bayyar kyanta ba, Dady ne ya bita da kallo, ta rame sai ta yi tsawo, tausayinta ne ya kama shi cike da kulawa ya ce.

"Har kin yi wankan?"

"Eh Dady na yi har da sallar azahar"

"Da kyau kin kyauta, zoki zauna ki huta kema"

Husna ta zauna gefensa kan 3sitter ta cigaba da kallon TV.

*****

B'angaren Momy kuwa tun ranar da ta dawo gida daga asibiti, ta rasa abin da ke mata dad'i, abin duniya ya ishe ta, sai ta kiran Haj. Uwani ta labarta mata duk abin da ya faru, cike da damiwa ta ce.

"Haj. Habee ina ga sai dai mu hakura dan wallahi nima ina cikin matsala, Alhaji ya hanani fita ko nan da can, ya ce in har na fita a bakin aure na, wai duk yawace-yawacen dana ke yi ana gaya masa, har zargina yake yi wai ina bin maza, ke in k'ark'are miki labari, a ranar ya cimin mutunci a gaban kishiyata, na yi kuka har na gode Allah, aure na yanzu lilo yake yi dan haka na saduda na barwa Allah, zan rik'e aure na tunkan ya gutsire"

Ajiyar zuciya Momy ta yi wanda ya bayyana tsantsar damuwar da take ciki, cike da karayar zuciya ta ce.

"Wallahi ni kaina ya kulle, ina tsoron matakin da Alhaji zai d'auka a kaina, kuma wallahi ina sonsa ban shirya rabuwa da shi ba"

"Ato tunda kina son zaman aurenki ai sai ki saduda kema ki ba shi hakuri ki gyara zaman aurenki, dan ni yanzu na hakura da komai na kama Allah, tunda na yi asirin in fidda kishiyata, na mallake Alhaji amma bai je ko ina ba ya karye, dan haka zan yi biyayyar aure, ki yi tunani na barki lafiya"

Bata jira mai Momy zata ce ba ta kashe wayar tare da bin wayar da tsaki.

"Allah ya wadaran kawar banza, duk ke kika jamin matsalar nan, dole ma in rabu dake dan kar ki ja min na rasa aure na"

Momy kuwa mamakin Haj. Uwani ta yi yadda ta sauya lokaci d'aya, damuwanta ya k'aru da tunanin matakin da Dady zai dauka a kanta.

Yau ma dasu Dady suka dawo tanajinsu ta kasa motsi mai k'arfi, kunya ce da nadama ya cikata tana jin nauyin had'a ido da shi da fargaban hukuncin da zai yanke mata, shiyasa ta kulle kanta a d'aki tana kai ko mo da tunani bar katai.

Sadiq ne ya yi sallama rik'e da leda a hannunsa, cike da farin ciki Dady ya amsa masa tare da masa umarnin ya zauna, ya zauna a k'asan kafet Dady ya ce ya zauna a kujera, bayan ya zauna ya gaishe shi tare da yi masa ya jikinsu, Husna ta gaishe shi cike da girmamawa, Sadiq ya ce.

"Husna tashi ki je ki d'auko plate da cup a cikin"

Da hanzari ta mik'e ta wuce kicin ta d'auko ta dawo ta mik'a masa ya amsa, take away na abinci daya siyo musu ya fara juyewa a plate d'in ya sanya ta ta d'auko tsokali, ya mik'awa Dady na shi ita ma ya mik'a mata nata, ya ajiye goran juice a kan center table tare da cup d'in, ya matsar da shi gaban Dady, sai ya mai da hankalinsa ga tv, Dady na binsa da kallo cike da k'auna a zuciyarsa, yana jinjina karamci irin na Sadiq, ya fara cin abincin, ita ko Husna tak'i cin nata ta kalli Sadiq.

"Uncle ina naka abincin?"

Sadiq ya kalleta da murmushi.

"Na ci nawa"

Husna ta yi murmushi sannan ta fara cin abincin. Bayan sun kammala Dady ya kai dubansa ga Sadiq.

"Sannu da k'ok'ari mungode kwarai, Allah ya saka maka da alkhairi ya yi maka albarka. Ada ina yi maka wani irin kallon, amma cikin k'ank'anin lokaci na fahimce ka, ka yi hakuri"

Sadiq kansa a sunkuye ya amsa da ameen tare Ida yiwa Dady godiya. Dady ya nima Sadiq ya kira masa Baba mai gadi, shima godiya Dady ya yi masa tare da niman alfarma a nimo musu 'yar aiki wacce zata rik'a kula da Husna tare da yi musu girki, nan Baba ya ce.

"Ai Alhaji zan je na lalubo Jimmai mai aiki domin ta dawo aikinta, dan tana da kirki kuma ta taimaka wa Husna sosai"

Cikin farin ciki Dady ya amince da haka kana suka cigaba da hira dukansu, Husna na kallon tv bata sanya musu baki ba.

*****        *****

Tun daga wannan rana Momy taki yarda su had'u da Dady, in kuwa sun had'u kanta na sunkuye bata iya had'a ido da shi, shi ko Dady kota gaishe shi bai amsawa kuma har zuwa lokacin bai yanke wani hukunci a gareta ba ya zuba mata ido, haka ta koma rayuwar *kad'aici* ba mai shiga safgarta, Nura ma baya kwana gidan yanzu sai ta yi kwanaki bata sanya shi a ido ba. Hatta Jimmai mai aiki Dady ya gargad'eta sosai akan Momy, ita ke musu girki da gyaran gida, in kuma Dady ya fita suna tare da Husna har ya dawo saboda aikin kwana take yi. Daga Husna har Dady yanzu suna rayawan walwala da jin dad'i.

Dady ya sanya wasu su yi masa bincike sosai a kan Sadiq, sannan Baba mai gadi ya ba shi labarin duk taimakon da ya yiwa Husna, wannan yasa Dady k'ara samun natsuwa da Sadiq sosai, duk kuma binciken da ya yi bai ji wani abu b'atanci ga Sadiq ba, sai dai bai samu wani cikakken labari game da iyayensa ba, duk wanda zai tambaya sai suce basu sani ba amma dai sun san shi kad'ai yake rayuwa a gidan kuma yaron kirki ne.

*****     ****     *****

*A Kaduna*

Husna pharmacy ya hab'aka, kullun suna cikin cikowar jama'a, Anty Zainab ta tattara natsuwarta gaba d'aya wajen business d'inta, taki bawa mane manta dama kan zancen aureta, a kullun burunta bai wuce Allah ya had'ata da masoyinta Khalil tare da 'yarta Husna abar k'aunarta, 'yan uwa sunyi mita har sun gaji kan maganar ta yi aure, ita dai kullun cewa take in lokaci ya yi zata yi, Little Al'amin yana samun kulawa sosai wajen Zainab, ya yi wayo da girma wanda har ya soma zuwa makaranta.

******

*KANO*

_*Gidan Yaya Ismail*_

Khadija ta mutu kan son Yaya Sadiq wanda tun tana yi a b'oye harya fito fili, Mahaifiyarta Anty Ameena tana ja mata kunne tare da yi mata fad'a akan rawar kan da take yi a kan Sadiq, wanda shi sam bai san tana yi ba. Akwai wani zuwa da suka yi Kaduna, Sadiq na d'aki ta same shi a can, juice ta kai masa ya amsa cike da kulawa ya sha, nan ta zauna ta fara masa surutu, hayaniyarta ya ishe shi ya daka mata tsawa ya koreta, cike da kuka ta fita falon Ammi Jidda tana kuka, nan Anty Jidda ta sameta ta tambayeta dalilin kukan, nan ta labarta mata abin da Ya Sadiq  ya yi mata, cike da jin haushi Ammi ta same shi a d'aki ta yi masa tatas, hakan da Ammi ta yi masa sai ya k'ara masa tsanar Khadija, tun daga lokacin ya k'ara tamke mata fuska domin ya gane take takenta. Hakan da ya yi bai sa ta sauya ba, ko gidansu yaje na nan Kano sai ta yi ta shige masa, a haka har ya gane manufarta sai ya rage zuwa gidan. Wanda a yanzu duk dangi suna ganin kamar soyayya suke yi, saboda abu kad'an Khadija zata ce Sadiq, kowa na murna da wannan had'i da suka yiwa kansu. Abin da basu sani ba, shi sam ba haka bane a gun

Sadiq bai san da labarin bama.

*******

Haka rayuwa ya yita tafiya, har su Husna sun kammala jarabawarsu na k'arshen secondary school, bayan sun fito daga d'akin jarabawa, Khadija ne rik'e da waya a hannunta tana ta danna-danne, Husna tana gefenta suna tafiya tare, wani wuri suka samu suka zauna, Khadija ta mai da kallonta ga Husna..

"Besty yau ga shi mun gama makaranta amma baki tab'a zuwa gidanmu ba, gwara ni nazo sau d'aya, ga shima ba phone a hannunki balle mu rik'a waya"

Husna murmushi ta yi.

"Ki yi hak'uri kin san Dady na baya barina fita ko zani school sai ya jamin kunne kar in biya ko ina, yanzu dai ki bani number ki zan kira ki da number Dadyna, in ya so sai ki yi saving muna communicating da shi, hakan ya yi miki?"

"Wato ba zaki zo bama sai dai ki yi min waya, to ba matsala ai na kusa barin Kano ma gaba d'aya, zan koma Kaduna a cen zan cigaba da karatu"

"Aiko na yi miki murna, ni dai ina son zuwa Kaduna amma banda kowa a can, ko a nan Kano ba wani yawa familyn Dady suke da shi ba"

"To wai ke ba kisan family Momy din ki ba?"

Husna ta yi murmushi wanda bai kai ciki ba ta ce.

"Ban san su ba, ko na fara yiwa Dady maganar Momyna sai ya hauni da fad'a, tunda naga baya so sai na kyale shi, har yau ban san Momy na ba"

Ta k'arasa maganar da kuka, Khadija duk sai taji jikinta ya yi sanyi.

"Karki damu insha Allah zaki santa ki yi ta Addu'a, amma ina fatan zaki zo bikina da yaya Sadiq, dan dana soma karatu za a sanya biki, a d'akina zan k'arasa"

Cike da farinci ciki husna ta ce.
"Wai dan Allah da gaske kike yi aure zaki yi da wuri?"

"Kwarai kuwa me zan tsaya jira, tun ina k'arama Allah ya jarabceni da son yaya Sadiq, dan haka lokaci ya yi ba zan bari wata ta kwace min shi ba"

Husna ta yi dariya.

"Haba k'awata akwai sauran lokaci, dan da k'uruciya a tare damu, shekarun mu 17 fa"

"Eh, ai ba yanzu na ce ba, at least nan da shekara d'aya ko biyu za a yi bikin"

"Ok, Allah ya kaimu, amma ni a nawa ra'ayin sai na kammala degree na kan inyi aure, ni totally ban ma san ya so yake ba balle har in fara, ni wallahi Khadija har mamaki kike bani kina kwailarki kin san Soyayya"

Duukan wasa Khadija ta kai mata.

"Eh na ji d'in, ai ba wani nake so ba sai yayana, kin ga kuwa abu ne na family"

"Hakane, yaushe zaki tafi kaduna?"

"Ina ga nan da kwana biyu zamu tafi"

"To Allah ya kaimu"

"Ameen".

Nan suka ta shi suka cigaba da tafiya tare da yin hira gwanin sha'awa har suka kai bakin hanya, suka samu abin hawa duk suka nufa gida cike da kewar juna.

Husna ta isa gida da misalin k'arfe biyar, direct d'aki ta wuce ta watsa ruwa ta sanya bak'ar jallabiya mai d'auke da kwalliyar Golding brown, ta fito falo ta zauna ta kunna TV ta soma tallon tashar Arewa24, Jimmai ce ta fito daga kicin ta ce.

"Au, Husna a she kin dawo shi ne baki ni meni ba?"

"Uhum Mama Jimmai ki yi hakuri, wallahi na gaji sosai kin san yau muka kammala exam d'inmu"

"Hakane to ya jarabawar, da fatan kun gama lafiya, Allah yasa ya fito lafiya"

"Ameen ya rabb, Mama Jimmai wai Dady bai dawo bane?"

"Ya dawo bayan Sallar Juma'a, Sadiq ya shigo sun fita tare, dan shi ne ma ya yi driving d'insu"

"Ok, Allah ya dawo dasu lafiya"

"Ameen, bari na kawo miki fruit salad d'in da na had'a miki"

"Wallahi kamar kin san ina tunanin had'awa yanzu"

Jimmai ta mik'e tare da cewa.

"To bari na mik'o miki, ban ma yi komai ba Dady ya ce kar na yi girki, shiyasa na ce bari na had'a miki dan nasan kina so"

"Gaskiya naji dad'i nagode kwarai"

Bayan ta kawo mata Hunsa soma sha, suna hira tare da kallon TV, Momy ce ta fito falon, duk ta lalace ta rame, bata kalle su ba ta wuce kicin, ta d'auko abin da take buk'ata ta wuce su, suma babu wanda ya kulata harta shige, Husna ce ta ce.

"Ni ko Mama Jimmai ina son yima Momy magana amma ina tsoro"

"Karki kuskura ki soma dan Alhaji ya ja min kunne sosai, dan haka ki adana maganarki"

Daga nan bata kuma cewa komai ba suka cigaba da kalon TV.

Su Dady basu dawo ba sai bayan Sallar Isha'i, sun samu falon ba kowa, Dady ya nufi sashinsa bai ga Husna ba sai ya wuce sashin Jimmai, can ya jiyo hirarsu ya k'arasa cike da farin ciki a fuskarsa ya yi sallama, duk suka amsa masa Husna ta mik'e cike da shagowa ta ce.

"Dady shi ne kuka tafi kuka barni kuma kunsan yau ne na gama exam"

Murmushi ya yi wanda har sai da hak'oransa suka bayyana.

"Haba 'yar lelena kar ki yi kuka, fitan da muka yi dan ke na yi, zo mu je ki gani,Jimmai kema zo mu je"

Nan suka d'unguma gaba d'ayansu suka nufa falo.

Sun samu Sadiq zaune shi kad'ai, nan suka gaisa, duk suka samu guri suka zauna, nan Dady ya fara kiciniyar bud'e wani kwali, katon cake ne ya bayyana wanda ya sha decoration mai d'auke da sunan Husna a kai, cike da farin ciki Husna ta isa wurin cake d'in, tana kallo, Dady ya d'ago tare da yi mata murmushi.

"Wannan cake d'in naki ne, na taya ki murnar gama exam"

Da murna ta rungume Dady tana tsalle, duk suka sa mata da dariya, nan suka taya ta yanka cake d'in, Dady ya yanka ya sa mata a baki, farin ciki ne fal cikinta tana ta dariya wanda ya k'ara bayyana mata kyawunta, duk suna mamakin dama Husna na dariya haka, a takaice dai wani

'yar kwarya kwaryan walima Dady ya shirya mata a wannan dare, sun ci sun sha sunyi hani'an, shima Baba mai gadi ba a barshi a baya ba dan da shi aka ci walima, haka shima Yasir abokin Sadiq ya zo walimar, gasu Inna da Baba Husain sun hallara, sai wani Abokin Dady mai suna Alhaji Ahmad, wurin aikinsu d'aya, shima yazo tare da iyalinsa, matarsa Halima tare da yaransu mata biyu Minal da Kausar, Minal tsarar Husna ce amma ita yanzu take SS2 sai Kausar da take JS3, Husna taji dad'in ganinsu wanda daga nan suka kulla k'awance da Minal.
Momy na cikin d'aki tana jinsu abin duniya ya isheta, tana son fitowa amma tsoro ya hanata. Sai misalin k'arfe goma taron ya washe in da Dady yasa Sadiq ya mai da su Baba Husain gida, Alhaji Ahmad shima ya wuce da iyalensa, Jimmai ta wuce d'aki dan tana so ta kwanta barci yana damunta, daga Dady sai Baba aka bari a falon, Husna ta raka Sadiq kai su Inna gida, Yasir shima tuni ya wuce gida.

Bayan sun dawo daga kai su Inna, Sadiq ya yi parking mota suka fito, har Husna ta wuce shi, sai ya kirata ta dawo ta tsaya.

"My Husna ina taka yi murnar kammala karatunki, Allah ya fiddo sakamako mai kyau"

"Amin uncle"

Sai ya cigaba da cewa.

"Da fatan zaki mai da hankali kan karatunki na islamiya, yanzu saura miki shekara d'aya ki yi saukan Al-Qur'ani"

Insha Allah zan mai da hankali"

Sai ya mik'a mata wani leda mai d'auke da kwali a ciki.

"Wannan shi ne kyaunarki da fatan zai saki farin ciki"

Cike da murna ta amsa tare da cewa.

"Uncle meye a ciki?"

Sadiq ya yi mata hararan wasa.

"In kin shiga ciki kya gani"

"Nagode uncle Allah ya kara bud'i"

Ta ce cike da tsantsar farin ciki.

"Ameen Husna, kuma godiyar ya isa haka, mu shiga ciki"

[10/30, 7:13 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 45 ~ 46_*

Suna shiga falo ta mik'awa Dady kyautar da sadiq ya bata, ya amsa tare da tambayarta.

"Meye a ciki, na waye?"

Dubanta ta kai ga Sadiq wanda yana kallonsu yana murmushi, ta ce.

"Uncle ne ya bani kyautar gama exam"

Murmushi Dady ya yi mai kayatarwa.

"Madallah, Allah ya saka da Alkhairi ya muku Albarka, shiga ciki ki bud'e abin ki"

Amsa ta yi ta wuce d'aki cike da murna fal cikinta.

Baba mai gadi ya mik'e yama su Dady sai da safe ya koma bakin aikinsa, falon ya rage daga Dady sai Sadiq, Dady ya gyara zamansa a k'asan carpet d'in falon ya jingina da jikin kujera ya yi gyaran munya.

"Sadiq matsonan ina son magana da kai"

Cikin ladabi ya matsa kusa da shi ya risina, Dady ya cigaba da cewa.

"Sadiq nagode da duk irin d'awainiyar da kake yi da mu, Allah ya saka maka da Alkhairi ya yi maka Albarka"

"Ameen Dady"

"Yauwa, ina son mu yi wata magana ce mai mahimmanci"

Nan Sadiq ya kara tattaro duk natsuwarsa ya gyara zama.

"Ina so ka gaya min meya ke tsakanin ka da Husna?"

Cike da mamaki Sadiq ya d'ago kai ya ce.

"Babu komai Dady, duk abin da nakewa Husna ina mata ne matsayin kanwata ta jini, banda wannan babu wani abu a tsakanin mu"

Dady ya girgiza kai alamar gamsuwa.

"Na fahimta! Sadiq gaskiya na zauna na yi tunani da nazari a kan abin da ya kamata na biya ka

bisa k'ok'arin da ka yi da Husna a lokacin da ta rasa gata, ka tallabi rayuwarta ka zame mata Uwa da Uba, abin da na yanke zan yi maka shi ne  na baka Husna ka aureta in har kana son ta"

Cikin razana Sadiq ya d'ago fuska su ka yi ido hud'u da Dady, bugun zuciyarsa ya k'aru tare da tsananin rud'ewa, dan bai tab'a tunanin wannan maganar daga gunsa ba.

'Son da yakewa Husna bai wuce na 'Yar Uwarsa ba, bai tab'a kawo aure tsakaninsu ba, kuma Husna ma k'arama ce yanzu, shi da ya da shekara talatin da daya ya bata kusan shekaru sha hudu, ya hakan zai yuwu?'

Duk wannan maganar a zuciyarsa yake karanto su. Shurun da ya yi na tsayin lokaci bai ce komai ba, shi ne ya tabbatarwa Dady Sadiq tunani yake yi, Dady ya gyara zama ya ce.

"Sadiq ka kwantar da hankalinka, in har ba kada ra'ayi zan jenye k'udirina akan ka, dalilin da yasa na zab'eka ka zama sirikina, ba komai bane face, kai yaron kwarai ne kuma mai tausayi da taimako ga kuma biyayya, ka had'a qualities da duk wani Uba zai gani yaso ya had'a zuri'a da kai, Husna yarinya ce kuma tana buk'atar taimakonka, sannan akwai shak'uwa mai k'arfi a tsakaninku, na aminta da kai Sadiq, na san zaka kula da Husna ko bayan bani a doran k'asa, kai mutum ne mai amana"

Dady yaja numfashi ya cigaba da cewa.

"Na baka nan da sati d'aya kaje ka yi tunani, duk abin da ka yanke sai ka sanar min, bana so ka zurfafa tunani, kuma karka b'oye min duk abin da ka yanke, zaka iya tashi ka tafi"

Cike da sanyin jiki Sadiq ya ce.

"Dady na d'auke ka mahaifi agare ni kuma ba zan iya jayayya da kai ba, batun inje inyi tunani bai taso ba, na amince na amshi tayin ka zan auri Husna kuma insha Allah zan rik'eta Amana, Dady na d'auki Husna 'yar uwa a gareni ba zan juya mata baya ba"

Ya k'arasa maganar zufa na keto masa, yana jin wani yanayi a zuciyarsa, wanda bai iya tantance murna ne ko damuwa. Cike da gamsuwa da farin ciki Dady ya ce.

"Nagode Sadiq, Allah ya saka maka da alkhairi da gidan Aljanna, yanzu sai kaje ka zanta da Iyayenka ka turo su, ina ganin ba zamu d'auki lokaci ba dan ba wani bikin kud'i za muyi ba, ina son Husna ta cigaba da karatu a d'akinta"

"Ameen Dady, nima nagode Allah ya k'ara girma, Insha Allah zan sanar da Iyayena, duk yanda muka yi dasu zan sanar maka, kuma maganar karatun Husna zata cigaba da yi Insha Allah."

"Nagode Sadiq, banda bakin gode maka sai dai in ce Allah yasa ka gama da gidan duniya lafiya"

Ya amsa da Ameen tare da mik'ewa su ka yiwa juna sai da safe sannan ya wuce gida.

Cike da farin ciki Dady ya wuce d'akinsa, ya samu Husna har ta yi barci ya shiga ya watsa ruwa kana ya gabatar da Sallan Nafila, sannan ya kwanta cike da farin ciki.

****** ******

*Washe gari*

Da misalin k'arfe goma na safe, Husna ce zaune a falo tana ta danna wayar da Sadiq ya bata a matsayin gift, wanda tun dare ta sanyata a chargy ta yi full, yau fuskarta kamar gonar auduga, d'auke yake da murmushi wanda har hak'oranta na fitowa, number Khadija take dannawa a wayar wanda jiya ta amsa a gunta, bugu biyu ta d'auka cike da murna Husna ta ce.

"Khadija, Husnah ce ke magana"

A d'ayan b'agaren ta ce.

"Laaa, wannan ne number Dady d'in?"

"Hmmm ba ita bace, wannan wayata ce"

Nan ta shiga bata labarin abin da ya faru jiya, Khadija cike da murna ta ce.

"Wallahi na taya ki murna gaskiya, Uncle d'inki yana ji dake"

Nan dai suka yi ta hira, daga bisani Khadija ta kuma cewa.

"Kin san kuwa yau zamu wuce Kaduna tare da yaya Sadiq, Abbana ya kira shi zai kaimu"

"Iyen ba, ashe zaku sha soyayya a hanya"

"Hhhh, ban son sharri fa, ki mana Addu'a kawai"

"To Allah ya kaiku lafiya"

"Ameen, nagode muna isa zan kira ki"

"To sh ikenan"

Nan su ka yi sallama suka aje kan wayar.

*
Sadiq ya wuce gidan yaya Ismail, nan ya yi breakfast kana ya d'auki su Anty Amina suka wuce Kaduna.

*********

*KADUNA*

Bayan sun isa, gida ya had'e da dangi kamar dama su ake jira, nan duk suka gaisa Sadiq ya wuce part d'in Anty Zainab dan bai ganta a falo ba, ilai kuwa ya sameta ta idar da sallar Azahar, nan ya zauna suka gaisa suka d'anyi hira kana ya wuce d'akinsa dan ya watsa ruwa tare da gabatar da sallar azahar wanda ya riskesu a hanya basu tsaya yi ba.

Da dare Sadiq ya samu Amminsa a d'aki tana karanta wani littafi na Addini, zama ya yi a k'asa ya gaisheta ta amsa, nan dai ya yi shuru bai kuma magana ba, can dai Ammi da ta ga yanayinsa akwai magana a bakinsa, sai ta ajiye littafin ta mai da hankalinta gare shi ta ce.

"Da fatan lafiya ko?"

Ya gyara zamansa ya sunkuyar da kai k'asa ya ce.

"Ummm dama wani magana nazo mu yi a kan yarinyar da dana ke nema?"

Cike da murmushi a fuskar ta ce.

"Au khadija ko?"

Nan ya kuma duk'ar da kai ya ce.

"A'a, ba ita bace, wannan a Kano take kuma mak'ota muke, mahaifinta ya nima dana tura magabata na, domin a fara maganar aure, wannan shekaran ta kammala jarabarta na waec, to shi ne mahaifinta ya ce na turo, bayan anyi auren sai ta cigaba da karatu"

Nan da nan fuskar Ammi ya sauya, cike da b'acin rai ta ce.

"Wato so kake ka watsa mana k'asa a ido ko? ita kuma zancen Khadija mu yi yaya da shi? wanda kasan iyayenka sun gama magana akai"

D'agowa ya yi cike da mamaki a fuskarsa.

"Ammi yaushe akai haka? ni fa sam bance ina son Khajija ba, ni ban san ma da wannan zancen

ba"

"Eh ai dole ka ce haka saboda ka zama mara kunya, to ka bud'e kunnen ka kaji, babu wata wanda zaka aura face Khadija kaji na gaya maka, ka koma kaje ka samu Baban yarinyar ka ce an maka mata dan ba zaka mai damu mutanan banza ba"

Wani gumi ne ya karyowa Sadiq, bai tab'a kawo cewa zai samu matsala gun iyayensa ba.

"Ammi dan Allah ki yi hakuri, ni bana son Khadija ku barni na auri wacce nake so"

"Dalla rufe min baki ni zaka gayawa haka, ta shi ka bani wuri mutumin wofi kawai, to bari kaji karka yarda Abbanka yasan da wannan maganar dan ranka zai yi nugun b'aci"

*Cakwakiya*😊
[10/31, 7:57 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 47 ~ 48_*

Jikin Sadiq ya yi matuk'ar sanyi haka ya mik'e tare da rashin kuzari, cikin dishewar murya ya ce mata sai da safe sannan ya fita daga d'akin, Ammi ta bisa da kallo babu alamar tausayi a fuskarta. D'akin Anty Zainab ya nufa, idonsa ya yi ja saboda b'acin rai, ya sameta tana kallo a TV, yanayin data ganshi zuciyarta ta shaida mata akwai matsala, zama ta gyara ta rage sautin tv, ta kalle shi cikin natsuwa.

"Sadiq yafiya kuwa?"

Sunkuyar da kansa ya yi k'asa.

"Anty wata magana naji wai za'a aura min Khadija, Wanda ni ban san da zancen ba"

Cike da mamaki ta kalle shi.

"To dama ba soyayya kuke yi ba wasan yara ne?"

Ta k'arasa maganar da zaulaya, Sadiq ya muskuta ya gyara zamansa.

"Wallahi Anty ko maganar kirki banyi da yarinyar nan, sam jinina bai had'u na nata ba, ita ce dai take ta haukarta"

"Tafd'i jam, mu da har mun fara shirin biki"

Ta yi maganar tana dariya, Sadiq ya k'ara d'aure fuska.

"Anty dan Allah ki bar wannan wasan, na zo ki bani shawara ne kan wata magana"

Zainab ta gyara zamanta.

"To ina jinka"

Nan Sadiq ya shiga bata labarin maganar auren sa da Husna kamar yadda ya korowa Ammi labari, ya d'aura da yadda suka kwashe da Ammi, ya k'arasa maganar kwalla sun taru masa a ido kamar zasu zubo, jikin Anty Zainab taji ya yi sanyi saboda tunawa da ta yi da soyayyarta da Khalil, ta san so tsartse ne mai zuwan bazata, kuma mai wahalan sha'ani, a yadda ta d'auka Sadiq na mugun son yarinyar ne sosai, ta gyara murya.

"Sadiq ka yi hakuri,  shawaran da zan baka ba lallai ta yi maka dad'i ba, ka daure ka yiwa mahaifiyarka biyayya domin hakan zai maka amfani nan gaba, duk abin da aka ce iyaye tofa an gaba komai, ja dasu masifa ce, kaje ka dage da addu'a da niman zab'in Allah, insha Allah zaka samu mafita, amma duk da haka zanje na samu Anty Jiddan muyi magana akai tunda baka son Khadija, sai a aura maka wacce kake so, ana yiwa mace auren dole ta zauna amma baga namiji ba, dan haka ka kwantar da hankalinka Insha Allah komai zai yi dai-dai, karma ka yi gaggawan gayawa mahaifin yarinyan zancen ka fasa, ka k'ara lokaci tukuna muga hukuncin da Allah zai yanke"

"To shi kenan Anty nagode sosai, har na d'an ji natsuwa kad'an"

Khadija ce tsaye k'ofar d'akin Anty Zainab wacce ta daskare tun shigar Sadiq ciki. Tunda ta hongoshi ya shiga, da saurinta ta k'araso dan ta cimmasa a d'akin sai kawai ta tsinkayi bayanin Sadiq, nan ta yi kasake tana sauraron maganar da suke yi, hawaye ya gama wanke mata fuska, zuciyarta na bugawa da sauri da sauri. Motsin da taji ne kamar za a fito yasa ta yi sauri ta shige cikin kicin dake falo ta goge fuskarta, ta tsaya na mintuna. Sadiq ya yiwa Anty Zainab sai da safe sannan ya wuce d'akinsa cike da tunani barkatai.

Khadija na fitowa ta wuce d'akin Anty Jidda ta same su a falo zaune da Abban Sadiq, suna zaune da alama hira suke yi, ganinta suka yi tsalam a firgice ta fad'a jikin Ammi ta sanya kuka mai tsuma zuciya, hankinsu ya yi matuk'ar tashi nan Ammi ta fara tambayar ta.

"Khadija lafiya, me aka miki?"

Cikin matsanan cin kuka ta soma magana.

"Ammi Yaya Sadiq ya ce baya sona ba zai aureni ba, na shiga uku Ammi ki taimaka karya rabu dani"

Cike da mamaki Ammi ta ce.
"Yaushe kuka yi hakan da shi?"

"Yanzu naji yana gayawa Antynmu a d'aki, wai har tana cewa ba za a ba shi ni ba tunda bai sona"

Nan dai ta yi ta zuba musu wauta da k'uruciya.
A fusace Abba ya mik'e ya fice, bai zame ko ina ba sai d'akin Anty Zainab, yana huci ya soma masifa.

"Wato saboda ke kin isa, kin iya bijirewa iyayenki shi ne zaki goyi bayan Sadiq ya bujire mana, kina so ki d'aurashi bisa mugun halinki da kika yi a baya ko?"

Cike da tashin hankali Anty Zainab ta mik'e.

"Yaya Aliyu lafiya? meya faruwa?"

Hannu yasa ya wanketa da mari ta dafe kuncinta, bai kuma cewa komai ba ya fice daga d'akin a fusace. Falo ya isa ya shiga kwalawa Sadiq kira kamar saukan aradu, cikin kankanin lokaci duk mutanan gidan suka fito a gigice, suna tambayar lafiya, Baffa da Umma, Ammi tare da Khadija duk sun bayyana a falon, haka ita ma Anty Amina da suke kira da Mami ta fito a sittin daga part d'inta duk tunanin ta ko wani abu ne ya faru, Sadiq shima a sukwane ya k'araso falon domin kiran ya yi matukar tsorata shi, tunaninsa ko wanin babban matsala ne ya auku, ganin kowa a tsaye sunyi cirko-cirko, hakan yasa Sadiq ya samu d'an nutsuwa sai ya k'arasa wurin Abbansa ya ce.

"Abba gani"

Saukar mari yaji a fuskarsa wanda Abban ya mare shi yana cewa.

"Wallahi baka isa ka raba mana zumuncin mu ba, ka yi kad'an karya kake, mu kake niman watsawa k'asa a ido"

"Wai lafiya me yake faruwa ne?"

Cewar Umma, Baffa shima ya ce.

"Aliyu wai lafiya kuwa?"

Sai ya yi musu umarni da duk kowa ya zauna, duk suka samu guri suka zauna, Baffa ya kai dubansa ga yaya Aliyu.

"To yanzu sai ku gaya mana abin da ke faruwa"

Ammi ta soma bayanin abin da Sadiq ya gaya mata d'azun, ta d'aura da cewa.

"Sai da naja masa kunne na gargad'e shi, domin munyi ni da shi mun rufe magana, ashe hakan bai masa ba shi ne yaje ya samu Zainab ya gaya mata, ashe ita kuma Khadija ta jisu, shi ne ta same mu muna zaune ta isa da kuka take gaya mana, kuma wallahi na yi niyyar ko shi yaya Aliyu ba zai ji wannan maganar ba domin mun rufeta, ashe shi ba haka bane a gunsa"

Anty Zainab ce ta fito idonta sunyi jajir saboda tsabar kuka, wuri ta samu ta zauna ta koro bayanin yanda suka yi da Sadiq, ta d'aura da cewa.

"Hak'ik'a nasan ina da tabo a zuciyarku, tabbas na yi ganganci dana yi k'ok'arin shiga maganar, insha Allah daga yau ba zan sake cewa komai ba akai, iya ka in ce Allah ya sanya Alkhairi, insha Allah ba zan zama silar rabuwar dangi na ba"

Ta k'arasa maganar tana kuka. Cikin fusata yaya Aliyu ya ce.

"Ai gwara ki janye bakinki daga cikin maganar, domin kina da record wanda bamu fatan sake samun irinsa"

Cikin b'acin rai Umma ta ce.

"Aliyu lafiyarka kuwa? k'anuwarka kake gayawa haka, wannan maganar bata wuce ba, meyasa zaka mai do hannun agogo baya, sannan ka manta a gaban yara kake fadar wannan maganan, haba in hankali ya gushe hankali ke nemo shi"

Sadiq ji ya yi duniyar ta yi masa zafi, damuwa ya gama baibaye zuciyansa, sun sanya shi cikin rud'ani akan maganarsu, hawaye yaji yana zuba masa, ya kasa furta komai. Anty Zainab cikin kuka mai tsuma zuciya ta mik'e ta isa d'akinta, hak'ik'a yau yaya Aliyu ya tado mata da tsohon mikinta, tana cewa cikin kuka.

"Yau ga rashin bin iyaye abin da ya jawo min cin fuska da wukalanci, hakaki na tafka kuskure, ko yaushe zasu gane ba laifi na ba, wannan rubutaccen kaddara ce wanda ban isa na goge shi ba"

Sai ta fada gadonta tana rusa kuka mai tsuma zuciya.

A falo, Mami ta mik'e cikin fushi ta jawo Khadija, mari lafiyayye ta zuba mata guda biyu ta kuma rufeta da duka. Ammi ce cikin fushi ta kwaceta tana cewa.

"Meye haka kuma Ameena? ya ana k'ok'arin gyara ke kuka kina hukunci?"

"Haba Anty Jidda wannan yarinyar duk ita ce musabbabin wannan tashin hankalin, a cikin daren nan ta hargitsa mana gida, ina so sai ta gaya min in da ta koyo had'a munafinci tunda ban koyar da ita haka ba"

Umma ne ta taso ta ce.

"Aminatu karki sake dukanta, in da ba ayi hakan ba tayaya zamu san halin da ake ciki, ba duka ya kamata ki yi ba Addu'a da nasiha zaki yi mata, tunda Khadija ta mallaki hankalinta, ta wuce duka"

Nan Baffa ya yi umarni da duk su zauna. Ta b'angaren Sadiq kuwa ya ji dad'in abin da Mami ta yiwa Khadija domin ta cancanci hukunci, Kuma shima yana nan ya yi mata tanadin hukunci kan munafircin da ta had'a. Baffa ya ce su Sadiq su basu wuri, haka ya mik'e jiki ba kwari ya wuce d'akinsa, Khadija wacce hawaye keta malala a fuskarta ita ma ta mik'e ta wuce jiki ba kwari ta nufi part d'in Ammi, domin yau ba zata iya kwana d'akin Anty Zainab ba, dan ita ce ta had'a wannan rigima, dana sani ne ya cika mata zuciya tana fad'an.

"in da nasan haka zai faru da na rik'e maganar a zuciyata na yi hakuri"

Sadiq yana isa d'aki ya duba agogon dake manne jikin bagon d'akin, yaga k'arfe tara da kwata na dare, jakar daya tawo da shi ya d'auka tare da key d'in motarsa, fita ya yi ta baya, ya yiwa mai gadi magana ya bud'e masa gate, ya cilla jakar a seat d'in baya, ya shiga mota kan kace meye ya figi mota a guje, su Baffa k'ugin motarsa suka ji kan suyi yunkurin fitowa ya fice, ya kama hangar Kano cikin wannan dare.

*To masu karatu sai mu had'u musa Sadiq a Addu'a Allah ya sauke shi lafiya*
[10/31, 7:16 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 49 ~ 50_*

Baffa ya d'auki wayarsa ya danna number Sadiq bugu biyu ya d'auka, kan ya ce wani abu Baffa ya soma magana.

"Kai Sadiq ina zaka cikin daren nan?"

"Baffa zan koma Kano ne Addu'atku nake nima sai na dawo"

Bai jira mai Baffa zai ce ba ya kashe wayar gaba d'aya ya jefata kan seat d'in dake gefensa, ya k'arawa mota wuta.

Baffa ya cire wayar a kunne ya bita da kallo, daga bisani ya nisa tare da ajiyeta, ya kai dubansa ga Abba Aliyu.

"Kunga irin abin da ake gudu, to Kano ya tafi cikin daren nan"

Abbansa cikin fushi ya ce.

"Yafi ruwa gudu, kuma ba zamu tab'a sauya k'udirinmu ba, aure ne ba fashi"

Ammi ji ta yi ba dad'i domin ta san Sadiq yana k'ok'arin yi musu biyayya, haka nan taji basu yi masa adalci ba, Mami Ameena ta ce.

"Ba zai yuwu ba tunda bai son Khadija to a bar shi ya auri wacce yake so"

"Ku dakata, yanzu dai za a bi komai a hankali, sannan tunda ya nuna bai so to lallaba shi ya kamata ayi, kuma yanzu ita Khadija karatu zata yi kunga kila sai nan da shekara biyu kan ayi maganar auren, inya so kila lokacin sun dai-daita kansu, kuma ina da tabbacin Sadiqu ba zai bijire da auren Khadija ba dan yaro ne mai biyayya, dan haka magana ta wuce, Addu'a za mu bisu da shi, Allah ya tabbatar da abin da yake Alkhairi"

Cewar Baffa, duk suka amsa da Ameen. Baffa ya kai dubansa ga yaya Aliyu.

"kai Aliyu ka ta shi kaje ka bawa 'yar uwarka Zainab hakuri dan baka kyauta ba, magana ya k'are bana so a kuma tadata, zaku iya tafiya"

Haka kowanne ya wuce part d'insa cike da damuwa, Abba Aliyu ya wuce d'akin Zainab ya same ta gefen gado ta rafka uban tagumi, zama ya yi a kujera nesa da ita ya soma bata hakuri da lallashi, cikin k'ank'anin lokaci ta sauko suka shirya, harda yi mata alkawarin zai canza mata mota, da haka ne yasa Anty Zainab ta soma murmushi nan ya yi mata sallama ya wuce cike da dana sanin abin da ya yi mata, sai yanzu da hankalinsa ya dawo jikinsa ne yaji bai kyauta mata ba. A can kasan zuciyar Zainab kuka take yi na kuskuren data aikata, wanda ya zama har yanzu ana goranta mata.

******

Sadiq gudu yake yi  kamar zai tashi sama, da yake cikin dare ne ba motoci sai tsiraru, zuciyarsa ta yi masa k'unci tare da tunani barkatai, mafita kawai yake nima domin dole ya hakura da auren Husna in dai yana son zaman lafiyan familynsa, da wannan tunani ya isa garin Kano da misalin k'arfe sha daya da rabi na dare, gidan su 'Yasir ya nufa, wayarsa ya d'auka ya kunna tare da danna number Yasir. Yasir yana barci sai yaji kiran wayarsa kamar daga sama, ya mirgina ya d'auki wayar ganin mai kiransa ne yasa ya murza idon don ya tabbatar da ba mafarki bane, saura k'iris kiran ya tsinke ya yi sauri ya d'auka tare da kara shi a kunensa ya ce.

"Hello! Sadiq ya a ka yi ne?"

Cikin dishewar murya Sadiq ya ce

"Ka fito ka yiwa mai gadinku magana ya bud'e min gate gani a k'ofar gidanku"

Cikin sauri ya mik'e tare da cewa ok, kana suka tsinke wayar. Yasir ya fito ya samu mai gadi ya yi masa magana cikin minti biyar Sadiq ya shigo ya yi parking, jakan kayansa ya d'auka sai waya, sannan ya kulle motan ya kalli in da Yasir ya tsaya.

"muje ko"

Shi dai Yasir mamaki ya hana shi magana sai kawai ya yi gaba Sadiq na binsa a baya har suka isa cikin d'akinsa, kana ya rufe k'ofa. Direct ba yi Sadiq ya nufa ya watsa ruwa kana ya fito d'aure da tawul, Yasir ya mik'e ya ciro masa sabuwan jallabiya wanda bai taba amfani da shi ba ya mik'awa Sadiq, ya amsa ya zira tare da ya kammala shirin barci, ya fad'a kan k'atuwar katifar da aka kwantar a k'asa, Sadiq ya rufe ido kamar mai barci, haushi ne ya fara kama Yasir domin miskilancin Sadiq wani lokacin yana ba shi haushi, a k'ufule ya ce

"Malam ka zo ka kwanta, kak'i yi min bayani sai wani cin magani kake yi, wai me yake faruwa ne? Kar dai daga Kaduna kake cikin daren nan?"

Tsaki Sadiq ya yi.

"Kai Malam ka kwanta ka yi kwanciyanka, ka barni naji da abin da ke damuna"

Shima Yasir tsaki ya saki.

"Ka cigaba da barin magana a cikin ka, wata rana sai ya kashe ka"

Sadiq bai tanka masa ba, haka suka kwanta kowa da irin abin da yake sak'awa a zuciya, har barci ya yi baga da su.

******     ******

*Washe gari*

*Kaduna*

Gidan duk sun tashi cikin walwala kamar babu abin da ya faru, Khadija ta isa d'akin Maminta, ta same ta zaune kan dinning tana karyawa, ta risina ta gaidata, Mami ta amsa kamar babu komai, sai da ta kammla kana ta mik'e ta koma falo ta zauna a cushing, Khadija tabi bayanta ta samu k'asan carpet ta zauna kanta na sunkuye ta ce.

"Mimina ki yafe min, wallahi sharrin shaid'an ne ya jani, amma ba zan k'ara ba"

Mimi ta yi ajiyar zuciya.

"Babu komai Khadija, ni dai ina k'ara jan kunnenki, ki rik'a yin gaskiya kuma kin san lab'e babu kyau, domin halin munafukai ne, sannan ina so kije ki samu Antynku Zainab ki bata hakuri"

Nan dai ta yi ta mata fad'a da nasiha, bayan sun gama magana Mami ta ce.

"Tashi kije ki kwashe kayan dining, ki shiga kicin ki gyara min shi"

Khadija ta mik'e tare da cewa to kana ta wuce.

Khadija ta samu Anty Zainab a d'aki, nan suka gaisa sannan ta bata hakuri, Anty Zainab ta nuna mata babu komai nan ita ma ta yi mata nasiha, tare da nuna mata illar nunuwa namiji so irin haka, tabi komai a hankali in Sadiq mijinta ne zata aure shi, nan dai ta yi ta mata bayani har Khadija ta saki jiki suka cigaba da hira kamar wani abu bai faru ba. Anty Zainab kenan tana da sanyin hali ba tada gaba ko tsananta fushi, kowa nata ne, hakan ne yasa ta saba da yaran 'yan uwanta domin tana sakin musu fuska sosai, sannan babu raini tsakaninsu.

*****        *****

*Kano*

Sadiq bai farka barci ba tunda ya koma bayan sallah asubahi sai goma na safe ya tashi, Yasir na zaune bisa kujera yana aiki a computer, Sadiq ya mik'e ya shiga bayi, wanka ya yi ya fito ya shirya cikin riga da wando k'ananun kaya, ya yi kyau sai dai fuskarsa babu walwala, har wani d'an rama ya yi, ya samu gefen Yasir ya zauna, shuru ya yi Yasir ya waigo suka had'a ido sai ya kauda shurun da cewa.

"Alhaji ina kwana? tunda naga azumin magana kake yi"

Sadiq ya wurga masa harara ya amsa a dak'ile.

"Lafiya"

"To ga breakfast d'inka can dan ni na ci nawa, Momy ta aiko mana da shi dan na sanar mata da zuwanka, in ka kammala sai muje mu gaisheta"

Ok kawai ya ce masa ya matsa wurin daninng, ya bud'e kulan soyayyat irish ne da plantain sai kuma kunun gyada, da yake yana son kunun gyada, sai ya zuba a cup ya soma sha yana cin plantain, bai ci irish ba saboda bai dame shi ba. Bayan ya gama suka isa falon Momyn Yasir, suka gaisa kana suka koma d'aki, Momyn Yasir ta yi murna da ganin Sadiq domin da ganin sa ta shaida natsuwarsa, hakan zai sa Yasir ya natsu ya rabu da tarkacen abokansa danta sanshi da jaye-jaye, tunda yake bata labarin Sadiq ta ji ya kwanta mata a rai, domin taga sauyin wasu halayyansa akan yawo da kuma niman matan da yake yi, hakan ya tabbatar mata Abota da Sadiq Alkhairi ne ga Yasir.

A d'akin Yasir kuwa haka suka zauna jugum-jugum, Sadiq ba yi da niyyar komawa gida. Da yake ranar lahadi ne, Sadiq ya koma ya kwanta abinsa sallah kad'ai yake tada shi.

Da dare suna zaune sun gama cin tuwon da Momy ta aiko musu da shi, suna kallon wani series film, Sadiq ya ce.

"Yasir ina so zamu yi magana"

Cike da mamaki Yasir ya juyo ya kalle shi.

"Na'am magana kake yi ne?"

"Van sani ba"

Sadiq ya mai da masa da martani cike da jin haushi. Yasir ya ce.

"Mai da wuk'ar, dan naga tun jiya kake fusge-fusge"

Sadiq ya yi murumushi gefen baki.

"Malam Bana son sharri, in zaka rage volume ka rage mu yi magana, in kuma baka shirya ba sai ka sanar min"

Yasir ya kwanshe da dariya.

"Ni ko na shirya, dan kunnena har sun fara min k'aik'ayi"

Murmushi Sadiq ya yi domin inya biyewa Yasir sai sun d'auki lokaci yana zuba masa shirme, shurun da yaji Sadiq ya yi shi ne yasa shi rage volume d'in TV kana ya gyara zama ya ce

"Ina sauraronka"

"Yau zan baka labari na kamar yanda kake ta son na gaya maka a baya, inna gama baka labarin, daga k'arshe sai ka bani shawara dan in samu mafita"

Nan Yasir ya natsu ya aje wasa tare da bama Sadiq hankalinsa. Sadiq ya shiga ba shi labarinsa, da labarin farkon had'uwansa da Husna, da yadda mahaifinta ya ba shi ita ya aura, sannan da irin rigimar da suka kwasa jiya a gidansu har ya zuwa dawowansa Kano. Ya nisa tare da hura iska mai zafi da bakinsa, damuwa fal a fuskansa, hawaye sun cika masa ido wanda kad'an yake jira ya sauko, jikin Yasir ya yi sanyi ya kuma jinjina lamarin ya ce.

"Yanzu kai ka amince da ka fasa auren Husna bayan da kai ta dace, ta ginu akan tarbiyyarka ka zame mata komai, wallahi da da farko na d'auka 'yar uwarka ce, sai a ranar da mahaifinta ya nuna baima sanka ba, wannan ya bani cewa akwai wani b'oyayyen Al'amari a tare da kai da Husna"

Sadiq ya nisa.

"Hakane, ga shi kuma yau na warware maka komai, kasan waye ni, dan haka sai ka bani shawara"

*wani shawara Yasir zai ba ma Sadiq?*
[11/1, 8:12 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 51 ~ 52_*

Yasir ya nisa ya ce.

"Ni ina ganin Sadiq kar ka yi saurin yanke hukunci, sai mu yi Addu'a, mu d'an bada lokaci, sai ka koma wurin iyayenka da maganar sai mu ji me zasu ce"

"Hmmm Yasir kenan, baka san Familyna ba akwai naci da kafiya,  ina ganin zanyi musu biyayya, dama ba son Husna nake yi ba, tausayinta nake yi da kuma ganin girman Dadynta, kawai zan masa bayanin cewa a gidanmu an bani mata"

Yasir ya yi murmushi ya ce.

"Kai yanzu Sadiq har zuciyanka baka jin son Husna? ni fa ban yarda cewa tausayinta ne kawai yasa zaka aurenta ba"

"Yasir ka yarda dani, banda tausayi babu abin da nake ji game da ita"

"Hmmm"

Yasir ne ya yi ajiyar zuciya a ransa ya ce.

'Wannan Guy d'in akwai shegen zurfin ciki, amma na san ta in da zan bida shi'

Yasir ya gyara zama ya ce.

"Kasan meye Sadiq? ina ganin tunda ni ina son Husna, dan tun ranar dana ganta naji ta kwanta min arai me zai hana muje wurin Dady ka nuna ni a matsayin wanda ka barmawa ya auri Husna"

Wani kallo Sadiq ya yi masa mai cike da tuhuma.

"Ba kada natsuwa, sannan ban yarda da kai ba, saboda kana da son mata, ba lallai na gane da gaske kake son Husna ba, dan haka bata dace da kai ba. Koda zan bada Husna sai wanda na tabbatar da halinsa tare da natsuwarsa kana na amince, Malam ka canza shawara wannan bata yi ba"

Murmushi Yasir ya yi a ransa.

'D'an rainin wayo, kana son yarinya kana wani dojewa'

A fili kuma ya ce.

"Allah abokina dagaske nake, zaka je wurin Dady ka nuna masa iyayenka sun amince, ni kuma zan je na samu Kawuna Sulaiman na gaya masa sai yaje ya nima min aurenta matsayin kai ne, in yaso sai kawun yama Dady bayanin ni ya nimawa aure ba kai ba, na san Dady ba zai musa ba illa kawai ya kira ka dan yaji dagaske haka ne, kai kuma sai ka nuna masa ka hakura ka bar mini saboda ni na nuna ina son ta kuma ka yaba da halina, kaga sai a d'aura dani"

Shuru Sadiq ya yi yana nazarin maganan Yasir, bugun zuciyarsa ya k'aru zufa ne ya keto masa duk sanyin dake cikin d'akin, amma bai hana shi zufa ba, Yasir ya ce.

"Kayi shuru? kafa tuna ka ce zaka cewa Dady iyayenka sun ki amincewa, to da kace masa haka gwara muyi hakan, kaga Dady ba zai ce ka watsa masa k'asa a ido ba, kuma zai gane bawai iyayenka bane suka k'i auren ba"

Sadiq ya yi ajiyar zuciya ya ce.

"Hakane, ka kawo shawara mai kyau"

Yasir ya yi murmushin jin dad'i ya ce.

"To ka amince kenan?"

"Eh, na amince, amma da sharad'in zaka rik'e Husna amana"

"Abokina karka samu damuwa, wallahi ina son Husna kuma zan rik'e maka ita amana, kafa san halina fa"

Wani irin damuwa ne ya ziyarci Sadiq, zuciyarsa na gargad'insa, amma babu yadda zai yi domin hakan ne mafita, Yasir ya karanci halin da Abokinsa ya shiga amma sai ya basar kamar bai kula ba, nan suka cigaba da tattaunawa daga bisani suka yi shirin barci suka kwanta.

********

*WAYE YASIR?*

_*Yasir Muhammad Auwal*_
D'a ne ga Alh. Auwal, wanda Allah ya yiwa rasuwa tun Yasir yana secondary school, Alh. Auwal

d'an kasuwa ne, yana saida atamfofi da yadika. Asalinsu mutanan garin Kano ne, mahaifiyarsa Haj. Aisha, yaransu uku duk maza, Yasir ne babba sai Aliyu mai bi masa sai autansu Umar Faruq, tunda mahaifinsu ya rasu Abokan Baban suka rik'e Amanar dukiyansu, da Yasir ya girma suka danka masa ya cigaba da business da gadonsu, sannan bayan ya gama karutunsa na engineering anan BUK, ya gama service, sai ya samu aiki a ma'aikatar matatan man fetur, inda a nan ne suka had'u da Sadiq suka k'ulla abota, tun Sadiq na ja baya da shi har ya saki jiki suka zama abokai sosai. Yasir mutum ne mai barkwanci da son mutane, matsala d'aya gare shi son mata, da yaga mace zai nuna yana so hakan yasa Sadiq yake masa fad'a, wanda a yanzu ya soma natsuwa, sannan ya rabu da abokansa na shashanci, ya sakesu ya kama Sadiq shi kad'ai, sai sauren tsiraru da yake mutunci dasu. Yasir yana da kyau dai dai gwargwado, ya iya wanka, wankan tarwad'a ne, yana da tsayi dai dai misali, yanada idanu sai dai bayi da tsayin hanci sosai, V face gare shi mai dauke da baki dan dai dai. A takaice dai shima yana da nasa kyau d'in, amma fa bai kama k'afar Sadiq ba.

_Wannan kenan._
******

Cigaban labari.

*Bayan kwana biyar*

Sadiq yana gidansu Yasir ya kasa komawa gidansa, tare suke zuwa aiki su dawo, d'an zaman da Sadiq ya yi da Yasir ya k'ara fahimtan hayayyarsa, mutum na mai kirki da barkwanci, nan da nan yaji ya k'ara kwanta masa yaji ya kara amincewa da ya auri Husna.

Ranar Juma'a sun dawo daga masallaci sunci abinci Sadiq ya shirya zuwa gidansa, Yasir ya ce.

"Ni kam da ka saki gidan cen ka dawo nan mu cigaba da zama tare, ni fa yanzu ka tashi a abokina ka koma d'an uwa na kuma Aminina"

Murmushi Sadiq ya masa, dan shima kansa zai so ya cigaba da zama da Yasir, dan yana deb'e masa kewan damuwarsa, amma ya zama dole ya koma makwancinsa, ya nisa ya ce.

"Kai mai zai hana muje kamin sati a gidana"

Yasir ba musu ya mik'e ya shiga shirya kayansa a trolley, mamaki ne ya cika Sadiq.

"Kai baka bani amsa ba sai ka shiga had'a kaya?"

Yasir ya kwashe da dariya.

"To ai in nuna mata na amince yasa na shiga had'a kaya"

"In kuma wasa nake yi fa?"

"To saina mayar da kayan, kasan ni ba bak'on zafi bane, daga ni har kai mun saba zaman gwauranci, gara ma ni su Momy na gidan, kai ko kwalli d'aya kamar maye"

Dariya ya ba Sadiq sosai.

"Wallahi ni ba maye bane, sabo ne kawai da rayuwan *KAD'AICI*, amma d'an zaman da na yi nan yasa ina son ka zauna dani a gidana"

"Kana so kana kaiwa kasuwa, to ai saina dawo mu cigaba da zama dan ni zamana na tamfarari ne, kasan na kusa zama Ango, sai na bar maka gidanka, ka cigaba da zaman *KAD'AICI* kan ka kawo Amaryanka Khadija take ko wa?"

Wani mugun fad'uwar gaba Sadiq yaji, nan da nan fuskansa ya sauya ba annuri, Yasir ya yi murmushi.

"Allah ya huci zuciyan ran maza, na lura danna kawo zancen nan ne kake huci kamar kumurcin maciji, to yi hakuri karka sareni"

Pillow dake gefen Sadiq ne ya d'auka ya bugawa Yasir ya mik'e ya ce.

"In ka gama min wulakancin, ina waje ina jiranka karka b'ata min lokaci"

"To malam ban gama shiryawa ba, zaka iya d'aukan motanka ka wuce, ni zan biyo bayanka da tawa motan"

Sadiq ya yi kwafa.

"Zaka zo ka same ni anjima"

Sai ya fita, Yasir ya bud'e murya ya ce.

"Kar dai ka tafi ba tare da ka yiwa Momy sallama ba garin fushi"

Sadiq na jinsa ya girgiza kai ya ce.

"Yasir baka da M zan rama"

Sai ya wuce sashin Momy ya yi mata sallama, kana ya fito mai gadi ya bud'e masa gate ya fice.

Yasir ya samu Mahaifiyarsa ya yi mata bayanin komawarsa gidan Sadiq, da farko bata yarda da zancensa ba sai da ta kira Sadiq ta tabbatar, kafin ta amince dan ta san halin kayanta.

Yasir na isa gidan Sadiq, ya cigaba da yiwa Sadiq tsiya, Sadiq banza ya yi da shi bai kula shi ba, dole ya yi shuru dan yasan miskilancinsa ya motsa.

*Da dare*

Sadiq yaje ya samu Dady ya sanar masa da iyayensa sun amince kamar yanda Yasir ya ba shi shawara, Dady ya yi murna sosai ya ce.

"Ya sanar musu da nan da mako biyu yana buk'atar ganinsu domin su tattauna akan maganar"

Jikin Sadiq ya yi sanyi, a k'asan zuciyarsa yana fargaban yadda Dady zai ji in Kawun Yasir da zo da batun nimawa Yasir auren Husna, haka ya yiwa Dady sallama zuciyarsa nata sake-sake ya wuce gida.

Yasir yaje ya yiwa Kawunsa zancen auren Husna, Kawu Sulaiman ya yi murna sosai nan ya kira sauran dangi ya sanar musu suka yanke Juma'a Biyu mai zuwa zasu je don tsaida maganar, nan Yasir ya d'auki kud'i masu tsoka ya bashi ya ce ya ci goro, cike da murna Kawu ya amsa, da yake shi mutum ne mai son kud'i, nan ya masa sallama ya wuce.

****** ******

*Bayan mako guda*

Yasir ya koma gidan Kawu Suleiman shi da Sadiq, kud'i ya ba shi masu d'an yawa kan maganar kud'in sadaki da gaisuwa da sauransu, duk yadda aka yanke sai su bayar, a nan Kawu ya shaida Sadiq ya jinjina masa tare da yi masa godiya.

Dady ya sanar da Baba Husain maganar zuwan Iyayen Sadiq, cike da murna Baba ya yi Addu'a, Inna ma Addu'an ta yi suka cigaba da hiran yadda abin zai kasance.

******

Yau ya kama juma'a kuma ya yi dai dai da ranar da Kawu za suje gidan Dady kan maganar auren Husna. Da misalin k'arfe na dare iyayen Yasir su uku sun zo, suna zaune babban falon baki, Dady yana zaune shi da Abokinsa Alhaji Ahmad suna tattaunawa, nan suka yanke sadaki budu hamsin, dukiyar aure dubu dari, kud'in kayan sa rana budu talatin, duka kud'in dubu d'ari da tamanin. Sunyi farin ciki sosai yadda suka amsa juna cike da mutuntawa, bayan sun gama zantawa suka tsaida ranar Biki wata d'aya, domin Yasir ya nima alfarman kar a sanya masa biki da nisa, kuma haka Kawunsa ya nima basu samu wani targard'a ba wajen Dady, domin shima bai son jan lokaci. Nan suka dai-dai ta daga bisani suka ci abinci gaba d'ayansu, su Kawu sai wajen k'arfe goma suka tafi cike da farin ciki, hak'ak'i sunyi murna da had'uwa da mutanan kirki,

haka ta bangaren Dady sunyi murna sosai, kana Dady ya raka Abokinsa mota suka yi sallama ya wuce.

Tun daga wannan rana Dady ya fara gyara gidansa, a b'angaren gidan sa akwai wani part da yake kulle shima ya gyara shi yaje ya samu su Baba Husain da maganar su koma gidansa dayan bangaren, suka ki yarda, magiya da ban baki ya yita musu da kyar suka yarda zasu koma, amma da sharad'in zai gyara musu nan yasa 'yan haya, haka ya amince da k'udurinsu.

*******

*Biki saura sati biyu*

Su Baba Husain suka tattara kayansu suka koma gidan Dady, farin ciki gun Husna kamar me, ita batasan wainar da ake toyawa ba, ta dai ga Dady na gyara a gidan, tunda taga su Inna sun dawo sai ta yi zaton saboda sune Dady ke gyaran gidan, can take yini wurinsu sai yamma lis take komawa b'angarensu.

Sadiq sai rama yake yi abinci sai ya yi da gaske yake iya ci, ya rasa meke damunsa sam baya cikin farin ciki tunda aka sanya bikin Husna da Yasir, kullun cikin zullumi yake ko Dady zai kira shi amma yaji shuru, abin duniya ya dame shi, Yasir duk yana kallon halin da abokinsa yake ciki, ya yi masa tambayar duniyan nan akan me yake damunsa amma yak'i gaya masa, sai dai ya ce bakomai kawai stress ke damunsa, haka Yasir ya hak'ura ya kyale shi.

******

*Biki saura kwana goma*

Yasir yana ta shirye-shirye ba kama hannun yaro, shi ko Sadiq baya iya tab'uka komai sai ido daya subawa Yasir, Yasir ya kammala had'a akwati da komai wanda ya kamata ya yi, hatta kayan da zasu yi fitan biki dasu an gama d'inka sumu, jiran ranar biki kawai suke yi. Ya gyara gidansa daya gina a hotoro, filat mai kyau guda Biyu a cikin gidan, ya gyara filat d'aya, babban falo mai d'auke da d'aki uku, ko wanne da bayi a ciki sai kicin a falo, da wani extra toilet acikin falon, sai wurin dinning , wanda a lokacin Dady ya tura an sanya furnitures d'in daya siya gado biyu da kujeru, Inna da wasu 'yan uwansu harda Momy Halima sunje sunyi jere. Komai tsaf aka rufe gidan.

Momy Halima Maman su Minal, musamman ta kira mai gyaran jiki mai suna Hajiya Kulu Shuwa, suka je gidan Dady, d'aki aka ware wa matar wanda ta shiga gyaran Husna ciki da waje harna tsawon mako guda. Husna ta yi kyau sai sheki fatar jikinta ke yi, ga wani sihirtaccen k'amshi da take yi duk inda ta gilma k'amshinta sai ya bud'e wurin mai dad'in shaka, wani irin kwarjini ta k'ara. Husna ta yi matuk'ar mamaki da wannan gyara da aka yi mata, tunanin duniyar nan ta yi amma ta kasa gano ainahin dalilin wannan gyara da aka mata, ga shi kullun Momy Halima sai ta zo tare da bata wasu magani masu dad'in sha, wani harda madara a ciki, ita kanta sai da taji

jikinta ya sauya, inta tamabayi Momy sai ta ce mata kawai na gyara jiki ne, kirjinta ya dad'a cikowa gasu a tsaye, hips d'inta ya k'ara fitowa ita kanta inta duba jikinta farin ciki ne ke cikata.

********

*Biki saura kwana biyu*

Gidan Dady ya fara taruwa da dangi na kusa dana nesa, sai kai komo ake yi, musamman Momy Halima ta tattaro kayansu suka sauke zango a gidan Dady, wani part aka ware mata tare da nata gayyan.

Momy Habee dai ta zama har kallo domin ga dukkan alamu jikinta ya gama bata cewa aure Dady zai yi amma yak'i gaya mata, haka dai take zancen zuci cewa in dai baya k'oreta bane zata jure ta zauna har ta samu kansa, dan tana son mijinta kuma sai ta mallake shi, ta d'auki d'amarar raba shi da duk wata 'ya mace dan bata yarda mijinta ya zama mijin biza ba yau yana can gobe yana nan.

*Wai ma 😡Momy baki da tunani. In dai aka juri zuwa rafi da tulu wataran sai ya fashe*

Husna bata fita ko ina kullun tana d'aki tare dasu Minal da Kausar sai wata 'yar uwar su Minal Khairy, sune kawayenta da suke d'ebe mata kewa, yanzu dai Husna zuciyarta ta gama shaida mata aure za ayi a gidansu, sai dai bata gama tantance auren waye za ayi ba, ta dai fi karkata da kila Dady ne zai yi aure shiyasa aketa yi mata gyara dan ta fito taro da kyau.

*******

*Ana gobe d'aurin Aure*

Dady ya kira Husna zuwa part d'insa, domin tunda su Minal suka dawo gidan ta gudu part d'insu can take kwana, bayan ta k'araso ta samu k'asan carpet ta zauna ta gaishe shi cike da girmamawa, nan Dady ya soma magana kamar haka.

"Husnah"

Ya kira sunanta, cikin sanyin jiki ta amsa domin yadda Dady ya kirata ta san da magana a bakinsa mai mahimmanci, ya cigaba da cewa.

"Na kira ki ne dan in shaida miki wasu magana wala Allah su yi miki dad'i ko akasin haka, amma ina so ki natsu ki saurare ni, domin duk Uban kwarai gatan da ya kamata ya yiwa d'iyarsa kenan in dai ta kai munzalin girma, Husna kin yi rayuwa nak'unci da KAD'AICI dalilin rashin Uwa, hak'ik'a hakan yana damuna inna tuna, burina naso ace kiyi karatu mai zurfi kafin in kai ga aured dake, amma na duba hakan bamai yuwuwa ba saboda ina so ki yi rayuwar freedom da jin dad'i kamar yadda ko wasu 'ya'ya suke samu, amma na duba hakan ba zai samu ba face na yi

miki aure kema ki samu gata da kulawan da ya kamata a gidan Mijinki"

Jikin Husna ya yi sanyi nan da nan zufa ya jikata ta fara tunanin me yake shirin faruwa da ita, burinta bai wuce ta yi karatu ba, dan soyayya bata kawoshi kusa ba balle yin aure, kiran sunanta da Dady ya yi ne ya dawo da ita duniyan tunanin da ta shiga, a sanyaye ta amsa wanda idonta harya kawo kwalla, ya ce.

"Ki yi hakuri Husna, kar ki yi tunanin na tauye miki rayuwa ne, a'a jin dad'i nake niman sama miki, insha Allah gobe in Allah ya kaimu za a d'aura miki aure da Mijin dana zab'a miki, insha Allah ba za ki yi kuka dani ba akan zab'in dana miki domin ya kasance shi ne zab'in da Allah ya fidda miki kenan"

Wani irin kuka Husna ta b'arke da shi mai tsuma zuciya, tashin hankali ya gama baibayeta, ji ta yi dama mutuwa ta yi da ganin irin wannan rana, nan Dady ya jawota jikinsa ya soma rarrashinta, da kyar ya shawo kanta ta yi shuru, sai hawaye ke fita tare da ajiyar zuciya, nan da nan zazzab'i ya rufeta. Dady ya cigaba da yi mata nasiha mai ratsa zuciya tare da kalamai masu dad'i,

"my Husna Insha Allah in an kammala biki zan had'aki da mijinki in baku adress d'in in da mahaifiyarki take domin ku je ku gana"

Da sauri Husna ta tashi daga jikin Dady, murmushi ya bayyana a fuskarta ta ce.

"Dagaske Dady?"

Wanin hararan wasa Dady ya yi mata.

"Au da na saba miki wasa ne irin haka?"

Dariya ce ta sub'uce mata.

"Ni bance haka ba, tambayarka dai na yi"

Murmushi ya yi yana shafa gashin kanta.

"Insha Allah za kije wurin Ummanki da zarar an kamala bikin nan, in kun natsa sai ku tafi"

Dad'i ne ya lullub'eta, take damuwar da take ciki ya ragu mata, duk da bata son auren a wani b'angare na zuciyarta ta yi farin ciki, dan auren zai zama sanadin had'uwarta da Ummanta. Da wannan farin cikin suka rabu da Dady wanda ya bita da kallo cike da tausayawa, a ransa yana tunawa da Matarsa abin k'aunarsa Zainab, wacce kullun kwanan duniya yake kwana ya shi da ita a zuciyarsa.

*So da k'aunar gaskiya bata rub'a, hak'ik'a So wani tubali ne a Zuciya wanda in har ya riga ya ginu, rushewarsa sai Allah. Ko da tazarar ya kai nan da bangon duniya ne to son yana nan daram, kamar yadda Khalil da Zainab suka tsinci kansu. Allah ka had'amu da masoya nagari. Ameen*

*******
*_Ranar D'aurin Aure..._*
[11/1, 6:18 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 53 ~ 54_*

*Ranar d'aurin aure*

Yau ya kama ranar d'aurin Aure wanda ya yi dai-dai da ranar Lahadi weekend, wanda za'a d'aura Auren da misalin k'arfe 11am na safe. Gidan Dady ya kacame da dangi sai hada-hada suke yi, girki kala-kala aka girka, Husna na masaukin Momy Halima, ta yi wanka ta sanya leshi pink mai ratsin bak'i da fari, d'inkin riga da zani rafa, Ruky mai make-up tazo ta tsantsara mata kwalliya had'e da d'auri mai kyau, fad'in kyau Husna zai iya cike spice d'in da ya rage na littafin, idonta ya kan kawo kwalla sai dai bata bari ya zubo take shanyewa, su Minal ne ma suke dan zolayarta take murmushi, kwalliyar ya gama bayyana tsarin fatarta kuma ya amshi jikinta, falon Dady suka wuce can suka baje ita da kawayenta, hakanan Husna ta riski kanta da fad'uwar gaba in ta tuno da Uncle Sadiq, ta kasa jure hakan da sauri ta mik'e ta wuce bed room d'in Dady, ta d'auki wayarta Numban Sadiq ta d'anna harya gama ringing bai d'auka ba, sai da ta yi masa kira kusan uku amma bai d'aga ba. Hakan yasa ta kuma shiga damuwa hawaye taji yana sauka kan kumatunta wanda bata san dalilin fitan su ba, zama ta yi gefen gado ta rafka ta gumi tana tunanin rayuwarta.

Ta b'angaren Sadiq yana kallon kiran amma ya kasa d'auka, zaune yake gefen gado abin duniya ya lullub'eshi, tunani iri-iri yake yi, ganin kiranta shi ne ya dawo da shi duniyar tunanin daya lula, bin wayar ya yi da kallo nan da nan idonsa ya kawo kwalla, ya yi yunk'urin kiran ta sai ya fasa, yana k'ok'arin aje wayar sai ga kiranta ya k'ara shigowa, ya d'auka ba tare da ya furta komai ba, ta b'angaren ta ta ce cikin muryan kuka.

"Uncle kana ina? cikin kwana kin nan inna k'ira ka baka d'auka uncle ko na yi maka laifi ne? Uncle ka yi min magana mana"

Ta k'arasa maganar da gunjin kuka, hawaye ne ya gama wanke idon Sadiq, a yau ya k'ara tabbatar wa zuciyansa ya jima da kamuwa da soyayyar Husna, ya kasa fahimta sai a cikin kwanakin nan, cikin sanyin murya ya ce.

"Husna baki min komai ba, kawai dai nayi nesa dake ne saboda aure zaki yi, kuma a matsayina na wanda bamu had'a komai ba kin ga ya kamata na k'auracewa duk wani abin da zai had'amu, ki yi hakuri ki daina kuka, Husna kin same min wani b'ari a rayuwata ina tare dake a Zuciyata, duk in da kika je ba zan manta dake ba"

Kukan tane ya k'aru tana yi da shassheka.

"Uncle ni bana son auren nan, har yau ban san waye Dady zai aura min ba, bana son kowa Uncle"

Da sauri Sadiq ya ce.

"Har ni baki so kenan?"

"A'a Uncle, a duniya daga Dady sai Momyna sai Kai, kune wanda nake So sosai, kuma bana burin rabuwa daku, dan Allah Uncle ka hana auren nan bana son sa"

"Ki yi hak'uri my Husna hakan ba zai yuwu ba, saboda aski yazo gaban goshi, ki yi hak'uri ki amshi k'addararki ki yiwa Dady biyayya insha Allah zaki sami fa'idar haka, kuma Mijin da Dady zai baki mutumin kirki ne, ina kyautata zaton zai rik'e ki Amana"

Nan ya yi ta lallashinta da kalamai masu dad'i har ta yi shuru.

"My Husna yanzu kije ki wanke fuskarki, ki k'ara yin make-up kinga saura awa d'aya a d'aura auran, bana son d'igon hawaye ya sake sauka a idonki"

"To my Uncle ba zan sake kuka ba amma sai ka yi min murmushi"

Murmushi ne ya sub'uce masa ya ce.

"Gashi na miki"

"To kamin waka mai dad'i"

Dariya ta ba shi har hok'oransa suka fito.

"Husna yau dai da rikici kike ji, kuma ni ban iya waka ba"

Cikin shagwab'a ta ce.

"Uhum my Uncle in baka yi ba zanyi kuka"

"A.a kar ki yi kuka, bari na miki"

Nan ya gyara murya ya soma rare mata wak'ar Nura M Inuwa na wak'ar Amarya.

_"🎶lokacin ki ne ya yi Amarya 'yar Amana zo ki je ki zauna da Miji Aure ibada ne,🎶 babu ke a

yau babu gantali a titi, kinga ke da Angonki ne nakewa baiti, ina da sahibata na kasa b'oye sonta, me zana je na furta ban shawara Amarya, tunda duk abin cewa yanzu na gareki🎶"_

Husna ta katse shi da cewa.

"Uncle waye kake so ne haka?"

Dariya ce ta sub'uce masa ya ce.

"Sirri ne, kuma ai wannan wak'a ce na miki, na M Inuwa bawai ni ne na rera ta ba"

Murmushi ta yi ta ce.

"Ashe ka iya waka sosai?"

"A'a ban iya ba, kawai dai koya na yi, kuma iya wannan na iya"

"To Uncle in zo in ganka?"

"A'a Husna, anjima zan shigo na ganki in baki gift d'inki"

"To nagode Uncle da ka sani farin ciki"

"Bakomai my Husna Allah ya miki Albarka"

"Ameen my Uncle"

Sannan ta kashe wayan.

Yasir na tsaye kan Sadiq duk wayar da su ka yi da Husna a kunnen sa, amma Sadiq bai san ya shigo ba, sai da ya aje wayan Yasir ya fara tafa masa.

"Da kyau Baban love, kai da waye kake waya haka harda waka?"

Harara Sadiq ya wurga masa.

"Lab'e ka koma yi ashe, to ka fita hanyata ka wani dameni da tambaya"

Murmushi Yasir ya yi.

"To mai da wuk'ar ni yau ba ranar fad'ana bane a matsayina na Ango"

Wani k'ululun bak'in ciki ne ya tokare zuciyar Sadiq sai bai tanka masa ba, Yasir ya lura da

sauyawar fuskarsa amma ya watsar ya ce.

"In ka gama nuk'u-nuk'u ka fito ga friends d'ina da abokan aikinmu sun zo, kuma saura rabin awa a d'aura aurena dan haka ka fito, kasan kai ne jagoran komai"

Yana gama fad'ar haka bai jira mai Sadiq zai ce ba ya wuce, wani harara Sadiq ya bi shi da shi tare da yin tsaki, mik'ewa ya yi ya d'aura babban rigarsa a saman k'aramar, farar shadda yasa mai aiki da ash color zare, ya sanya cover shoe da hula Ash, a gogansa ma ash, ya yi matuk'ar kyau, fuskarsa a murtuke babu yabo ba fallasa. Shima haka Yasir ya yi na shi kwalliyar, shadda fara mai aiki brown, ya sanya hula da cover shoe brown, agogo kalar brown, ya yi kyau sosai ya fito a angon Husna.

Sadiq yana fita harabar gidansa ya ci karo da mutane. Nan suka soma gaisawa, da yake wasu sun san Sadiq da miskilanci bai cika fara'a ba shiyasa basu gane halin da yake ciki ba na damuwa, Emanuel ne ya ce.

"Kai mutumina ka yi kyau kamar kai ne Ango"

Murmushi ya masa ya ce.

"Ga Ango can yana washe baki kamar gonan auduga"

"Amma fa gaskiya ka fishi had'uwa fa"

"kai Ema baka duba da kyau ba"

Nan dai suka cigaba da hira, dan dama sun saba.

A wajen k'ofar gidansu Dady an sanya tempol da yawa, motoci sun cika layin gaba d'aya dayin ya cike da Jama'a, ga duk kan alamu lokacin d'aurin qure ya k'arato, Dady sai gaisawa yake da mutane yana nuna musu wurin zama, da shi da Alh. Ahmad suna ta hada-hadan karb'an Jama'a, Kawu Suleiman shima ya k'araso dana shi tawagar, nan su Dady suka tarbesu suka gaisa tare da nuna musu masaukinsu suka zauna, Kawu Suleiman ya d'auki wayarsa ya kira wayar Yasir bugu d'aya ya d'auka, kan ya ce wani abu Kawu ya fara magana

"Kai Yasir kuna ina ne ga wuri ya gama had'uwa saura minti biyar fa a fara d'aurawa, ya kamata ku hanzarto ku taho"

Yasir ya ce.

"Ai Kawu gamu nan a cikin gidan Sadiq yanzu zamu fito"

"To sai kun fito"

Nan ya gimtse wayan.

B'angaren Husna ta sake kaya ta sanya wata atamfa blue color mai fulawa yallow da fari, Ruky mai make-up ta tsantsara mata d'auri tare da gyara mata kwalliyarta, Minal ce d'auke da turare a hannunta ta shiga fesa mata, Husna ta yi wani shegen kyau sai sheki take kamar gold, hotuna suka shiga d'auka a yawarsu, suna cikin haka wayar Husna ta d'auki k'ara, tana dubawa taga number Khadija ce, cike da mutuwar jiki Husnah
 ta d'aga wayan tare da shiga bedroom d'in Dady, suka gaisa kana Khadija ta fara mata k'orafin bata kiranta, Husna ta bata hak'uri ta ce.

"k'awata wallahi ina cikin matsala ne shiyasa baki ga kira na ba"

Da sauri Khadija ta tari numfashinta.

"Matsalar me? nima fa ina cike da damuwa"

Nan Khadija ta labarta mata abin da ya faru a gidansu, ta k'arasa maganar da cewa.

"Wai ni yaya Sadiq yake cewa bai so na, dan Allah Husna ya zanyi?"

Mumfashi Husna ta sauke ta ce.

"Ina ganin na ki Khadija mai sauki ne, Ni fa a yau Dady ke d'aura min aure da wanda ban sani ba"

Ta k'arasa maganar muryanta na rawa kamar za ta yi kuka, wani ihu Khadija ta yi wanda sai da Husna ta kauda wayar a kunnenta ta ce.

"What? Aure fa kika ce Husna? shi ne baki gaya min ba"

Nan Husna ta fara kuka ta bata labarin yadda abin ya kasance, ita ma bata sani ba sai jiya da Dady yake gaya mata, Khadija kuka ita ma ta shiga yi, innalillahi kawai take ambata.

"Yanzu an kusa d'aura Auren?"

"Mmmm, yanzu ma za'a d'aura, dan k'arfe sha d'aya safe za'a d'aura, kuma lokacin ma ya yi"

Masu karatu bari na bar Husnah da k'awarta su cigaba da wayarsu, dan na koma wajen d'aurin aure muga wainar da suke toyawa.

K'arfe sha d'aya da minti goma, kowa ya yi tsit ana sauraran shirye-shiryen d'aurin aure, iyaye sun had'u, Baba Husain na zaune, Dady da Alh. Ahmad, sai Baba mai gadi daya sha shadda

brown tasha aiki, Dady ya d"inka masa tare da takalmi da hula bakak'e masu kyau, sune iyayen amarya, sai Kawu Suleiman da Abokinsa malam Tanimu, sai k'aninsa Alh. Ghali, da sauran tawagarsu, sune iyayen Ango. Alh. Ahmad shi ne Dady ya bama waliyyin Amarya, sai Kawu Suleiman shi ne waliyyin Ango, nan suka fara yin sigan Aure kamar yanda Addini ya tanadar mana da shi.
Sadiq da Yasir suna zaune a gefe nesa dasu Dady cikin tempol su da Abokansu, Sadiq ya sunkuyar da kai ya fad'a kogin tunani, bai san abin da ake cikin ba.

Muryan marok'i suka juyo yana shela a lasifika cewar.

_"An d'aura Auren *ASMA'UL HUSNA KHALIL da ABUBAKAR SADIQ ALIYU* bisa sadaki dubu hamsin lakadan ba ajalan ba"_

Wani irin zabura Sadiq ya yi ya kai kallonsa ga mai sanarwa, wanda ya cigaba da shela sai da ya maimaita har sau uku, a zabure Sadiq ya mik'e.

Ta b'angaren Husna kuwa, tana waya da Khadija, tana jin wannan marok'i yana fad'ar an d'aura mata aure da Sadiq, sai ta yi wani wawan ihu ta saki wayar a k'asa ta tarwatse.

_*Wak'ar Sadiq da Husna*_😉

💃💃💃💃💃
_🎶Huuuusna na zama tauraruwaa, sanyin idaniyaa, ni ce zinariyaa.🎶_

🕺🕺🕺🕺🕺
_🎶Husna fito Husna, Husna taho Husna, komai nabai Husnaah.🎶_

💃💃💃💃💃
_🎶Nazo nagaishe ka, na amsa sunanka, so ga shi na bakaa.🎶_

🕺🕺🕺🕺🕺
_🎶Na d'aga kambun soyayya, akan haka na shirya, mai hak'uri an ce mini ba shi asara, kin saka gasa na d'auka, cikin mu samari nai zarra, a duniya an sa mini suna rimio, zo bani soyayya, a so bani jin kunya, sunanki ne Husnaah.🎶_

💃💃💃💃💃
_🎶Abin da nake So ina nan tare da shi, ko kad'an ban son in nesa da shi, bani son komai ya tab'a mini shi, zuciyata dan ta yarda dan ta yarda dashi, juyo na kalle ka, So amshi na baka, ba wanda zai kaikaaa.🎶_

🕺🕺🕺🕺🕺
_🎶Kyauta ta ba zan baiwa kowaba, sai wacce nake So batai min So da wasa ba, inna bata a raina nasan naci riba, zamanmu da ke Soyayya nasa mun saba, zan miki kankamba, shigata

kid'an duba, Sona na bai Husnaah.🎶_

💃💃💃💃💃
_🎶Farin ciki na kai ka zamo sanadi, zuciyata murna ba a dadi, sannu-sannu sai mu jira wa'adi, lokacin ne zanma Albishiri, zan baka Soyayya dan yanzu na shirya, Husnah ta zamo takaaa.🎶_

🎶🎶🎶🎶🎶🎶🎶
🕺🕺🕺💃💃💃
[11/2, 10:02 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 55 ~ 56_*

Mik'ewan da Sadiq ya yi sai kallo ya koma wurinsa, kowa ya yi masa ca da ido, jikinsa ya yi sanyi tare da jin kunya, hakan yasa dole ya koma ya zauna, suka had'a ido da Yasir ya galla masa harara mai cike da tambayoyi, murmushin mugunta Yasir ya masa irin na ko a jikinsa. Bayan an kammala d'aurin aure koya ya mik'e aka shiga hada-hada da abinci dan walima. Sadiq cikin sauri ya isa gidansa, d'akinsa ya wuce ya zauna I gefen gado, malun-malun ya cire tare da hula, ya shiga fifita da hulan saboda duk jikinsa ya had'a gumi, mai-maita kalmar an d'aura masa aure da Husna ya ke yi a zuciya, d'akin d'auke yake da sanyin AC amma ko kad'an baya shigansa sai wani sabon gumi yake yi.

Yasir ne ya shigo yana kwala masa kira sai ya yi arba da shi zaune kan gado sai fifita yake yi da hularsa, dariya Yasir ya kwashe da shi haryana rik'e ciki, cikin dariya ya ce.

"Malam duk gumin murna ce haka? Kazo ka jirge a d'aki ga jama'a nata tambayar ina ango"

Sadiq ya yi tsaki cike da hasala ya fara magana.

"Yasir ban san kana da tab'un hankali ba sai yau, ina so ka sanar min ya haka ya kasance bacin kaine mijin Husna, kowa ya shaida haka hatta abokanka sun san bikinka suka zo, kun sanyani a rud'ani wallahi, gaba d'aya na gaza samun sukuni, ka warware mini yadda zan gane ba mafarki nake yi ba?"

Murmushi Yasir ya yi masa ya samu wani farar kujera ya jawo ya zauna nesa kad'an da Sadiq yana fuskantansa.

"Sadiq hak'ik'a kowa yasan da cewa ni ne zan auri Husna amma ban da ni da Kawu Suleiman da Dady, kai in tak'aice maka su Kawu bani suka nimawa Auren Husnah
ba, da sunanka suka nima aurenta"

Wani razanan nan kallo Sadiq yabi Yasir da shi, kan ya yi magana Yasir ya cigaba da cewa.

"Na san dole za ka yi mamaki, yanzu haka abokaina da sauran mutane na sanar musu

gaskiyarvlamari, cewa kaine ango, dama mun b'oye hakan ne saboda wasu dalilai da bamu son wasu su sani sai ranar aure, da haka suka gamsu yanzu haka suna chan suna cin abincin walima"

Kallon mamaki yanzu Sadiq ya kema Yasir, yana son yin magana Yasir ya katse shi.

"Sadiq duk wani nuku-nuku da kake yi wallahi nasan kana son Husna, ka sani har ga Allah ba zan iya zama da Husna a matsayin mata ba, bacin nasan kana sonta, tun lokacin daka bani labarinka tare dana Husna na fuskanci akwai soyayyar Husna a zuciyarka. Shiyasa na yi wasa da zuciyarka na nuna maka ni zan aureta domin in samu damar da zan had'aku, matsalar iyayenka mai sauki ne Sadiq, nan gaba Insha Allah zasu fahimci komai. Sannan a ganina Husna bata dace da ko wani namiji ba face kai, Sadiq kaine silar farin cikinta harta samu 'yanci, hakan ne yasa Dady ya maka ta yin Aurenta dan ya san in ba kai ba da wuya Husna ta samu miji kamanka, na san kuma ya yi duba da haka ne domin kyawawan halayyar ka, bana tunanin inda ace su Kawu sun je da zancen ni ne zan aureta to babu shakka da wuya ya yarda, domin na san ba zai tab'a amincewa ba, dan yaushe ma ya waye ni da zai bani 'yarsa wacce yafi so a duniya, Sadiq kaima inda ka yi tunanin haka tofa kasan bamai yuwuwa bane, dan haka ka tashi kawai ka fito ka warware my friend mu cigaba da shagalin biki"

Sadiq wani nannauyan ajiyan zuciya ya saki tare da dafe kansa, yana tunanin tabbas abin da Yasir ya fad'a gaskiya ne, ya d'ago kai suka had'a ido da Yasir, cikin raunin murya ya ce.

Yasir ya zanyi da Iyayena in suka ji na yi Aure bada izininsu ba, duk bayanin da zan musu ba zasu yarda ba saboda tunda na baro Kaduna ranar da abin nan ya faru ban sake komawa ba, kana ganin ya zanyi dan sune damuwana yanzu?"

Yasir ya yi ajiyan zuciya tare da matsowa ya dafa Sadiq.

"Abokina ka zama Namiji mana, ka kauda wannan damuwar ka yi shagalin bikinka, Insha Allah komai zai yi dai-dai, na yi alkawari tare zamu Kaduna domin in warware musu komai su gane ba kada laifi ni ne mai laifi"

Sadiq ya yi shuru yana nazarin maganan Yasir can ya nisa.

"Ba damuwa, bari na watsa ruwa na canza kaya"

Yasir ya yi masa murmuahi.

"Good My friend, bari naje na cigaba da karb'an mutane sai ka fito"

Bai jira mai zai ce ba ya fice. Sadiq yana binsa da kallon kauna ya ce a fili.

"Alhamdulillah da samun aboki nagari"

Kana ya mik'e ya shiga wanka.

Ta b'angaren Husna kuwa, ihun data saki yasa su Minal shiga bedroom d'in da gudu har suna bige juma ita da Kausar, sun sameta a tsaye kikam ta runshe idonta, tare da k'ank'ame jikinta, hak'ik'a tana cikin shock, da sauri Minal ta kira sunanta da k'arfi.

"Husna lafiya? meya sameki?"

Haka ta jero mata tambaya wanda babu amsa, bud'e ido ta yi a hankali ta soma kallonsu ba um ba um-um, Kausar ta zuk'unna ta dauki wayar Husna da ta watse a k'asa ta had'a tare da dubawa taga harta tsage kad'an daga sama, ta ce.

"Anty Minal ko zamu kira Momy ce?"

Da sauri Husna ta ce.

"Karku kira kowa babu komai, wai dagaske an d'aura min aure da Sadiq?"

Minal cikin sauri ta ce.

"Eh ba ki ji bane ai anata sanarwa, mu dai ki gaya mana meya baki tsoro kika yi k'ara da k'arfi haka?"

Hawaye ne ya shiga zarya a kan kuncinta.

"Ba komai, kawai dai rud'ani na shiga da wanda na ji ya zama Mijina, ni Uncle Sadiq kawai na sani, kuma ina zargin ko shi ne mijin da Dady ya zab'a min?"

Minal ta ce.

"Ayya 'yar uwa ki yi hak'uri, Dady ba zai had'aki da mutumin banza ba Insha Allah, zaki ji dad'in zama da shi"

Murmushi Husna ta yi mai cike da ma'anoni da yawa.

"Hakane, mu je wurinsu Momy"

Cike da natsuwa suka rankaya cikin gida. Husna tana tunani barkatai akan in Sadiq ne mijinta wani irin zama za su yi ita da take masa kallon Uncle d'inta.

***

Yasir ya lek'o bedroom d'in Sadiq ya ce.

"Kai Malam kanata b'ata lokaci ya kamata ka gama shiri yanzu ai"

"To ai na gama"

Farin material na maza ya sanya mai shara-shara ana ganin singilet d'insa, bak'in hula yasa da bak'in takalmi ya yi matuk'ar kyau, ya sanya agogo bak'i ya feshe jikinsa da turaruka masu dad'in kamshi, ya fito a ango sosai, Yasir binsa ya yi da kallo mai cike da burgewa.

"Kai Sadiq kafa yi kyau ka fito a Ango sak"

Dariya Sadiq ya saki wanda ya bayyana fararen hak'oransa.

"Ban son sharri fa"

"Ba wani sharri, in da baka yi kyau ba ai ba zan tanka ba"

Sadiq ya k'araso kusa da Yasir ya kamo hannunsa.

"Yasir ban da bakin gode maka, face in maka Addu'a Allah ya baka Mata tagari ya saka maka da gidan Aljanna. Ka samar min da farin ciki, yau hak'ik'a na k'ara tabbatar da kai Aminin kwarai ne kana min soyayya na gaskiya, ina alfahari da Abotar mu"

Nan ya yi ta kwararo masa maganganu masu dad'i, ai ko saboda murna Yasir ya jawo shi ya rungume shi.

"Karka damu kai dan uwana ne, haka na d'auke ka tun farkon had'uwar mu. Allah ya barmu tare ya bar zumunci"

Duk suka Amsa da Ameen. Sadiq ya zame jikinsa yana kallon Yasir idonsa cike da hawaye ya ce.

"Kamin komai Yasir, wallahi da ace ban auri Husna ba da samun farin ciki yaye a zuciyata, domin na rasa farin ciki na kenan har abada, kai ne mutum na biyu da ka fuskanci son da nakewa Husna sai Dady, domin Dady ya hango hakan ne ya nima had'amu aure. Matsala d'aya yadda zan fuskanci Husna a matsayin miji, bayan ta d'auke ni a matsayin Uncle d'inta"

Murmushi Yasir ya yi.

"Ni kam ina ganin shawo kanta ba zai baka wuya ba domin ai kun saba sosai, kawai sauya akala zaka yi zuwa nuna mata soyayya cikin saban salo, dan ina ganin ita kanta Husna akwai k'amshin sonka a tare da ita, kurciya ce kawai ba zaisa ta fahimta ba"

"Kai abokina ya a kai ka gane haka?"

"Hhhhh an gaya maka ni na wasa?"

"Hakane fa, domin kai baban soyayya ne makaranta kawai zaka bud'e wa matasa a kan karatun soyayya"

Dariya sosai dukansu suka yi Sadiq ya ce.

"Insha Allah zan koyawa Husna sona, kan muyi wani mu'amalan aure,  kamar nan da shekara biyu lokacin ta k'ara girma da hankali, dan yanzu ni raino aka bani fa"

Dariya Yasir ya yi harda tafa hannu.

"Abokina kar nan da 9 months mu zo shan suna fa?"

"Kai haba dai ai Husna yarinya ce da sauranta"

"Uhum mu dai je zuwa Malam Allah yasa ka iya kaiwa 2month"

"Zan baka mamaki fa Yasir"

"To me na ce, ai na zuba ido kawai, nan zaka so kana bani labari Malam"

Nan dai suka fita suna hira cikin nishad'i har suka isa wurin abokansu, suka cigaba da shagalin biki.

An cigaba da shagalin biki har zuwa yamma, an shirya walima a nan harabar gidan Dady, wata Malama aka gayyato Malama Aisha Muhammad dan ta yi bayani akan zaman takewar aure, an shirya filin gidan da fararen kujeru, in da mata zuka baje sunata kwasar garab'asar sirrin rik'e miki a bakin Malama Aisha, sunsha wa'azi daga bisani k'arfe shida da kwata aka rufe taro da Addu'a tare da raba abubuwa na walima. Can na hango matan *sirrin 'ya mace* sunata hotuna da amarya, su *fatima demsel* harsa sanabe sai wani shigewa Husnahm take yi dan irin ace tafi kowa murna da auren lol😆😚.

Husna jikinta ya yi sanyi da irin wa'azin da taji na girman kyautatawa miji, hak'ik'a ta karantu, kuma ta d'aura d'amarar kyautatawa mijinta iya k'arfinta.

****

Da misalin k'arfe takwas da rabi, motocin d'aukar Amarya sun cika layi, matan Kawu Suleiman da matan mak'otansu, kai harda Momyn Yasir ta taho dan Yasir yaje ya yi mata bayanin komai, sai da ta yi masa fad'a akan abin da ya yi, daga k'arshe ta yi masa nasiha da karya sake aikata irin haka.

"Domin iyaye ba abin wasa bane, yanzu in iyayen Sadiq su kaji aurensa ya zasu d'auka? gaskiya karka sake kamanta irin haka, dan abin da iyaye suka k'i shi tofa ku guje shi, sai ku d'aura da Addu'a"

Nan dai ya bata hak'uri harta sakko ta biyo 'yan d'aukar Amarya a motarta.

Dady ne zaune a falon baki in da ya kira Husna ta zo falon sanye cikin leshi brown riga da zani rafa, ta d'aura dankwali da babban mayafi ya sauka sosai a jikinta ta rufe kanta, sai k'amshin Amare take yi, zama ta yi akasan kafet, ba ta yi minti biyar da zama ba Sadiq ya shigo sanye cikin shadda brown riga da malun malun, ga hula milk ya d'aura, wuri ya samu ya zauna k'asa kan kafet gefen hannun hagun Dady ita kuma Husna gefen dama. Nan Sadiq ya gaida Dady kana suka yi shuru na tsayin minti biyar, Dady ya nisa ya ce.

"Husnah baki ga Uncle d'inki bane?"

Kanta na sunkuye da murmushi a fuskarta.

"Uncle ina yini"

Ya amsa cike da kulawa, daga nan kuma duk su ka yi shuru kowa da abin da yake kitsawa a ransa. Dady ya yi gyaran murya.

"Sadiq ga Husnahm nan na baka ita amana ka kula da ita kamar yadda ka kula da ita a baya, in ta yi kuskure ka tsawatar mata, ka kula da ibadarta, yanzu nauyinta ya dawo hannunka"

"Insha Allah Dady zan kula da ita"

"Yauwa, kema Husna ga Uncle d'inki shi ne Mijin dana zaba miki, ki yi masa biyayya dan Alajannarki yana tafin k'afarsa, in kin bi shi sauda k'afa ki shiga aljanna in kuma kika sab'a masa ki shiga wuta, kuma ki kula da ibadarki, sannan ku d'aura niyyar za ku yi zaman aurenku bisa Ibada ne"

Nan ya cigaba da yi musu nasiha mai ratsa zuciya wanda Husna sai kuka ta ke yi mara sauti da tunanin sabon rayuwa da zata shiga.

"Sadiq zaka iya tafiya yanzu zan taho maka da matarka"

Sadiq ya mik'e cike da jin kunya, ya yi godiya kana ya fita. Dady ya mik'e ya kama hannun Husna ya nufi part d'in Momy Habee.

Zaune take da wasu kawayenta su uku sunata hira da shewa, bud'e d'akin da Dady ya yi ne yasa su yin shuru don ganin mai shigowa, ya shiga fuskarsa ta mau babu walwala ya ce.

"Gata ta zo miki sallama"

Momy jikinta a sanyaye ta mik'e ta isa wurin Husna ta ce cikin sanyin murya.

"Husna Allah ya baku zaman lafiya da zuri'a na gari"

Idon Momy ya kawo kwallar nadama, ta cigaba da cewa.

"Husna ki yafe min duk abin da na miki, hak'ik'a nasan na azabtar da ke na yi nadamar abin da na yi miki, kaicona! ban san ina son ki ba sai da naga dagaske gidan zaki bari"

Ta fashe da kuka sosai, Husna zuwa ta yi ta rungumeta ta ce.

"Momy na yafe miki, nima ki yafe min wasu abubuwan dana yi miki"

Nan suka had'u suna kuka Dady ne ya yi gyaran murya ya ce.

"Husnah ta shi mutafi"

Momy ta ce.

"Bari mu taho tare sai mu wuce"

Dady ya k'ara daure fuska.

"Ki yi zamanki ni zan kaita, bana son ganin k'afarki a gidan ta"

Yana gama fad'ar haka ya kamawa Husna hannu suka tafi suka bar Momy a tsaye cike da jin zafin abin da Dady ya ce mata. Jiki a sanyaye ta koma ta zauna, ta rafka ta gumi, sai yau take jin son Husna na ratsa zuciyarta a dai dai lokacin da zasu rabu, nadama ya ratsata, wata k'awarta ce ta da fata ta ce.

"Hajiya ki yi hak'uri, ki yi k'ok'arin amfani da shawarar da muka baki har ki jawo hankalin mijinki gareki, ki watsar da shirman da kika aikata a baya kuma ki rabu da Haj. Uwani dan wallahi ita ce ta sanyaki hanyar halaka"

Momy ta nisa ta ce.

"Kwarai Haj. Uwani ta taka muhimmiyar rawa wajen bani mugayen sharawa, zan gyara halayyata kafin Alhaji ya yanke min hukunci har Allah yasa in shawo kansa"

***

Dady suna fita ya wuce da ita part d'in su Inna, nan ma fad'an suka mata kana suka rankaya

waje, Dady ya sanya Husna a seat d'in bayan motarsa shima ya shiga sai Sadiq ya zauna gefen Dady suka sanya shi a tsakiya, sai Minal ta shiga gaban mota Yasir ya tuk'asu. Sauran motocin suka kwashi mutane, Momy Halima ta d'auki su Kausar a motarta da su Inna, haka aka rankaya kai Amarya gidanta.

Yasir ya yi parking a haraban gidan, da yake har sun samu mai yi musu gadi, duk suka fito Dady ya kama hannun Husna ya isa da ita bakin K'ofar d'akin ta, dama ya gaya mata wasu Addu'o'i da zata karanta tun a mota in sun k'araso, nan ta karantosu sannan Dady ya bud'e d'akin ta shiga da k'afar dama, suka shiga cikin falon sauran mutane na biye dasu a baya, Dady ya zaunar da Husnahm a kujera, kana ya ce kowa ya shiga yaga d'aki ya bada minti sha biyar, aiko nan matan da suka rako amarya suka shiga d'akuna suna kallon irin dukiyar da aka zuba a gidan, lungu da sak'o na cikin falon sun lek'a dan kashe kwarkwatar ido, wasu na fita wasu na shiga har suka kammala, sannan suka yiwa Amarya sai da safe suka fita, kowa ya koma motar daya kawoshi suka zauna.

Dady ya kira Yasir da su shigo da Ango sannan ya fita ya basu wuri. Abokan Ango suka gama gaisawa su Minal kawayen Amarya, suka yi siyan baki sannan suka mik'e dan tafiya, a nan ne Husna ta fara kuka kamar ranta zai fita ita a dole sai ta bisu, cike da tausayawa Sadiq ya rik'eta har suka tafi. Kana ya sanya mai gadi ya rufe gidan.

Dady yana zaune a mota Yasir yana tukasu, sai Minal da take kusa da Yasir suna hira k'asa-k'asa, Dady hawaye yaji yana saukar masa ji yake kamar ya koma ya d'auko Husna, tausayinta yake ji amma dole ya yi hak'uri dan auren shi ne mafita a gareta, yanada tabbacin Sadiq zai kula da ita fiye dashi ma, tunanin Zainab ya dawo masa sabo, yana tuno ranar aurensu da irin soyayyan da suka sha, ji yake kamar yaje Kaduna dan jin halin da take ciki, amma ina hakan ba zai yuwu ba saboda korarvkare da 'yan uwanta suka yi masa, da wannan tunanin a ransa har suka isa gida.

Da kyar Sadiq ya lallasheta ta yi shuru, mik'ar da ita ya yi ya kama mata hannu ya kaita d'akinta ya ce.

"Nan ne d'akin ki, yanzu ki samu ki natsa bari naje d'akina na watsa ruwa"

Shagwab'e fuska ta yi ta ce

"Uhum ni Uncle tsoro nake ji ba zan zauna ni kad'ai ba"

"Husna ina fa cikin gidan ba fita zanyi ba, ki yi hak'uri ki zauna naje da dawo kinji".

Gyada masa kai ta yi alamar to, nan ya fita ya barta a tsaye, Waldrop d'inta ta bud'e taga an jera mata kaya a ciki, dubawa ta yi ta ciro wani doguwar rigar barci mai hannun bes tsayinta ya kai k'aurinta, ta tub'e kayanta ta sanya wannan rigar ta k'ulle gashinta ta sanya hulan barci ta d'auki gyalenta ta yafa a jikinta, kwanciya ta yi kan gado tana sauke numfashi, bata wuce minti

biyar da kwanciya ba sai ga shi ya shigo rik'e da tire a hannunsa da leda akai, sanye yake cikin farar jallabiya mai guntun hannu na barci, ya ce.

"Husna ba dai kin kwanta ba? tashi muci abinci, dan na san da wuya in kin ci abincin kirki yau"

Da sauri ta ta shi ta zauna ta ce

"Wallahi ni Uncle k'ishin ruwa ma na ke ji"

"Ok, ta shi ki je kicin yana nan a fridge saiki d'auko mana drink da ruwa"

Ido ta zaro ta ce.
"Uncle ni fa tsoro nake ji"

"kai Husna yaushe kika fara jin tsoro ne haka? nan fa gidanki ne dole ki koyi zama ke kad'ai saboda wata ran zan fita aiki nabarki ke kad'ai a ciki har sai na dawo, yanzu dai yi huk'uri ki je ki d'auko mana babu abin da zai kama min ke"

Cikin sanyin jiki ta fita, kicin d'in ta isa ta d'auko ruwan da drinks d'in, gyalenta ne ya zame mata akai sai ta ji kamar motsin mutum a bayanta, da gudu ta arce ta fad'a d'akinta tana haki ta saki drinks da ruwan a k'asa ta k'ank'ame Sadiq tana maida numfashi, gyalen ma ya zame mata yana falo, wani irin shock Sadiq yaji gaba d'aya ya shiga wani yanayi, duk kan gab'ob'insa sai da suka amsa da bak'on al'amari, nan da nan idonsa sun sauya sun d'an yi ja tare da k'ank'ancewa, d'ago fuskarta ya yi cikin sanyin murya ya ce.

"Husna meye ya baki tsoro?"

A hankali ta bud'e ido suka sauka kan na shi, sun d'auki kusan minti uku suna kallon juna, take nan ta ji ya saukar mata da kasala ta yi saurin kauda idonta ta mai da su suna kallon k'irjinsa, cikin sark'ewar murya ta ce.

"Uncle motsi naji a bayana kamar na mutum, shi ne na rugo da gudu, Allah ni fa tsoron gidan nan na ke yi, ka maidani gidan Dady"

Ta k'arasa maganar cikin shagwab'a, murmushi ya yi mata ya ce

"Ke dai kin cika tsoro, kuma ba in da zan kai ki kin zo kenan, dan aurenmu babu saki yarinya, sakeni karki sa na fad'i ba shiri"

Ya karasa maganar da zolaya yana jan hancinta, cikin shagwaba ta ce

"Uhum ni ban da Karfin da zan kayar da kai, dafa har goyani kake yi fa"

"To na ji, yanzu muci abinci kin ga dare yanayi"

Ba musu ta sake shi cike dajin kunya, sai yanzu ta tuna da irin shigar dake jikinta ga gyalenta yana falo, nan suka yi ciye ciyensu da Yasir ya siyan musu da sauran drunk, tun tana nuk'u-nuk'u har ta saki ji, suka ci suka k'oshi. Husna ta shiga bayi ta wanke baki ta dawo ta zauna bakin gadonta, Sadiq ya mik'e ya kai kayan kicin ya wuce d'akinsa, ya wanke baki ya zauna bakin gado yana tunanin ya kwanta a nan ne ko yaje dakin Husnah?.
[11/3, 8:08 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 57 ~ 58_*

Yanke shawara ya yi bari ya kwanta a binsa in taji shuru ta yi barci. Ya kashe fitila ya yi Addu'a ya kwanta cike da tunani barkatai. Husna tana zaune tana ta jiran dawowar Sadiq amma taji shuru, komawa ta yi ta kwanta ta rufa da barko, runtse ido ta yi ko kila barci zai kwasheta, amma ina tsoro ya hana ta barci sai juyi take yi, ko fitilan d'akin ta kasa kashewa, har kusan misalin k'arfe 12am na dare barci bai d'auketa ba, cikin jin tsoro ta mik'e ta bud'e d'akin a hankali tana waige-waige cikin sand'a take taku harta isa d'akin Sadiq ta murd'a k'ofar ta yi sa'a a bud'e yake, sai dai akwai duhu, haka ta shiga tana zare ido tana lalube harta isa bakin gadonsa, a hankali take kiran sunan shi amma taji shuru yak'i amsa mata, kuma shima bai samu yin barcin ba saboda tunanin daya zurfafa a ciki, yana jin lokacin data bud'e d'akin nasa, tana lalube har hannunta ya kai kan k'afansa, ta tab'a shi amma ya yi mata shuru kamar yana barci, kuka ta fara yi a hankali, sannan ta hau gadon gefensa ta kwanta, ta k'udundune kamar mai jin sanyi, Sadiq yana jin nishin kukanta bud'e ido ya yi ya juyo gefen data kwanta sai ya mirgino ya jawota jikinsa da k'arfi ya rungumeta, wata 'yar k'ara ta saki, sautin kukanta ya k'aru, cikin muryan barci Sadiq ya ce.

"Husna me yake da munki ne? ashe baki yi barci ba? mema ya kawoki d'akina?"

Ya jero mata wannan tambayoyi, cikin kuka ta ce.

"Uncle tsoro nake ji"

K'ara matseta ya yi jikinsa har suna iya jin bugun zuciyan juna.

"Ok, shi ne kuma zaki zo nan ki hanani barci ko?"

Shuru ta yi tana shakar kamshin turarensa. Hannu yasa ya d'ago fuskar ta, ko da suna cikin duhu Husna ta san fuskarta yake kallo, suna shakar numfashin juna, bugun zuciyarta ne ya k'aru da kuma jin wani bak'on al'amari, harshensa yasa ya soma bin hawayen fuskarta yana gogewa, wani irin yanayi suka cinki kansu wanda suke fidda numashi da sauri, sai da ya goge mata tas sannan ta sauke wani gwauran numfashi, a hankali Sadiq ya kira sunanta sai ta b'oye kanta a jirjinsa tana mai da ajiyar zuciya a hankali, murmushi Sadiq ya yi domin ya gano Husna ba zata yi masa wuyar juyawa ba, d'ago fuskarta ya yi ya had'e bakinsu, tsawon minti goma kana ya saketa. wani iron kuka ne Husna ta b'arke da shi wanda bata san dalilin yinsa ba, shin na farin cikin ne ko kuma na bak'on al'amari da Uncle yazo mata da shi. Yana rungume da ita ya

yi ta lallashi har barci ya yi a won gaba dasu.

*******

Haka Sadiq ya yi ta koyawa Husna abubuwa masu wuyan fassarawa, na yau daban na gobe daban, Husna ko tsananin jin kunyarsa take yi wanda bata iya had'a ido da shi. Cikin k'ank'anin lokaci ya kowa mata yadda zata saba da shi, shak'uwa mai k'arfi ya kullu a tsakanin su a cikin tawon kwana bakwai, kullun Sadiq yana gida masallaci kawai ke fidda shi waje, da yake ya samu hutu na 2weeks a gun aiki, kullun daga gidan Dady ake aiko musu da abinci, Yasir ne mai jigilan kawo musu.

*****

*Bayan kwana goma sha biyu*

Yau ya kama Friday kwana goma sha biyu da auren su, tun da suka wayi gari Husna ta fad'a kicin domin ranar ne zata fara girki kuma ranar ne Abokan Ango zasu zo cin girkin Amarya, da misalin k'arfe 9am na safe, sai ga Minal ta shigo gidan nasu domin dama tun jiya Husna ta kira ta akan tazo ta taya ta aiki, dama Sadiq tun safe ya fita, haka suka duk'ufa girki, tunwon shinkafa da miyan agushi, sai miyan kib'ewa danya da Uncle Sadiq ya ce yana so, sai fried rice da suka yi, peppe chicken, sai sultan chips mai had'e da kayan cikin sa, cikin k'ank'anin lokaci gida ya gauraye da k'amshi, Minal sai ta zama 'yar kallo domin ita bata iya girki sosai ba, iya ka ta taya Husna yanke-yanke da kuma hira, juice d'in kankana ta yi da soya milk juice. Ta sanya a fridge, Minal da ta d'an d'ana sai santi take yi.

Da misalin k'arfe 1pm Husna ta kammala komai harta zubasu a masubi, a falo ta shirya kulolin a carpet, juices d'in ne bata fito da suba suna fridge, wanka ta yi ta sanya wata purple atamfa mai d'auke da fulawowi fari da yalo, d'inkin fitted riga da siket ta yi kyau sosai, ta yi d'auri mai kyau kamar gwagwaro, turaruka ta fesa kana ta fito bayan ta yi sallah. Minal binta ta yi da kallo tana ya ba kyau da Husna ta yi, murmushi ta sakar mata ta ce.

"Malama ya da kallo kamar baki sanni ba"

Ita ma murmushin ta mayar mata.

"Kalau sisi, kawai na ga Amarcin ya amsheki ne, gaskiya uncle ya iya kiwo"

K'arasowa ta yi da sauri wurinta, ta kai mata dukan wasa sannan ta zauna tana cewa.

"Kai sis bana son sharri, dama can haka nake"

Nan dai Minal ta cigaba da zaulayarta suna hira da barkwanci. Kallo suke yi har misalin k'arfe biyu da minti goma na rana, sai ga sallaman Sadiq ya shigo, cikin nutsuwa Husna ta mik'e ta isa wurinsa, daskarewa ya yi a tsaye yana kallonta domin wani bala'in kyau ta yi masa, murmushi ta sakar masa ta amshi ledan hannunsa tare da yi masa sannu da zuwa, shima murmushin ya

mayar mata da cewa.

"Yauwa, ya aiki? dan nasan yau kin gaji"

"Aiki Alhamdulillah Uncle, dan ba wani yawa ma Minal kuma ta taya ni wasu ai"

K'arasawa suka yi cikin falon ya zauna suka gaisa da Minal nan ta shiga kicin ta ajiye abin da Uncle ya siyo, kayan miya ne da sauran abin buk'ata. D'akinsa ta wuce shima ya bita a baya suna shiga ya rungumeta ta baya yana shak'ar k'amshin turarenta ya ce.

"Kai my Husna wannan kyau haka da kika yi, sai ki sanya na kasa fita ko nan da can"

Dariya ta yi.

"kai Uncle ai ina yi kullun fa"

"Eh, amma yau dai kwalliyar taki tasha bamban dana kullun"

"Tom Uncle nagode, yanzu ka shiga ka yi wanka"

"No ba zanyi wanka yanzu ba, domin su Yasir suna hanya"

"Ok, anjima sai ka yi ai".

Falo suka koma, bayan minti biyar sai ga kiran Yasir a wayar Sadiq, ya d'auka da yi masa izini su shigo kawai, kallon Husna ya yi.

"Tashi ki je ki d'auko mayafi ki yafa"

Cikin shagwaba ta ce.

"Uncle ana zafi fa, kuma ai a falo muke ko fita za mu yi ne?"

Sadiq ya yi mqta hararan wasa.

"Malama ta shi kije kisa tun kan raina ya b'aci, su Yasir ne fa suka zo, kina nufin a haka zasu ganki?"

Dole ta tashi ta shiga tana shagwab'a harda buga k'afa, aiko Minal ta kwashe da dariya ta ce.

"Sisi Allah ya shirkeyi har yau baki girma ba"

Dariya shima Sadiq ya yi ya ce.

"Rabu da ita zata bari ne ai"

Rufe bakinsa keda wuya sai ga sallamar su Yasir, nan suka baje a falo su bakwai harda Ema da wani Mujaheed, falon ya gauraye da kamshin turare dana abinci, su Yasir har sun fara had'iye yawu, suka gaisa da Minal ta mik'e dan kiran Husna, ta cimmata zata fito nan suka dawo tare, Husna ta gaishe su, daga nan suka shiga kawo musu juices dasu plata, bayan sun gama had'awa Husna ta zuk'unna zata zuba musu, Uncle ya dakatar da ita ya ce.

"Ki barshi kowa zai zuba iya cikinsa"

Ba musu ta mik'e ta wuce d'akinta, Minal ita ma ta take mata baya.

Sun ci abinci sun sha juice suna santi, shi kanci Sadiq ya yi mamakin yadda Husna ta iya tsara abinci haka, duk kallon da yake mata bata gama iya komai ba yana mata kallon k'aramar yarinya, su Yasir kuwa an saki ciki sai lodi suke yi, duk abin da ta kawo sai da suka ci. Hatta miyar kub'ewa wanda ta yiwa Sadiq sai da suka ci shi bayan sunci miyan agushi, Yasir harda cewa a zuba masa sauran fried rice a kula dan ya samu na dare.
A gaskiya sun yaba da kwazon Husna wajen girki wanda suka yi ta ma Abokinsu barka da samun Husna matsayin matarsa, Sadiq yaji dad'i sosai da farin cikin Husna ta fidda shi kunya, har Allah-Allah yake su tafi dan ya mata albishir na tukwicin farin cikin da ta sanya shi.

A nan suka yi sallan la'asar a masallacin unguwar su Sadiq, sai misalin k'arfe shidda na yamma suka tafi, Mujaheed ya d'auki Minal a motarsa dan ya sauketa a gida, daga nan kuma soyayya ya kullun a tsakanin su.

Bayan sallan isha'i Husna ce sanye cikin riga da wando English wears, sun kamata sosai, ta yi mild make up, tayi kyau abin ta, falo ta fito ta zauna ta soma kallon Arewa24, Sadiq ya fito daga d'akinsa sanye da wando tree quarter sai riga ta shan iska mai guntun hannu, k'arasowa ya yi cikin sanda yaje ta bayan kujerar da Husna ke zaune, wanda gaba d'aya ta tattara hankalinta tana kallon TV, hannu yasa ya rufe mata ido da k'arfi, aiko zabura ta yi ta tsandara ihu, Sadiq ya ke ce mata da dariya har yana kyalkyatawa yana rike ciki, b'ata rai ta yi tana hararansa harya k'araso kusa da ita ya jawota jikinsa.

"My Husna sarkin tsoro, zanga ranar da zaki girma da yin ihu"

Kukan shagwab'a ta shiga yi masa harda hawaye tana dukansa a k'irji, murmushi ya yi.

"Husna ta ki yi hak'ura ba zan sake ba"

D'ago fuskanta ya yi yana kallon kwayan idonta wanda yake cike da hawaye, murgud'a masa baki ta yi ta kauda kai gefe.

"Ni kike murgud'a wa baki? aiko yanzu zanyi maganin sa"

Kama bakinta ya yi ya sanya hannu ya murd'e su ta saki k'ara min k'ara.

"Kai Uncle, Allah da zafi fa"

"Tom sorry My Husna, bari na ba shi magani ya daina zafi"

Kan ta yi magana ya fincikota ya fad'a bakinsu guri d'aya, sun kai tsayin minti goma kana ya saketa suna mai da numfashi da sauri, ta mik'e ta ruga d'aki da gudu tana haki, binta ya yi da kallo yana dariya. Shima mik'ewa ya yi ya isa d'akinsa, Alwala ya yi kana ya sauya kayansa zuwa jallabiya milk color, ya fito ya nufi d'akin Husna wacce ita ma ta sauya kaya zuwa kayan barci maroon color, binta ya yi da kallon sha'awa ya ce.

"My Husna zo muje d'akina in nuna miki wani abu"

D'agowa ta yi da hararen wasa.

"Ni barci zanyi"

"Haba sweet Husna, ki yi hak'uri muje in nuna miki"

Ya marairai ce fuska kamar zai yi kuka, dariya ya bata ta soma kyalkyatawa, dama burinsa kenan ya sata dariya dan ta daina fushi da shi, yad'aukar mata zani da hijab suka wuce d'akinsa. Alwala yasa ta ta yi, ba musu taje ta yi da yake ya sabar mata da kwanciya da alwala, bayan ta fito taga ya shinfid'a dadduma da mamaki ta ce.

"Uncle Sallah za mu yi ne?"

"Eh Nafila za mu yi dan godiya ga Allah daya had'amu aure bisa raya sunnar Monzon Allah S.A.W. murmushi ta yi bata kawo komai a ranta ba, ta d'aura zani tare da sanya Hijab suka tada Sallah.
[11/3, 10:00 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 59 ~ 60_*

Bayan sun idar da Nafilar, ya yi mata nasihohi da jan hankali game da zaman takewar aure, sannan ya dafa kanta ya karanto addu'o'i kamar yadda Manzon Rahma ya koyar damu s.a.w. bayan sun gama sai suka mik'e duk suka k'ara shirin kwanciya suka kwanta, Sadiq ya rage hasken fitilar d'akin. Ganin haka nima sai na yi musu fatan alkhairi na yo waje na nufi gidan Dady.

*******

Dady da Momy zaune suke a falo, Dady yaba zaune saman Cushing, Momy na durk'ushe a gabansa ta gurfana kamar mai rok'an gafara, Dady ya ce.

"Habeeba a yau zaki girbi abin da kika shuka, na san zaki ga na yi miki shuru kamar abin bai dameni ba ko? hmmm, to ina sane da komai, na bari ne in samu nutsuwa sosai kan sanin wani hukunci ya dace na yanke miki, dan haka nagode da duk makirci da abubuwan da kika ai kata, ni ba ki yi min komai ba kanki kika yi mawa, ki sani dai duniya fararra k'ararre ne, kuma duk abin da ka shuka hak'ik'a zaka girbe shi imma khairan ko sharri, ni duk abin da kika min da wanda kika wa Husna duk na yafe, amma fa ki sani zamana dake ya k'are"

Wani irin razana Momy ta yi, ta d'ago kai a firgice ta d'aura hannu bisa kai.

"Na shiga uku Alhaji kamin rai karka gutsire igiyar aurenmu, wallahi na tuba na sauya halina ba zan sake kamanta haka ba, ka yafe min"

Kallon k'ask'anci Dady ya yi mata.

"Zan so ki tuba d'in, sannan Allah yana son mutum mai amsan laifinsa kuma da niyyar ba zai zake saba masa ba har iya k'arshen rayuwarsa, dan haka na riga na yanke igiyar aurena dake har guda biyu, ga takardar saki a rubuce, na sake ki saki biyu, in kin gama idda ki samu miji kiyi aure"

Kuka Momy ta saki, ta kasa karb'an takardar, Dady ya ajiye mata a k'asa, ya cigaba da kallon TV abin sa, kuka take kamar ranta zai fita, yau nadama ya shiga zuciyarta da dana sanin abin da ta aikata, yau taga sharrin bin boka da tuggu, duk gasu ba su yi mata rana ba, bayan ta yi kuka ta gaji ta sassauta kukan tare da share hawayenta ta ce cikin dishewar murya saboda tsabar kukan da tasha.

"Alhaji ina niman ya fiya a gunka tare da alfarman zanyi zaman idda a d'akina, har zuwa lokacin da ya cika sai in tafi"

Tana kaiwa nan ta tsaya don jin me zai ce, har azuciyarta ta yi amfani da hakan ne domin ta samu hanyar da zata shawo kansa su shirya, kan ta gama iddan ta samu ya maidata d'akinta domin akwai sauran igiya d'aya. Dady shuru ya yi na mintuna daga bisani ya ce.

"To shi kenan zaki iya zama ki yi idda, domin musulunci ma ya yarda da ayi hakan, dan haka ki yi zaman idda a d'akinki, in kin gama sai ki tafi"

Yana kaiwa nan ya mik'e ya wuce part d'insa ba tare da ya k'ara waiwayen inda take ba, hawaye masu zafi suka sauka kuncinta, tana tuno irin abin da ta yi da kuma dana sani akan aikatasu da ta yi. Haka ta mik'e ta wuce d'akinta rik'e da takardar saki, ta fad'a kan gado ta k'ara kecewa da sabon kuka.

Haka dai gidan Dady suka kwana ko wanne da irin damuwansa. Sab'anin gidansu Sadiq da su ka yi kwanan farin ciki.

******     ******

*Washe gari*

Da asubahi Husna tana kwance ta k'udun dune da bargo, shi kam Sadiq yana gabatar da Sallar asubahi, ya idar ya zauna yana lazumi, Husna na kallonsa hawaye na zuba mata na farin ciki, hakanan taji son mijinta na ratsa duk kan b'argon jikinta, tana tuno abin da ya faru a daren jiya, sai taji ta cintsi kanta da murmushi tare da hawaye, hak'ik'a Allah ya bata Miji d'aya tamkar da dubu, ko da dai tasha wuya sosai amma ya rangwanta mata saboda tsananin tausayinta da ya ke yi. Tasowa ya yi ya k'araso wurin gadon sai ta yi sauri ta runtse ido kamar mai barci, murmushi a kan fuskansa ya fara kiran sunanta a hankali, motsawa ta yi sai taji wani azabar zafi ya ratsata da sauri ta bud'e ido tare da fad'in wash, cikin kulawa ya ce.

"My sweet love ta shi kije ki yi wanka ki zo ki yi Sallah, kinga lokaci yana tafiya"

Shagwab'e fuska ta yi ta fara rera kuka, matsawa ta yi sosai kusa da ita wanda har tana jin hucinsa, ya ce.

"My sweet Husee menene kuma?"

Bata tanka shi ba ta muskuta gefe tana mai runtse ido na azaba, domin duk yadda ta motsa sai taji zafi na ratsata, ta mik'e da kyar tare da bargon data cikwi kwiye jikinta da shi ta fara takawa a hankali dan ta isa bayi, murmushi ya bita da shi ya mik'e cikin azama ya cimmata, d'aukarta ya yi cak ya shige da ita bayi tana wutsil-wutsil. Da kansa ya gasata ya mata wanka, sannan yana kallonta ta yi wankan tsarki, ya kuma d'aukarta ya dire ta a gefen gado, d'akinta yaje ya d'auko mata jallabiya bak'a ya kawo mata, haka ta zura ta mik'e tana dingisawa ta sanya hijab ta tada sallah, bayan ta idar ta haye kan gado dan huta gajiyar jiya.

A Ranar Sadiq ya sha shagwaba duk inda ta motsa idonsa na wuri, hatta abinci shike bata a baki, sai wani narke masa take yi, Sallah ma a gida ya yi bai iya fita masallaci ba, shi ya ja musu jam'i, ko nan da can bai iya motsawa suna tare, ko da Husna na jin kunyarsa, ta dan saki jiki sun sha soyayyar su mai cike da So da K'auna. Sadiq har mamaki Husna take ba shi yadda take da jarumta da juriya, sannan ko wani salo ya koya mata tana rik'ewa a kanta, wanda take azamar ta yi masa dan ta sanya shi farin ciki.

***********"

*Bayan wata d'aya*

Husna ta soma sabo da rayuwar aure, wanda yanzu ta saki jiki ta k'ara fahimtar ya aure yake da

abubuwan da suke ciki, tana iya k'ok'arinta wajen farantawa mijinta rai, ta aje sunan Uncle ya dawo sunan Miji yanzu, abinci kala-kala tana k'ok'arin yi masa, gyaran gida da duk wasu abu tana k'ok'arin gyarawa, a b'angaren shinfid'a ma tana k'ok'ari domin ta soma sabo da sabar rayuwa da ta tsinci kanta a ciki, kuma Sadiq yana yaba mata saboda juriyarta. Sun zama hanta da jini, duk wani abu tare su ke yi in dai yana gida, shak'uwa mai k'arfi ya shiga tsakaninsu ko aiki yaje suna manne da juna a waya, Soyayya suke yi sosai wanda duk wanda ya gansu zai yi tunanun sun shekara da zama tare. Sadiq ya kanyi mamakin yanda Husna ta kware wajen yi masa abubuwa sosai, ga ta dai da k'ank'anin shekaru amma sai kace babbar Mace. Abin da Sadiq bai sani ba shi ne a kullun in ya fita aiki, takan saurari kaset na wa'azi kan zamantakewar aure da yadda Mace zata tarairayi Mijinta, in ta kammla aikin gidanta kuma takan hau WhatsApp group d'in *Anty Rahma* ta samo ilimi akan sirrin rik'e miji a wajen Matan *Sirrin 'ya Mace group*.  A wajen girki kuma tana samun ilimi sosai a group d'in *Nana diso kitchen* wajen sarrafa abinci kayan ciye-ciye da sauran juices da drinks. Da yawaita karatun lissafan Addini na gyaran Ibada dana gyaran jiki. Wannan sune sirrikan da Husna ta rik'e take samun ilimi wajen faranta ran mijinta har ta kware sosai.

*******     *******

*Bayan mako guda*

Ranar Juma'a, da dare su Sadiq suna falo, Husna ta d'aura kanta a kan ciyarsa yana wasa da gashin kanta wanda yasha gyara, hira suke yi kasa-kasa na masoya wanda baka iya jiyo hiransu. Kira ne ya shigo wayarsa wanda ya katse musu hirar, ya sanya Husna ta d'auko masa, ganin sunan da ya bayyana a kan phone d'in yasa shi fad'uwar gaba, da sauri ya d'auka ya kara a kunnensa ya ce.

"Abbana ina yini"

D'ayan b'angaren aka hau masifa.

"Ban sani ba, yanzu kai Sadiq ka zama mara mutunci ko? tunda aka maka fad'a kusan wata uku kenan kak'i ka waiwayo gida ko, ka nuna mana bamu isa da kai ba ko?"

Risina wa Sadiq ya yi kamar Abban na kallonsa, ya ce.

"Abba ka yi hak'uri wallahi aiki ne yasa ban zo ba, amma Insha Allah zan zo"

"Rufe min baki sakaran banza kawai, to ina so ka sani gobe-goben nan in Allah ya kaimu ka taho Kaduna, mutumin wofi"

Gaban Sadiq ya shiga fad'uwa ya ce cikin rawar murya.

"Abba ayi min hak'uri zuwa mako mai zuwa insha Allah zan zo"

"Naki na bari mako mai zuwa d'in, Allah ka kiyaye ni fa tunkan musa k'afan wando d'aya da kai, in Allah ya kaimu gobe na ce ka zo, in ba haka ba wallahi ranka sai ya yi mummunar b'aci"

Ya kashe wayar ba tare da jin amsar da Sadiq zai ba shi ba. Gumi ne ya ketowa Sadiq gaba d'aya zuciyansa ya dagule, yana tunanin ta ina zai fara, Husna duk tana jin maganar da suka yi, da yake Abban na magana da k'arfi, matsawa ta yi kusa da shi ta dafa shi ta ce

"Sweet hubby me yake faruwa ne?"

Nan Sadiq ya goge zufan da ya karyo masa a goshi.

"Sweet Husee, Abbana ne ya kira ni, ai kin ji maganar da mu ka yi da shi?"

Ta gyad'a masa kai alamar eh ta ce.

"To Baby muje mana, ashe dama ba a nan Kano suke ba? wallahi ni har na ji dad'i zamu Kaduna, dama ban tab'a tafiya mai nisa ba, kullun ina Kano"

Ta karasa maganar cikin shagwab'a, murmushi ya yi wanda ya tsaya iya kan leb'e ya ce.

"Husna ba zaki gane ba, akwai babban matsala ne"

Husna ta zaro ido kamar zasu yo waje.

"Matsala kuma?"

Ya gyad'a mata kai, nan ya jawota jikinsa ya shiga bata labarin shi da asalinsa, da duk abin da ya faru har ya zuwa aurensu, hak'ik'a Husna ta razana da wannan labari, d'ago ido ta yi wanda suke zubar hawaye.

"Yanzu uncle rabamu za su yi ko?"

Sadiq ya k'ara matseta a jikinsa.

"Ina, babu wanda ya isa ya rabamu sai Allah, ki kwantar da hankalinki komai zai yi dai-dai."

K'ank'ame shi ta yi tana kuka a hankali mai kashe zuciya. Sadiq ya sumbaci kanta yana lalla shi, a ransa ya na jin, ko kashe shi za su yi wallahi ba zai iya rabu da matarsa ba domin ita ce rayuwansa.

[11/4, 7:01 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 61 ~ 62_*

Washe gari da sassafe suka ta shi suka shirya, babban trolley biyu suka sanya kayansu a ciki, sunyi wanka sun shirya Husna ta sanya a tamfa dark blue mai kwalliya yallow, fari da baki, riga da siket d'inkin fitted, ta sanya farin gyale da bak'in takalmi da jaka, sai sarka da dan kunne silver color, ta d'aura bakin agogo a hannunta, ta yi kyau sosai ko da ba wani kwalliya ta yi sosai ba. Sadiq shi kuma ya sanya yadi sky blue ya sanya hula da takalmi bak'i sai agogo ash color, ya yi kyau shima sosai. K'arfe takwas na safe da 'yan mintuna suka fito, sallama suka yi da mai gadi kana suka kulle part d'insu suka wuce gidan Dady.

Bayan sun isa, ya yi parking mota a k'ofar gida suka shiga cikin gidan, sun gaisa da Baba mai gadi sannan suka k'arasa cikin gidan, sun hango Dady da Baba Husain zaune bisa babban dadduma a wata 'yar baranda dake cikin gidan, da murmushi a fiskokinsu suka isa wajensu, zama su ka yi kana suka gaisa Dady ya k'urawa Husna ido saboda wani girma da kyau data k'ara, dan tunda aka yi auren ya hana Sadiq ya kawota wai sai ta yi 2 months, yanzu ma ya yi mamakin ganinsu da safe haka, su Sadiq suka wuce part d'in Inna suka gaisa kana suka fito, nan ya zayyana masu Dady tafiya ce ta kamasu zuwa Kaduna sati d'aya zasu yi su dawo, su Dady suka yi musu Addu'a kana ya k'ara yi musu nasiha sannan ya ciro bandir d'in kud'i na dubu ashirin ya bama Sadiq da su sha mai a mota, ya amsa cikin girmamawa ya yi godiya kana suka yi sallama suka tafi cike da farin ciki. Baba Husain yana yaba natsuwar Sadiq da kyawawan halayyarsa, gaskiya suna farin ciki da samun siriki nagari.

Su Sadiq sun shiga mota ya yi sallama da Baba mai gadi ya ba shi dubu uku ya amsa yana godiya, ya kunna mota suka wuce idonsa na kan gidan da ya bari wanda Yasir ya cigaba da zama aciki, da yake kud'in hayan bai k'are ba, kamar ya kira shi ya sanar masa da tafiyansu sai ya basar saboda baya so ya shiga cikin matsalarsa, k'ok'arin had'asu aure da ya yi da Husna ma ya gode masa kuma a kullun yana masa addu'an fatan alkhairi. Haka suka kama anyar kaduna.

Sun tafi baifi da rabin sa'a ba sai ga Yasir ya shiga gidan Dady domin ya karya a nan, dama tunda aka yi auren su Sadiq, Dady ya ce ya rik'a zuwa yana cin abinci a nan, yana shiga suka gaisa kana Dady ya tura masa kular wainar shinkafa da miyan taushe ya ce.

"Ga mutuminka yau nasa anyi mana"

Da murmushi ya jawo kulan ya shiga zubawa, ya zuba miyan ya soma ci, Dady ya ce.

"af, Yasir ga lipton na manta ko zaka fara sha ya warware maka hanji"

Yasir ya yi dariya ya ce.

"Ai Dady nasha tea d'azu wainar kawai zanci"

Baba Husain ya ce.

"Ai Khalilu rabu da shi tunda ya samu muradinsa ai baya ta tea"

Suk su ka yi dariya, yana gama cinyewa Dady ya ce

"Ashe zuwa Kaduna ya kama su Sadiq yau d'in nan, nasan ya gaya maka dan d'azu ma suka mana sallama"

Cike da mamaki Yasir yake duban Dady ya ce.

"Wallahi bai gaya min ba, kuma fa nace masa in za shi ya sanar min dan nima ina son zuwa"

Hannu ya zare daga wainar da yake ci ya wanke, da sauri ya mik'e tsaye.

"Dady bari nabi bayansu"

Cike da mamaki Dady ya ce.

"Haba Yasir da sauri haka, ka bari mana wani lokacin sai ka tafi"

Murmushin yak'e ya yiwa Dady.

"Kumin Addu'a kawai Dady, amma dole na tafi yanzun nan"

Dady ya ba shi 10k shima yasha mai, ya amsa ya yi musu godiya da fatan alkhairi ya wuce. Yana fita ya shiga mota ya bata wuta sai Kd, tun a hanya yake kiran Sadiq amma yaki d'agawa, parking ya yi ya tura masa text.

_"In ka gama wulak'ancin ka turo min address d'in gidanku na Kaduna din nima ina bisa hanya"_

A lokacin Sadiq sun kusa shiga Kaduna, duk yana jin shigowar kiran amma yak'i d'auka, yaji shugowan text shima sai ya share.

********   ***   ********

*Kaduna*

Bayan sun isa Sadiq ya yi parking a harabar gidan ya d'auki wayarsa ya duba, text kawai ya turawa Yasir na address d'in gidan, kana ya waiga wurin Husna ya ce.

"Baby mun k'araso, yanzu ki ja mayafinki ki rufe fuskarki sannan ki natsu da kyau sai nace ki yi magana sannan za ki yi, kuma ki toshe kunnenki da duk abin da za ki ji, ki yi hakuri komai zai

wuce kin ji"

Hudna ta gyad'a masa kai alamar ta gamsu, sannan ta ja gyalenta kamar yadda ya yi mata umarni, fitowa suka yi ya kira mai gadi ya shigar musu da kaya cikin babban falon gidan, Sadiq ya doshi k'ofar falon zuciyansa na dukan uku-uku, dakewa ya yi ya matse ya shiga, Husna na biye da shi, tana ganin ya shiga ta ja ta tsaya a bakin k'ofa. Sadiq ya tadda su Baffa, Abba Aliyu mahaifinsa sai Abba Ismail, da alama hira suke yi, da yake weekend ne ko wanne yana gida, ganin Sadiq ne ya katse musu hiransu suka zuba masa ido harya k'araso cikin falon ya zauna a k'asan carpet Kansa a sunkuye, duk tunaninsa Husna ta shigo sai ya waiga yaga wayam bata shigoba, tunani ya fara yi.

'Mai ya hanata shigowa?'

Baffa ne ya katse masa tunaninsa da cewa.

"Babban Mutum yau kaine a gari, na yi tunanin sai mun ciko mota mun zo har garin Kano biko"

Murmushi ne ya kubce masa ya ce.

"Baffa kusha zamanku Ku huta gani tafe da kaina, da fatan na sameku lafiya?"

"To masha Allah, lafiya lau muke"

Daga nan ya gaishe da iyayen nasa, Abba Ismail fuskansa sake ya amsa, amma Abba Aliyu kuma fuska murtuke ya amsa ba yabo ba fallasa, falon ya d'auki shuru, Abba Aliyu ne ya d'auki wayarsa ya kira Ammi Jidda ya ce.

"Ki zo ga d'anki ya dawo da kika matsa min dole saina kira shi, to gashi nan ya yi kiba ya samu natsuwa hankalinsa kwance ya manta damu, amma ke kin kwallafawa ranki damuwa bai san kina yi ba"

Yana kaiwa nan a maganarsa ya kashe wayan ba tare da ya jira mai zata ce ba, Sadiq ya d'ago suka had'a ido da mahaifinsa sai ya harare shi ya kauda kai gefe, tunaninsa ya zai mik'e ya je ya shigo da Husna dan ayi ta ta k'are.

Tab'angaren Husna kuma tana tsaye tana jin tsoron ya zasu amshe ta, hankalinta tashe, tana sak'a da warwara na mafita, dole ta yanke shawarar shiga dan ba tada wata mafita illa yin hakan, kanta a sunkuye rufe da mayafi ta k'usa kai ciki da sallama, shiganta ya yi dai-dai da shigowar Ammi Jidda, kallone ya koma kan Husna kowa yana tunani wace bak'uwa suka yi ne da safiyan nan, wurin da Sadiq ya zauna can ta nufa ta zauna gefen damansa, mamaki ne ya cika fuskokin su Baffa, sun kasa furta komai sai kallonsu da suke yi, kafin wani ya jefo tambaya, Sadiq ya risinan da kai k'asa ya ce a hankali Husna ki gaishe su, kanta na sunkuye rufe da mayafi bata d'agoba ta gaidasu, babu wanda ya iya amsawa saima kalon-kallo da suka shiga yi

da juna, Ammi ce data shigo ta ce cikin d'aga murya.

"Sadiq wacece wannan?"

Dam dam yaji zuciyar shi ya buga, haka ma ta b'angaren Husna, sosa kai ya fara yi cikin inda-inda ya ce.

"Matata ce"

A zabure Abba Ismail da Abba Aliyu suka mik'e tsaye, Baffa ko mai da bayansa ya yi ya jingina da bayan Cushing da yake zaune a kai, Ammi Jidda kuwa wasu zafafan hawaye ne suka shiga zarya a kumatunta. Da sauri ta fita ta isa sashin Umma cikin kuka ta ce mata ta isa babban falo, Umma na tambayanta me ya faru bata iya bata amsa ba ta wuce sashin Mami Ameena nan ma abin da ta cewa Umma shiga gaya mata, haka ta gaya wa Anty Zainab duk suka tawo falon a sukwane. Haka duk suka tsaya cirko-cirko kamar yadda suka ga su Abba Aliyu a tsaye, mamaki ne a fuskokinsu wanda kallo ya koma gurinsu Sadiq, Baffa ne ya yi k'arfin hali ya ce musu duk su zauna, ba musu kowa ya samu wuri ya zauna, harda su Khadija, Baffa ya kai kallonsa ga Sadiq ya ce.

"Yaushe kuka yi aure? kuma a ina? sannan wasu iyaye ka samu wanda suka fi maka mu?"

Ba k'aramin kad'uwa su Umma suka yi ba kanma Anty Zainab da take da tabo akan haka. Gumi Sadiq yake yi wanda duk sanyin falon baya jinsa, kansa sunkuye ya ce.

"A Kano aka d'aura, wata d'aya kenan da kusan sati biyu, a can na samu iyaye da suka yi min wakilci akan auren"

Zabura Abba Aliyu ya yi yana huci.

"Kai har kana da bakin bayani ko sha-sha-sha, wallahi tun kafin in ta shi in yi k'asa-k'asa daku ku fice a gidan nan, na tsameka daga zura'armu, bamu ba kai kaje can wurin iyayen daka sake"

Hawaye mai zafi ya fito ma Sadiq ya ce.

"Abba kuyi hak'uri ku yafe min, wallahi akwai dalilin da yasa na yi wannan auren, kaddara ce"

Ammi Jidda ta ce cikin muryan kuka.

"Rufe mana baki wallahi, Sadiq ka bani mamaki, maza tashi ku koma in da kuka fito"

Ai Husna kuka ta b'arke da shi, ta matsa kusa da Sadiq ta rik'e hannunsa tana cewa.

"Uncle tashi mu tafi kafin su dukemu"

Zan iya cewa Sadiq ne kad'ai ya iya sanin me take cewa, Abba Ismail ya ce.

"Ko baka ji abin da aka ce maka bane? ta shi kabar gidan nan maza, tun kan raina ya gama b'aci"

Mami Amina ta ce.

"Dan Allah ku barsu mu ji abin da yasa hakan ya faru, bai kamata a yanke hukunci cikin fushi ba kuma..."

Wani mugun kallo ne da Abba Ismail ya wurga mata wanda yasa dole ta yi shuru ba tare da ta gama fad'an abin da ke bakinta ba, Umma kuwa ta kasa magana banda rafka tagumi da ta yi, Anty Zainab kuwa kuka take yi sosai tana kaicon abin da ta aikata, da bak'in cikin k'addarar da bai tsaya kanta ita kad'ai ba.

'Wannan wace irin k'addara ce?'

Khadija ko lafewa ta yi jikin Maminta tana kukan bak'in ciki da abin da masoyinta ya yi, Sadiq ya kama hannun Husna ya mik'e bai iya furta komai ba face hawaye dake gudana daga idonsa, har sun isa bakin k'ofar fita, Anty Zainab ta ruga da gudu ta kama hannun Sadiq cikin kuka ta ce

"Ba in da zasu dole ne su zauna a gidan nan, sannan ma bakwa tunanin abin da ya faru ne a baya? in har aka kori Sadiq to ba ayi adalci ba, tunda nima ba a koreni ba, kuma dole ne a gyara wannan kuskuren gudun kar gaba ya kuma faruwa. Ai Allah ya nuna mana ishara ce akan irin hukuncin da kuka zartar a kaina a baya, kuka rabani da masoyina akan k'addarar da ubangiji ya rubuta akanmu, dan haka dole ne yanzu mu amsheta mu yi imani da hakan, ko Allah zaisa wannan ya zama k'addara ta karshe a garemu, ko kun manta Allah ya ce muyi imani da k'addara mai kyau ko mara kyau"

Ta k'arasa maganar da kuka, jikinsu ne duk ya yi sanyi hak'ik'a maganar Anty Zainab ya yi tasiri a zuciyoyinsu, Baffa ne ya nisa ya ce.

"Sadiq Ku dawo ku zauna"

Ba musu suka dawo suka zauna, Anty Zainab ma ta koma ta zauna duk suka yi shuru.

Yasir ya shigo Kaduna yana tabin address d'in da Sadiq ya tura masa, harya zo dai-dai gate d'in gidan, suka gaisa da mai gadi ya ce

"Malam, dan Allah ina ne gidan Alhaji Ahmad Mai Kanti?"

mai gadin ya yi murmushi ya ce.

"Ai ka zo gidan, dan nan ne"

Cikin sauri ya bud'e mota ya fito.

"Sadiq na ciki?"

"Eh, basu jima da zuwa ba, yana ciki"

Key motar Yasir ya bama mai gadi.

"Ka iya mota?"

"Eh"

"Ok, shigo min da ita ciki"

Bai jira mai zai ce ba ya shi. A falo Baffa ne ya ce.

"Sadiq ka gaya mana ya wannan auren ya kasance? sannan meye dalilin ka na yinsa ba tare da sanin muba?"

Yasir ya shiga falon a dai-dai Baffa yana wa Sadiq wannan tambayar, caraf Yasir ya amsa da cewa.

"Nine na had'a auren, Sadiq bai da laifi, nine nan mai laifi"

Ya nuna kansa, ai kallo sai ya koma wurin Yasir, mamaki ya rufe su Baffa, gashi dai bak'on fuska ne basu waye sa ba.

*Cakwakiyar tana nan*
[11/4, 7:20 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 63 ~ 64_*

Baffa ya ce.

"Bawan Allah k'araso ciki ka mana bayani dan bamu wayeka ba"

Cikin sauri Yasir ya k'arasa kusa da Sadiq gefen damansa ya zauna, yabi 'yan falon da kallo wanda suma kallonsa suke yi, daya kai kallonsa ga Anty Zainab sai ya kura mata ido cike da mamaki a fuskarsa, kamar Husna ya hango a fuskarta, abin da ya yi banbanci Husna ta fita haske sannan tafi yarinta sosai amma da ka gansu kasan akwai had'uwar jini a tsakaninsu. Baffa ne ya katse masa tunaninsa da cewa.

"Kai yaro muna sauraron ka"

Nan Yasir ya gabatar musu da kansa da kuma yadda suka had'u da Sadiq har suka k'ulla abota, kana ya yi musu bayanin yadda aka yi Sadiq ya auri Husna da yadda ya had'a auren, cike da mamaki mutanan falon suke kallon Yasir, bayan ya gama ya cigaba da cewa.

"Sauran bayani yana gun Sadiq"

Sadiq ya d'ago suka kalli juna kana.

"Ai ka gama gaya musu abin da ya faru"

Yasir ya yi murmushi.

"Sadiq ya zama dole yau ka sanar da iyayenka yadda ka had'u da Husna, domin b'oye-b'oye bai da wani amfani"

Anty Zainab na jin an ambaci Husna taji gabanta ya yi mummunar fad'uwa, wanda ita kad'ai ta iya tunawa da 'yarta Husna a cikin wannan yanayin. Abba Ismail ya nisa ya ce.

"Kai Sadiq maganar b'oye-b'oye ya k'are ka gaya mana asalin yadda ka had'u da wannan yarinya, hakan shi ne zai sa mu gamsu da duk kan bayanin da abokinka ya yi mana yanzu"

Sadiq ya risinar da kai.

"To Abba"

Ya ce tare da gyara zama ya cigaba da cewa.

"Na had'u da Husna tun tana k'arama wato tana da shakara bakwai zuwa takwas a lokacin"

Daga nan ya cigaba da basu labarinta wanda ya sani da wanda ya samu labari wajen Baba mai gadi, da duk irin wahalar da ta yi na rayuwar k'unci da *kad'aici*, da azabar da Momy ta gana mata har haukan data d'aura mata, da asirin da ta yi ta raba ta da Dadynta harya zuwa tonuwar asirinta, da karyewar asirin da ta yiwa Dady, har zuwa had'asu aure da Dady ya yi da komai ya zayyana musu. Ai tambayoyi ne cike a zuk'atan su Baffa bama ga Anty Zainab wanda kuka ya wanke mata fuska, su Ammi Jidda, Mami Amina Umma dama Khadija duk hawaye suke yi da tausayin irin wahalar da Husna ta sha, Abba Ismail da Abba Aliyu duk jikinsu ya yi sanyi, falon ya yi shuru na mintuna bayan Sadiq ya yi shuru, shashshekar kukan Husna ce kawai ke tashi a falon, sun zauna jugum-jugum kamar wanda aka yi musu mutuwa, Baffa ne ya yi gyaran murya cikin sanyin jiki ya ce.

"Sadiq meyasa tun farko baka yi mana bayanin halin da yarinya nan take ciki ba? Ai ina ganin da mun ji duk wannan bayanin ba mai hanaka aurenta, yanzu ma shin shi mahaifinta ya san cewa ba mune muka nima maka aurenta ba mu da muke ainahin iyayenka?"

Sadiq ya ce.

"Gaskiya bai sani ba saboda duk wannan aikin Yasir ne, Kawunsa ya nima auren kamar yadda ya muku bayani"

"To yanzu ya za'ayi mahaifinta yasan da mune iyayenka, sannan mu ba shi hak'uri mu nuna masa kuskurenmu tunda tun farko mune muka jawo faruwan haka, saboda k'in amincewar mu"

"In mun koma zanje na yi masa bayanin komai, in ya so sai na kiraku a waya yaji daga bakinku"

"To shi kenan, ya sunan mahaifin nata inya so sai ka bani numbern sa, in kun koma sai na kira shi, domin kuwa mune ya kamata mu fara nimansa"

"Sunansa Alh. Khalil"

Ai kan ya rufe baki Anty Zainab ta zabura ta mik'e tsaye tana nuna Husna da yatsa, su Umma shock suka ji wanda hatta Baffa sai da yaji gabansa ya fad'i, Abba Ismail da Abba Aliyu mutuwae zaune suka yi suna tunanin faruwar wani abu, kallo ne ya koma wanjen Anty Zainab ta isa wurin Husna da sauri ta fincike gyalen da ta rufa da shi, tuni tsoro ya ziyarci Husna ta tsandara ihu ta k'ank'ame Sadiq, tunaninta ko dukanta zasu yi, ai mutuwar tsaye Zainab ta yi tana bin Husna da kallo tare da fitan zafafan hawaye ta waiga tana kallonsu Anty Jidda ta ce da k'arfi.

"Anty Jidda wallahi Husnata ce,wallahi 'yata ce, ita ce Allah"

Sadiq ya zaro ido kamar zasu fad'o waje ya ce cikin tsoro.

"Anty ban gane ba wai meke faruwa ne?"

Yasir ya yi murmushi ya ce.

"Sadiq ka natsu yanzu zamu gane komai"

Anty Jidda da sauri ta taho wurin Husna ta fincikota jikin Sadiq da k'arfi, ta daka mata tsawa saboda taki tsayawa, cikin tsoro Husna ta tsaya cak tana kallon mutanan falon idonta wanke da hawaye, Khadija ta mik'e da sauri ta ce.

"Husna dama ke ce? Mami wallahi ita ce k'awata da kullun nake baki labarinta, wallahi Husna ce"

Itama Husna bin Khadija ta yi da kallon mamaki, ai tuni salati da salallami ya cika falon kowa na fad'an albarkacin bakinsa, Baffa ko jikinsa mutuwa ya yi yana kallon wani ikon Allah.

"Ameena a shekarun baya na taba gaya miki wata mata ta kawo min wata yarinya asibiti, dan na bata maganin da zai haukatata, tabbas wannan yarinyar ita ce, innalillahi wa inna ilaihir raji'un! Kaiconmu! Rashin sani, ashe d'iyata ce, Allah ya kiyaye ban bata ba"

Cewar Abba Isma'il ya dafe kansa cike da jimamai.

"Kwarai Abban Khadija na tuna, wannan shi ne ikon Allah mai yin yadda ya so"

Cewar Mami Ameena, Ammi Jidda ta ce.

"Husna a she dama zamu sake tozali da ke?"

Sai ta rungume ta ta saki kuka, Sadiq ya kuma rud'ewa ya ce.

"Dan Allah ku min bayani, karku sanya na zauce"

Cikin kid'ima yake magana, Abba Aliyu ne ya yi gyaran murya ya ce.

"Ke Jidda samu wuri ku zauna domin a samu fahimta"

Ba musu suka zauna taja hannu Husna, aiko tak'i yarda dole ta koma wurin mijinta Sadiq, ta d'aura kanta a kafad'arsa tana kuka, ita kanta ta gaza gane komai sai rud'ani da ta tsinci kanta a ciki.

Falon ya yi tsit kamar bakowa aciki sai k'aran fanka dake juyawa, Baffa ya ce.

'Sadiq bani number Khalil"

Jin haka mamaki ya kuma cika Sadiq, ba musu ya karanto mishi number daga wayansa, Baffa ya yi dialing number a wayarsa ta soma ringing, bugu biyu Dady ya d'auka ya kara a kunnensa tare da sallama, suka gaisa, Dady ya ce.

"Amma Alhaji ban wayeka ba, ko zaka min bayani domin number nagani"

Baffa ya yi jim da yake wayar yasa a hand's free duk mutanan falon suna ji, Baffa ya ce.

"Sunana Alh. Ahmad mai kanti, Baffan Zainab"

Ai kan ya k'arasa fad'a cikin Dady ya yi kulululu, saboda bai tab'a tsammanin haka daga dangin

Zainab ba, ya nisa ya ce.

"Baffa ka yi hakuri ban wayeka ba ne da farko"

Nan ya kuma gaishe shi cikin mutunci.

"Khalil in ba damuwa ka zo Kaduna yau ina son ganinka a gidana, wancen karan mune muka kore ka, wannan karon kuma ina mai baka hakuri ka zo dan Allah ba dan abin da muka aikata maka ba"

Jikin Dady ya yi sanyi ya ce.

"Baffa ai kai uba ne a gareni, ba sai ka bani hakuri ba zan zo insha Allah yanzu, da fatan dai lafiya?"

"Lafiya lau"

"To ganin zuwa"

Nan suka yi sallama suka aje kan wayar. Cike da mamaki Khalil yabi wayar da kallo, cikin sauri ya ta shi ya kimtsa, part d'insu Baba Husain ya je ya sanar musu da abin da ke faruwa, ai nan Baba Husain ya ce da shi za ayi tafiyan, Inna ma ta ce da ita za ayi, cikin k'ank'anin lokaci suka shirya sai Kaduna.

*****

A nan falon kuma Baffa ya ce kowa yaje ya natsa har kafin zuwansu Dady Kaduna, ba musu kowa ya mik'e cike da jimami da tunanin wannan bak'on lamari mai cike da abin mamaki, ta b'angaren Zainab kuwa ta kama hannun Husna don suje part d'inta amma tak'i yarda, dole Anty Zainab ta rabu da ita ta wuce d'akinta tana mai zubda kwalla, Mami Ameena dasu Umma tausayinta ya kama su, Abba Ismail da Abba Aliyu kuwa a yau suka k'ara dana sanin raba aurenta da suka yi da Khalil, ga shi ba aje ko ina ba Allah ya nuna musu ikonsa.

Da misalin k'arfe biyu na rana su Dady sun iso, da yake motar gida ne kuma tafiyar sauri suka yi, anyi musu masauki a babban falon gidan kana aka cika su da abinci kala-kala da abin sha, Suka d'an ci, kana Baffa ya fito suka gaisa cikin mutunci sannan ya d'auki waya ya sanar da duk mutanan gidan da su fito babban falo, d'aya bayan d'aya suka soma shigowa, Sadiq ne suka shigo shi da Husna, Dady ya kallesu cike da mamaki ya ce.

"Kai Sadiq meya kawo kunan dama kasan mahaifiyar Husna ce?"

Tambayar daya jeho masa, sai ya k'ara rikita Sadiq, idonsa sun yi ja ya ce.

"Dady nima na kasa gane wannan sark'ak'iyar, nan gidan family house d'inmu ne"

Cike da mamaki Dady ya ce.

"What"

Sai ya bi 'yan falon da kallo bai ga Zainab ba, Baffa ne ya ce.

"Kuyi hak'uri komai zai warware yanzu, wai ina Zainab ne? Ke khadija ta shi ki je ki kirata..."

Baffa bai rufe baki ba sai gata ta shigo kamar an jehota, har wata 'yar rama ta yi na damuwa, tsayawa ta yi cak ta kasa k'araso wa, Dady ya kura masa ido ko kiftawa baya yi, ita ma shi take kallo hawaye na malala a kuncinta, shima Dady hawaye yaji ya cika masa ido sai ya yi na maza ya danne su dan karsu zubo, ya mai da kallonsa ga Husna da ta takure a jikinsa ya ce.

"my Husna ta shi ki je gun Mahaifiyarki"

Cikin razana ta d'ago kai tana kallonsa.

"Dady wacece Momy na?"

Ya nuna mata Zainab da hannu.

"Gata can a tsaye jeki shigo da ita cikin falon"

Ido bud'e cike da tsoro take kallon mutanan falon, Baffa ne yasa baki ya ce.

"Jikata je ki wurin Mamanki, ita ce ta d'auki cikinki na wata tara kana ta yi nak'udarki kika zo duniya"

Cikin mutuwar jiki Husna ta mik'e tana kuka tare da jan k'afa don ta isa gunta, ji ta yi k'afarta ba zai d'auketa ba ta tsaya cak cikin tsakiyan falon, kanta ne taji yana juyawa ya yi mata nauyi kamar ba nata ba, wani razanan nan ihu ta saki ta fad'i k'asa sumammiya.

Dady, Sadiq, Anty Zainab, Abba Ismail, Abba Aliyu, dasu Anty Jidda, Umma da Mami Ameena, suke yi kanta da gudu har suna bangazan juna, Dady ne ya ce a kawo ruwa, aka kawo ruwa kana ya zuba a kofi ya yi tofin Addu'a a ciki ya soma watsa mata a jiki da fuska, wani k'aran ta saki, ta ta shi zaune tana huci tana furzar da miyau ta ce kakkausar murya.

"Karku k'onani ni masoyiyarku ce, bana nufin cutar da kowa, dan Allah ku rabu dani"

Dady ya ce.

"To ki tafi ki rabu da rayuwarta in dai ke musulma ce"

"Eh ni musulma ce, na shiga jikinta tun tana k'arama ni ke bata kariyar wasu abubuwa saboda rayuwar *kad'aici* data ke ciki"

Nan ta yi ta surutu, ta k'ara basu labarin yadda Husna ta yi rayuwar *Kad'aici* da rashin gata, ta nuna su Abba Ismail da Abba Aliyu ta ce.

"Duk kune kuka ja komai, kuka rabata da mahaifiyarta, kuka raba musu aure, harda kai Baffa saboda wani ra'ayinku na daban"

Nan dai ta yi ta surutu daga bisa ni ta ce.

"Dama wannan rana nake son gani in ga Husna ta ga mahaifiyarta, dan haka zan tafi ba zan sake dawowa gareta ba dama rayuwar *kad'aici* da take ciki ne yasa na shigeta, na tafi, na tafi"

Husna ta saki wani ashiwa mai k'arfi sai ta koma luuuu zata fad'i, Sadiq ya tare ta da hannunsa ta fad'a jikinsa.

Ta kai minti biyar a haka kana ta ta shi tana waige-waige, caraf ta had'a ido da Mominta cikin kuka ta ta shi zaune, da rarrafe ta isa wurinta ta rungumeta kamar zata koma cikin cikinta, wani nannauyar ajiyar zuciya duka suka saki, kana Zainab ta d'agota suna kallon juna suka sakarwa juna murmushi, Husna ta ce cikin shagwaba.

"Momy dama kina raye? ki min alk'awari ba zaki sake nesa dani ba, na yi kewar ki ba adadi"

Cikin nuna so da k'auna Zainab ta ce.

"Wace ni, ai muna tare mutu ka raba 'yata"

Duka falon suka sa dariya, amma banda Dady daya sha kunu, ko meye dalili oho.
[11/5, 8:38 AM] Rahma Kabir🌺: *_Page 65 ~ 66_*

Nan suka kara gaisawa daga bisani Baffa ya d'aura da cewa.

"Sadiq da Husna ina so ku sani ku 'yan uwa ne, Zainab ita ce mahaifiyar Husna, Aliyu shi ne mahaifin Sadiq wato yayan Zainab kenan"

Daga nan ya d'aura da bayanin yadda auren Zainab da Khalil ya faru, bayan ya kai aya Yasir ya d'aura da bayanin yadda ya had'a auren Husna da Sadiq, aiko Dady ya cika da mamaki da jinjina wannan lamari na Allah, wanda babu wanda ya isa ya yi shi sai shi kad'ai Allah mabuwayi gagara misali, wannan kad'an kenan daga cikin ikonsa in yaso ya had'a ko ya raba, babu abin

bautawa da gaskiya sai shi kad'ai Allah, wanda babu wani bayan shi. Falon ya d'auki shuru kowa na jinjina wannan abin ta'ajibi hak'ik'a aya Allah ya nuna musu domin shi da ya had'a shi kad'ai yasan dalilin had'awar, su Baffa sun amshi kunkurensu kanma Abba Ismail da Abba Aliyu da suka yi ruwa su kai tsaki akan raba auren Zainab da Khalil, Sadiq ya jinjina lamarin a she iyayensa sune masu lafi dumu-dumu, sannan kuma shiyasa yake jin Husna a a zuciyarsa tamkar jini da tsoka, ya yi murna da aurenta ya zama silar had'uwar dangi da kuma nunawa su Abba kuransu.

Nan Khadija ta matsa kusa da ita ta ce.

"Husna shiyasa nake jinki sosai a raina a she ke 'yar uwa ta ce, nagode Allah da yasa kika zamo cikin ahalina, kuma a yau nake sanar da cewa, na hakura da auren Yaya Sadiq, na bar mini shi har abada dan ba zan iya miki butulci ba"

Nan falon ya gauraye da murna suka shiga sanyawa Khadija albarka, Yasir ne ya sunkuyar da kai ya ce.

"Baffa ni fa ina kamu dan ina son Khadija"

Baffa ya yi dariya.

"Madallah, Yasir na baka ita amma fa sai ta amince, dan yanzu mu dangin nan namu babu mu ba auren dole, ko wani naji zai yi haka sai na masa nasiha ya gane illan yin hakan"

Khadija cikin jin kunya ta sunne kai k'asa, Husna cikin dariya ta ce

"Baffa ita ma ta amince tunda ga shi sai dariya take yi"

Duka Khadija ta kai mata ta ce.

"Wayyo Momy na kin ganta ko"

Nan falon ya cike da dariya, sai hira da raha suke yi da murna, sannan suka yafi juna bisa abin da yafaru a baya. An kira Sallan la'asar dole suka mik'e dan gabatar da sallah. Falon ya watse mazan suka nufi masallaci su Umma suka shiga ciki, musamman aka gyarawa su Baba Husain wani part a gidan. Zan iya ce muku wannan family sun kwana cikin farin ciki mara misaltuwa wanda suka jima ba suyi ba.

*****

Ranar Juma'a bayan an sakko masallaci aka d'aura Auren Zainab da Khalil su Baffa suka yi komai hatta sadaki, sannan aka kuma d'aura Auren Khadija da Yasir wanda Dady shi ne ya yi masa wakilci ya biya sadaki da komai, sannan aka d'aura Auren Zahra k'anuwan Sadiq da angonta Jabir wanda suka jima suna soyayya. an kira dangin Yasir an sanar musu,

mahaifiyarsa ma ta zo nan Kaduna da kannensa da wasu danginsu.

Bayan an d'aura Aure aka shirya gagarumin liyafa a wani babban hol dake nan Kaduna, wanda sai wanda suka jik'e da naira suke shagalin biki a gun. Zainab ta yi kwalliya kamar ba ita ba sai wani tseki da kyalli take yi, Dady shima ya yi kyau fuskansa cike da murna amma fa suna had'a ido da Zainab sai ya gimtse fuska ya galla mata harara, murmushi take masa domin ta san dalilin hararen saboda taki bari su kebance shiyasa yake cin magani, su Husnahm kuwa murna baya misaltuwa sai wani dad'i take ji ta mance komai na rayuwarta ji take kamar an sake haifo ta ne saboda farin cikin da take ciki, haka gogan naku Sadiq fad'en farin cikinsa ma b'ata baki ne sai wani murmushi yake yi, a fagen rawa kuwa sun cashe shi da Husnarsa kamar ba suba, ni kaina na yi mamaki nace ashe dama su Sadiq suna dariya haka sai wani rawa suke na burgewa. Ango Yasir da Amarya Khadija abin ba'a magana dan bakinsu ya kasa rufuwa, sai iya yi su keyi su Khadija dama ba kunya sai rawar kai, suma kam sun yi kyau kuma sunyi matching sosai, su Zahra ma da Angonta ba'a barsu a baya ba, sun yi kyau kuma suma sun cashe sosai abin gunin sha'awa, anyi shagali an washe duk sun dawo gida.

*******    *******

*Washe Gari*

Aka shirya Momy Zainab tare da Amarya Khadija domin kaisu gidan mazansu a Kano, su Sadiq ma ba'a barsu a baya ba suka kwashe komatsensu suka bi sahun Amare. Amarya Zahra a nan kd aka kai ta gidanta dake marafa.

Kusan duka gidan aka dunguma sai Kano hatta su Baffa sun bisu dan suga wurin dasu Khalil suke zama da kuma Husna, suna isa suka dire a gidan Dady, wanda danginsa sun cika gida dan tarban Amarya,  Momy Habee cike da mamaki take kallon su, an sauke Momy Zee a part d'in Dady wanda ya sha gyara duk an canza kayan d'akin an zuba sabbi, Zainab ta kalli d'akin da kyau ta ce.

"Hmmm yau naga auren gata, ji yadda aka kashe kud'i sai kace wata budurwa"

Mami Ameena ta yi dariya ta ce.

"Wannan aikin mijinki ne ba kud'in Baffa a ciki, kuma ai ke yanzu 'yar gata ce kuma kamar budurwar kike a gunsa"

Ta lumshe ido ta yi murmushi kana suka ci gaba da hira.

Bayan komai ya lafa suka had'u a babban falon gidan, Dady ya ce
Husnah ta kira masa Haj. Habee, Husna taja hannun Khadija suka isa part d'in Momy Habee, sun sameta gefen gado tana zaune ta zabga tagumi, cikin murna Husna ta isa wurinta ta ce.

"Momy ina yini"

Firgigit ta d'ago kai ta ce.

"Husna yaushe kika zo?"

"D'azun nan muka zo, Dady ya ce ki zo falo mun yi bak'i"

Haka suka dunguma suka isa falon, Momy ganin bakin falon yasa jikinta ya yi sanyi, gefen can ta samu ta zauna ta soma gaishe su, sannan ta kai kallonta ga Dady ta ce.

"Alhaji gani"

"Yauwa, Habeeba ga dangin mahaifiyar Husna nan, wannan ita ce Zainab wato mahaifyar Husna jiya aka mai da Aurena da ita, dalilin kiran ki da na yi dama shi ne, na shaida miki cewa Husna bata hanyar zina na sameta, saboda kinsa fad'ar haka"

Momy idonta na kan Anty Zainab tana mamakin kamarta da Husna, sun kuyar da kai ta yi cike da jin kunya, kwalla ne ya cika mata ido har ya zibo ta soma hawaye ba tare da sauti ba, ta d'ago ido wanda suka rine suka yi ja ta ce.

"Dan Allah ku yafe min bisa ga mugun rik'on da na yiwa Husna sharrin shaidan ne da zuciya, alhakin ta ma nasan Allah ba zai barni ba"

Ammi Jidda ta ce.

"Ba zamu yafe ba munafuka"

Umma ce ta katseta.

"Haba Jidda ai muma muna da laifi dan haka ke Habeeba kike ko wa, ki je mun yafe, Allah ya yafe mana gaba d'aya"

Duka falon suka amsa da Ameen. Baffa ma ya d'aura da nasiha da kuma jan hankali game da amana da daraja dan Adam. Nan Dady ya musu bayani cewa.

"Idda Momy Habee take yi a gidan dan ya saketa, kuma da zarar ta gama zata tafi"

Kuka ne yaci k'arfinta ta tashi da gudu ta nufi d'akinta. Duk sai tausayinta ya kama su amma fa banda Dady, Nan sukaci suka sha.

Da yamma aka d'auki Khadija aka kai ta gidan mijinta, wanda gidansu daya da Husna d'ayan

part d'in Sadiq yasa aka gyarawa Yasir dan su zauna tare kafin Sadiq ya gama gininsa. Da yamman nan su Baffa suka koma Kaduna akabar gida kowa ya watse sai masu gidan.

Husna sai dare Sadiq ya zo ya d'auketa suka nufi gidansu. Suna isa part d'in Khadija ta nufa, Sadiq ya zauna a barandar gidan kan kuje ta yana jiran zuwan Ango da abokansu.
Bayan sun k'araso aka yi siyan baki kowa ya kama kansa. Khadija har da kuka wai Husna ba zata tafi ba da kyar ta saketa ta wuce part d'inta. Ta samu ta watsa ruwa ta yi shigan barci da shegun wani rigan barci ruwan hanta iya karta rabin cinya ya tsaya mata, ta d'aura k'afa d'aya kan d'aya a kujera tana kallon TV tare da shan ice cream da Sadiq ya siya mata a hanya. Gogan naku shima ya fito da wani wando tree quarter sai riga mai guntun hannu fara tas, wandon ma fari, da murmushi ya k'arasa wurinta ita ma tana mayar masa da martani, yadda suke jefar junansu da wani sihirtaccen kallo da gani kasan sunyi missing juna, yana zuwa ya karb'e robar ice cream d'in ya ce.

"Baby Hussy bana so mura ya kamin baby na dake cikin ki"

Da wani irin kallo ta bi shi ta ce cikin sigar kallon d'aukar hankali.

"Nifa ban isa haihuwa ba"

Dariya ya yi ya jawota jikinshi ya ce.

"Ok na ji, amma bari naji da kyau in baki isa ba"

Jawota ya yi jikinsa tana mutsu-mutsu tana son zillewa, matseta ya yi a jikinsa, kafin ta yi aune ya had'e bakinsu waje d'aya tare da sarrafa harshensa a ciki, tuni ta saki jiki ta suka fad'a wani duniyan, ina ganin haka nima na kama kaina na nufi gidan Dady.

Na tadda Dady da Momy Zee sun idar da Nafila na godewa Allah daya k'ara nuna musu wannan rana a matsayin ma'aurata, nan Dady ya ce.

"Zee na"

Ta d'ago ta kalleshi tare dayi masa fari da ido ta ce.

"Naam my Khalil"

Lumshe ido ya yi ya bud'e, ya mik'e tare da yin shirin barci, d'aukanta ya yi chak ya direkan bisa kan gado yana mai fidda nishi ya ce.

"Kai my Zee kin ji yadda kika k'ara girma, gaskiya da alama ko tunani na ba kya yi, ni kam ji yadda na lalace tunda na rabu dake ban sake farin ciki ba, sai ranar dana aurar da Husna da kuma ranar yau"

Murmushi ta yi ta ce.

"My Khalil kusan kullun dare sai na zubda kwalla, da tunaninka nake kwana wasu lokutan harda mafarkinku nake yi kai da Husna, kullun Addu'a nake Allah ya sadani daku cikin aminci, kuma ina ji a jikina zan had'u daku, shiyasa tun mutuwar yaya Al'amin nak'i yin Aure, na samu manema sosai amma nak'i yarda, su Umma sunyi mita sun gaji haka suka hak'ura suka cigaba da min Addu'a, kaga kuwa kana raina Mijina"

Khalil cike da farin ciki ninke a zuciyansa ya rungumeta tsam har suna jiyo bugun zuciyan juna, tuni suka farfad'o da soyayya, suka fara tuno tsantsar soyayarsu ta da, take nan suka fara faranta ran junan had'e da nunama juna tsantsar missing da suka yiwa juna. Ganin wannan yana yi da suka shiga na shayar da junansu zumar kauna, sai nima na lallab'a nayo waje dan sanin sirrin ma'aurata sai Allah.

Ta b'angaren Amarya Khadija da angonta Yasir da amarya Zahra ita ma da angonta Jabir, suna can suna gwangwaje soyayya mai cike da so da kauna da tarin tarihi.
To ma'aurata Allah ya baku zaman lafiya. Ameen.

Su Baffa suma sun kai Kaduna kowa ya kwanta yana huta gajiya. ta b'angaren su Baba Husain suma suna part d'in su sun kwanta suna huta gajiya.

Ta wajen Momy Habee kuwa barci ya k'aurace mata sai jiyu take, ta yi kukan ta gaji, nadama ya cika zuciyarta, tana tunanin yadda taga mahaifiyar Husna sai da ta raina kanta, gata matashiya kuma ga kyau ta had'a komai da namiji yake so, a yanzu ta kuma sadak'arwa Khalil ya mata nisa, tasan tunda ya mai do da Zainab tofa ba wata mace da zata kuma samun k'ofa a ziciyarsa. Da tunani barkatai barci ya yi a won gaba da ita.
[11/6, 6:42 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 67 ~ 68_*

*Bayan wata d'aya*

Khalil da Zainab suna ragargaza love hankalinsu kwance ba ruwansu da wani, hakan yasa Momy Habee ke yini a d'aki saboda sam bata sakewa in suna babban falo, domin idonsu rufewa yake su yi ta soyewa ba ruwansu da tana wurin, Momy Habee har mamaki take yi yadda taga Khalil ya saki jiki sai soyayya yake yi ga fara'a da sakin fuska ba kamar yadda yake mata ba, lallai ta san ita ya aureta ne dan kawai ta tusa kanta ne ba dan soyayya, tunani ta farayi na barin gidan domin hakan shi ne samun kwanciyar hankalinta.

Zainab tana falo zaune bisa kujera tana nazarin wani littafi sallama ta ji anyi tare da shigowa, Husna ta isa da gudu ta rungumeta suna murna sosai da ganin juna, in kuka gansu sai sun baka shawa'a, Momy Zee ta ce.

"D'aga ni karki karya ni, ina shi Sadiq d'in ya tsaya bai shigoba?"

Husna dariya ta yi, ta d'aga mata d'in key mota ta ce.

"Da kaina na zo"

Ido Momy Zee ta zaro.

"Yaushe kika iya tuk'i"

"Uhum shiya koya min, kuma wallahi na iya, zo mu je ki d'ana sabon motata da Uncle ya siya min na zuwa makaranta"

"Kai masha Allah, Allah ya sanya alkhairi, muje na gani"

Haka suka fita haraban gidan ta bud'e mata tana gani, Momy ta yaba sosai da motar, ta yi mata Addu'a.

"Gaskiya na ji dad'i sosai dota Allah ya yiwa my Son Albarka"

Husna tana mirmushi ta amsa da amin, Momy Zee ta ce.

"Wani course zaki karanta?"

Husna ta kanne ido d'aya ta ce.

"Pharmacy nake so"

Momy zee ta zaro ido cikin wasa ta ce.

"Gasa kike yi dani ko?"

Husna  ta kwashe da dariya.

"Haba Mom in rasa wanda zanyi gasa da shi sai ke, kawai ina so ne saboda tun ina k'arama nake son shi a raina"

"To shi kenan, Allah ya taimaka ya bada sa'a, ita Khadija fa?"

"Eh tare zamu rik'a zuwa, ita biochemistry zata karanta"

"To masha Allah, Allah ya Baku sa'a"

"Ameen Mom"

Suka jera suna hira har suka shiga cikin falo, suka zauna tare da cigaba da hira gwanin ban sha'awa.

Momy Habe tana d'aki ta zabga tagumi abin duniya ya isheta, TV na kunne yana aiki amma bata iya gane mai ake yi ba, saboda ta fad'a duniyar tunani, tashan liberty tv ne suna nuna labarai, gawarwakin mutane uku a ka nuna duk maza da alama ana cigiyar ko za a samu 'yan uwansu, kamar ance Momy ta kalli TV, haka nan taji fad'uwar gaba ta kurawa tv ido, bata iya fahimtar me suke cewa illa bin gawarwakin da ta yi da kallo, wani zabura ta yi ta murza idonta da hannunta domin ta tabbatar da abin da take gani, ilai abin da ta gani gaskiya ne babu karya a ciki Nura ta gani kwance cikin jini ba rai, hannu ta aza akai ta tsandara wani wawan k'ara, wanda duk yake gidan nan sai da yaji, a gigice Momy Zee da Husna suka rankaya zuwa d'akin Momy Habee, cike da kad'uwa Momy Zee ta ce.

"Hajiya lafiya?"

Kuka take rusawa tare da nuna musu tv da hannunta, bin tv suka yi da kallo, Husna na arba da hoton fuskar Nura ta ji kamar an cikareta, ita ma kuka ta fashe da shi tana fad'in.

"Momy Ya Nura ne, innalillahi wa inna ilai hir rajiun, yaya Nura ne"

Da gudu ta fita falo duk su Momy suka rufa mata baya, wayarta ta d'auka ta shiga kiran Dady, bugu d'aya ya d'auka ya kara a kunne ya ce.

"My sweet dota"

Kukanta da yaji shi ne ya hana shi k'arasa maganar da zai yi cike da kad'uwa ya ce.

"Husnah lafiya?"

Cikin kuka ta ce.

"Dady yaya Nura ya mutu yanzu aka nuna a TV"

Gabansa ne yaji ya fad'i, ya mik'e cikin sauri.

"Wani asibiti suka ce yake"

"Asibitin Murtala"

Bata jira mai zai ce ba ta kashe waya.

Kan a ce miye dangi da mak'ota sun samu labarin mutuwar Nura, gidan ya soma cika da mutane. Cikin k'ank'anin lokaci a asibiti aka bama su Dady gawar Nura suka dawo gida aka yi masa sutura, Momy ne zuk'unne gaban gawar tana kuka mai ban tausayi, hatta Dady a yau yaji tausayinta ta ce.

"Nura kaine kad'ai kwai na a Duniya, ga shi ka tafi ka barni a lokacin da nake buk'atarka, ina tsoron had'uwata da Allah da kuma mahaifinka saboda ban baka yarbiyya na kwarai ba, kaitsona na zamo nurasar uwa mara tsoron Allah, hak'ik'a alhakin Husna ce ya ke bibiyata, Allah ya gafarta maka yasa ka yi mutuwar shahada, d'a na ka yafe ni"

Wata 'yar uwanta ne ta dafata tana bata hak'uri cike da tausayawa, haka aka d'auke shi Momy Habee tana ihu had'e da sambatu marasa kangado. Ankai Nura makwancinsa an barshi da halinsa, tom mu dai sai muce Allah ya jikan duk kan musulmi Ameen.

******

*Bayan kwana bakwai*

Anyi sadakar bakwai kowa ka ganshi yana jimamin mutuwar Nura, domin labari ya ishe kowa akan hanyan da ya mutu. Sun je club ne sunyi shaye- shayen kayan maye sunyi tatil, tsautsayi bata wuce ranar ta, wani a cikin abokansu ya ce su zo suje wani club akwai wata kawarsa tana birthday, cikin maye suka shiga mota dan suje su hole da mata, motan ne ta kubcewa mai tuk'asu suka fad'a wani rami, dukansu babu wanda ya shura suka ce ga garinku nan, jami'an tsaro sun kawo musu d'auki, ko da aka kaisu asibiti sun riga sun mutu. Dan haka kowa ke tausayawa ake musu fatan samun Rahma, Momy Habee har wata k'aramar hauka ta yi da kyar aka samu ta daina kuka, da yamma 'yan uwanta suka tattarata suka wuce da ita gidansu, gaba d'aya Momy ta zama abin tausayi ta zama shuru-shuru, magana sai ya zama dole take yi, nadama kam Momy ta na cikinsa a kullun Addu'a take Allah ya gafartwa Nura ya yafe mata kura-kuran data aikata.

****** **** ******

Bayan Addu'ar arba'in 'yan uwanta suka zo suka kwashe kayanta duka domin ta k'arasa iddanta a gidansu, ta yi sallama dasu Momy Zee da Dady, Dady ya bata mak'udan kud'i danta juya su in kuma wani bukata ta taso mata ta zo ta same shi insha Allah zai taimaka mata, da godiya cike da jin kunya ta tafi.

*********

*Bayan wata d'aya*

Momy Zee ta soma laulayi abu kamar wasa Momy Zee da ciki, farin ciki wurin Dady baya misaltuwa, ita ko kunya taji wai da girmanta tana da ciki, Dady yana ta mata dariya da zolaya.

"Ai da sauranki ma a haihuwa dan baki gama ba ki shirya jero min 'ya'ya tagwaye say uku"

"Dear ka rufa min asiri, Husna da Al'amin sun ishe ni"

Da yake little Al'amin ya dawo nan Kano, Dady ya rok'a a basu shi ya zauna wajensu.

Ta b'angaren amare suma duk sun kamu suna da ciki, Husna ce dai abun shuru tana ta karatunta. Anty Binta ma Allah ya amshi Addu'arsu ita ma ta samu ciki, farin jiki wajensu ita da mijinta Mustapha baya misaltuwa, haka dangi sunyi san barka da Addu'an duk Allah ya saukesu lafiya.

******

Cikin Momy Zee na wata shiga Husna ta soma laulayi, su Khadija suma suna ta ja da cikinsu suma da yake wata shiga nasu yake, da Zahra ma, Anty Binta ne mai cikin wata biyar. Tun da Sadiq yaji Husna na da ciki ya soma nan-nan da ita kulawa ta musamman komai shi ke mata hatta wanka, makaranta kuwa shi ke kaisu ya dawo dasu. Yasir shima ba baya ba dan shima Khadija tana samun kulawa ta wajensa, ta bangaren Dady kuwa abin ba'a cewa komai.

Momy bayan ta gama Idda ta auri wani Dattijo mai Suna Alh. Tukur lecturer ne, kuma cikin ikon Allah ta natsu a d'akinta suna zaman lafiya da mijinta, matsala d'aya take samu wajen kishiyarta da yaranta, amma dai tana hakuri tare da kau da kai bata kulata, kishiyar nata ganin ga yadda Momy Habee take bata kulata sai ta sauko suka cigaba da zama lafiya da mutunta juna. Takan kawowa Momy Zee ziyara dan yanzu suna zumunci.

Ta b'angren gidan Abokin Dady Alh. Ahmad, zumunci ya kullu da Momy Halima da Momy Zee, sun zama kawaye sosai, Auren Minal da Mujaheed abokinsu Yasir, ya taso su Momy Zee dasu aka sha biki, su Husna da Khadija sune kawayen amarya, ita ma ta tare a gidanta mai kyau suka angonce abin sha'awa.

*******

Cikin Momy Zee ya shiga wata tara da sati d'aya ta haihu 'yan biyu duk maza, farin ciki kamar me a wajen Dady, Momy ta ga So da K'auna a gurin Dady, da kansa yake zama ya bata abinci ya taya ta kula da yara, har hutu ya d'auka a wajen aiki. Husna da Sadiq kuwa farin ciki a wajensu baya misaltuwa ita ma tarewa ta yi a gidan tunda aka yi haiguwar. Ta b'angaren dangi kuwa suma ba baya ba 'yan Kaduna sai zarya suke na zuwa barka, Ammi Jidda, Mimi Amina, Anty Binta duk sun zo ana saura kwana biyu suna, su Inna suna ta karb'an baki, Baba Husain har kuka ya yi ya ce.

"Ashe zanga takwarana"

Ya tuna da d'an uwansa mahaifin Khalil daya rasu suma 'yan biyu ne, shi ya yiwa yaran hud'uba aka bar musu sunansu Hassan da  Husaini, ranar suna an ci an sha, su Momy Habee harda

kayan barka ta kawo, Zahra tana cen bata samu zuwa ba domin tana gab da haihuwa. Haka Khadija ita ma ta zo suna amma bata iya komai zaune take da tsohon ciki turus, Husna sai tsiya take mata, Husna ita ma cikinta ya fita tana wata na shida ya yi mata das a jiki, ta k'ara kyau Sadiq kamar ya lasheta dan So. Anci suna an watse koya ya koma gida an bar mai jego da yaranta da Dady mai taya ta raino. Inna ce ke kula da mai jego ta bangaren wanka dana yara.

***

Bayan sati d'aya da suna, Zahra ta haihu 'ya Mace mai kyau ta yi kama da ita, ranar suna yarinya ta ci sunan mahaifiyar mijinta Aisha suna kiranta da Nasreen, anci ansha an washe taro lafiya. Bayan sunan Zahra da kwana biyu Khadija ta haihu itama an samu d'a Namiji, murna wajen Yasir ba a cewa komai Momyn sa ta yi murna sosai da 'yan uwa gaba d'aya, daga Asibiti aka wuce da ita gidansu Dady, part d'in Inna a can zata zauna, Inna na kulawa da ita har ta yi arba'in, Yasir bai so haka ba amma ya ya iya tunda anfi k'arfinsa, mutanan Kaduna nata zuwa barka, wannan karan harda Baffa ya zo ganin yaro da kuma 'yan biyun Momy Zee, Umma ma ta zo sai da a ka yi suna ta koma, Ranar suna yaro ya ci sunan mahaifin Yasir wato Muhammad Auwal suna kiransa da Na'im, anyi taro lafiya an watse kowa ya koma gidansa.

******     ******

*Bayan kwana arba'in*

Su Khadija sun yi arba'in, Inna ta gyara ta sosai ta koma gidanta, Momy Zee ita ma ta yi arbain da sati biyu kenan ta cigaba da kula da mijinta da yaranta, su Inna kusan yaran wurin su suke yini, sai suna buk'atar nono ne ake kai mata su.
Anty Binta itama ta haihuwa ta samu Namiji yaro mai kyau mai kama da Babanshi, ranar suna yaro ya ci sunan Baffa wato Ahmad suna kiransa da khalifa, anyi suna an waste lafiya. Haka dai rayuwa ya cigaba da tafiya, wannan dangi suna cikin farin ciki da K'aunar juna.

***

*Bayan wata uku*

Da haihuwar su Momy Zee, Cikin Husna ya kai wata tara da kwanaki, ranar juma'a da yamma ta fara nak'uda, Sadiq yana tambayarta lafiya? ganin yadda take ya mutsa fuska, amma tana cewa ba komai, da abin yazo gadan-gadan wani kuka ta barke da shi tana wash, Sadiq da sauri ya d'auketa ya sanyata a mota sai asibiti. Bayan Sallar magrib ta haihu 'yan biyu Mace da Namiji. Zo kuga murna wajen Sadiq kamar zai mai da Husna cikinsa dan murna, harda kukan farin ciki ya yi. Daga asibiti gida aka wuce da ita aka dire ta part d'in Inna, kan kace miye dangi na kusa zun soma zuwa barka cikin dare, harda su Momy Habee a 'yan barkan dare, little Al'amin kuwa yana mak'ale da gadon yaran sai murna yake ya samu abokan hira, mutanan Kaduna da sassafe suka kamo hanya Ammi Jidda ne kawai suka bari a gida irin ta yi kunyar d'an fari, Umma ko da ita aka zo dan sai anyi suna zata tafi, wannan karan su Zahra da su a kaci suna suma goye 'ya'yansu gwanin sha'awa sunyi bul-bul. Ranar suna yara suka ci sunansu Hassan da Husaina, suna kiransu Amir da Amira, anyi shagali sosai. Sadiq har wata 'yar walima

ya had'a a wani hol, Malamai biyu aka kira suka yi wa'azi akan *Tarbiyyan yara A Musulunci*, bayan an gama wa'azi aka ci aka sha. can na hango matan *sirrin 'ya mace* suna cin rengem, gaskiya kuna da zuminci domin kun yiw Husna kara da Uncle Sadiq. Allah ya kara zumunci Ameen. Lol😊
[11/6, 8:28 PM] Rahma Kabir🌺: *_Page 69 ~ 70_*

_Karshe_

*Wannan page din kyauta ce gare ku masoyan wannan littafi, Allah ya bar zumunci ya bar kauna. Ina muku so d'aya tak mara algush.♥✨*

Bayan Husna ta yi arba'in sai da ta kuma wata d'aya, a lokacin yaran sun k'ara kwari kafin aka d'auketa sai gidan mijinta, da mai taya ta raino Mama Jimmai mai yi musu aiki, domin Husna ta ce bata son kowa sai ita, dole aka bata ita su kuma su Momy Zee suka samo sabuwa.

An zarce da su sabon gidanta da Sadiq ya gina, babban filat mai kyau, Husna da mamaki take kallonsu tana son magana amma sai ta yi shuru tana tunanin kila zasu biya wani waje ne, hon Sadiq ya yi mai gadi ya bud'e musu ya shiga ya yi parking wajen parking space, mai gadi ya rugo da gudu yana ma Sadiq sannu da zuwa, kayansu ya d'auka ya yi ta shiga dasu, da mamaki Husna take binsu da kallo har suka gama shiga da kayan, Sadiq yana mata murmushi ya d'aga mata gira.

"Madam mu shiga ko"

Ba musu tabi bayansa tana rik'e da Amira, Mama Jimmai na rik'e da Amir, suna shiga Husna tabi falon da kallo tana santinsa.

"Wow gaskiya gidan nan ya had'u tsarinsa ya min"

Sadiq ya yi dariya Sadiq yana kallonta.

"Ga key d'in, gidanki ne"

Husna tsalle ta yi ta rungume shi da yake ta kwantar da Amira a kujera, shima rungume ta ya yi tsam a jikinsa kana ya d'auketa cak ya wuce da ita bedroom d'insa, Mama Jimmai ta bisu da murmushi da alama sun manta tana falon, yaran ta gyarawa kwanci ta kunna TV ta soma kallo. su Sadiq kuwa sabon soyayya ce ta b'arke, suka shiga tarairayen juna saboda tsabar missing d'in da suka wa juna, tuni salon ya canza nan na fito na basu guri.

Bayan komai ya lafa suka filo cikin sabon shiga Husna sai sunna kai take k'asa wai tana kunyar Mama Jimmai sai yanzu ta tuna da ita, Sadiq ya nunawa Mama Jimmai d'akinta dake cikin falon, d'akine mai d'auko da gado da Waldrop da bayi a ciki, Jimmai ta jinjina wannan karramawa da suka mata nan ta yi godiya suka barta. Sadiq ya nunawa Husna nata sannan

suka koma part d'insa mai dauke da k'aramin falo da d'akuna biyu a ciki nata d'aya na shi d'aya, sannan a nan babban falo a kwai nashi da nata ma, komai ya yiwa Husna kyau.

Bayan kwana biyu da dawowarta, ya kai ta gidan Yasir da shima ya dawo kusa da gidansu, duk in da Sadiq yake yana biye da shi kamar bindi, ganin Sadiq yana ginin gidansa yasa shima ya siya filin kusa dana Sadiq din ya soma gini, sun gama kusan lokaci daya sai ya riga shi tarewa saboda Husna tana gida wanka. Mak'ota suke ginin na jikin juna, akwai k'aramar k'ofa a tsakani wanda zasu sadu da juna ba lallai sai sun fita ta gate ba kan suje gidan juna, kusan gininsu iri d'aya ne, Khadija taji dad'in ganin su suka sha hira, sannan ta nunawa Husna yadda gidan nasu yake, sai dare suka koma gidansu.

*******

Su Husna an cigaba da karatu ga yaransu sun k'ara girma da wayo, soyayya tsakaninta da mijinta kuwa sai abin da ya yi gaba.

Ta bangaren Dady kuwa ya yi retire ya soma business d'in motoci inda ya bude sabon company mai suna Al'amin motor's limited, yana shigowa dasu daga k'asashen waje, arziki yaci uban na da. babban Pharmacy ya bud'ewa Momy Zee mai suna Zainab pharmacy, wanda suke sarar da magani ga k'ananan 'yan kasuwa, tana zuwa aikinta su Hassan sun yi wayo sosai, wajen su Inna take barinsu, haka Husna pharmacy dake Kaduna su Baffa suna ta kula mata da shi sai hab'aka yake.

Dady ya siyawa Baba mai gadi gida nan kusa dasu ya dawo da iyalinsa suna zumunci, sannan ya sanya shi cikin harkan company sa, sai suka samu sabon mai gadi ya cigaba da aikin Baba.

*******

Husna da Sadiq suna kallon tashar Sunnah TV, Sadiq na zaune kan kafet Husna ta d'aura kanta a bisa cinyarsa yana wasa da gashin kanta, Amir da Amira suna ta wasa, da yake sun fara zama har k'ok'arin ta shi suke yi yanzu, Sadiq ya ce.

"Sweet baby ina so in d'auki hutu na wata d'aya domin mu zaga k'asar waje dan shakatawa, amma me kika gani saboda karatunki?"

Cike da murna ta ce.

"Haskena, ka bari mu gama exam tun da mun kusa farawa, da mun samu Hutu sai mu tafi, amma ni nafi son mu tafi k'asa mai tsarki mu yi Umarah"

"Eh gaskiya kin kawo shawara mai kyau, to ya za mu yi dasu Amir?"

"Sai mu tafi dasu tare da Anty Jimmai"

Murmushi ya yi na gefen baki.

"Na so ki yayesu kawai mu tafi mu biyu, amma tunda kin ce mu je dasu ba matsala"

"Wai, ai Uncle ba zan iya tafiya ba dasu ba dan basu isa iyaye ba"

"Uhum ni ko gani na yi ya dace a samo musu kwanuwa dan sun girma"

Husna ta zaro ido cike da tsoro.

"Haba dai Uncle wallahi tsoro nake ji dan haihuwa akwai wahala, ni su Amira ma sun ishe ni"

"Kai my Hussy, bafa wahala nishi d'aya za ki yi ki haihu, dan haka ina son yara da yawa sai ki shirya amsarsu"

Husna ta shagwab'e fuska.

"Ni fa bana so Uncle"

Yatsansa ya sanya akan lips d'inta.

"kar ki sake kira na da Uncle kin gane"

"Uncle tuna baya na yi"

Ya lakace mata hanci.

"Na sani, tsokana ce kawai irin naki"

Kafin ta yi magana ya rufe mata baki da na shi, suka tsunduma kogin masoya, cikin tak'aitaccen lokaci sun mance duniyar da suke ciki, kukan Amir suka ji kamar daga sama, a firgice ya saketa ya isa gunsa da sauri ya shiga liliya masa kansa in da ya buge, ya soma lallashinsa sannan ya yi shuru, Husna ta mik'e tana hamma ta d'auki Amira ta ce.

"Uncle"

Da sauri ta rufe bakinta tana fad'in.

"Au sorry baby, sweet hubby zance"

Murmushi ya yi ya ce.

"Zan kamaki ai, mu je mu kaisu gun Mama Jimmai, naga kin soma hamma da alama barci kike ji"

"Kamar kuwa ka sani"

Sun kai yaran wajen Anty Jimmai suka dawo part d'in Sadiq, suna shiga ta fad'a kan gado tare da gyara kwanciya.

"Me kike nufi? kima ta shi dan ba zaki yi barci yanzu ba sai kin min tausa"

"Kai hubby, barci nake ji fa"

Ta ce cikin shagwaba.

"Eh, za ki yi barci, amma fa zai mun kai ziyara k'asar masoya"

Dariya ta kwashe da shi, kan ta yi aune ya fad'a kan gadon ya tsafkota.

"Wa ki kewa dariya?"

Sai ta k'unshe sauran dariyan a bakinta, tama kasa magana, cakul kuli ya soma yi mata tana kwasar dariya, da kyar ta iya kwace kanta ta wurga masa pillow, daga nan kuma wasa ya sauya salo, tuni na fito d'akin na rufe musu k'ofa, to Sadiq da Husna a hau jirgin masoya lafiya.✈😌

*Karshe*

_Matasa mu sani duk kuskuren da muka aikata ya yin aure, tofa mu sani fa bamu kad'ai zaiwa illa ba hatta 'ya'yanmu zai shafa, mu rika aiki da tunanin abin da zai je ya dawo, kar so ya rufe mana ido mu tafka kuskure_

*Kuma Iyaye ku sani auren dole babu kyau a musulunci, in yaro ya ce bai so ga zabinsa, tofa mu tsaya mu duba muga shin wanda take so yana da nagarta da dabi'a mai kyau? in yana da shi sai a bata in kuma bai da shi sai a lallasheta a nuna mata illolinsa cikin lumana ba tare da takurawa ba, dan matsawa da takurawa shi ke haifar da tuburewar yaranmu suk'i yi mana biyayya. Allah yasa mu dace, Ameen.*

*A nan na kawo karashen wannan littafi mai Suna KAD'AICI. Allah ya bamu ikon ammani da abin da mukaranta dake ciki, ya kuma yafe mana bisa kuskuren dake ciki. Allah ya karemu da bata bayan shiriya. Sai kun jini a sabon buk dina mai suna SO SANADI❤😰*

Kamar yadda na sanar muku tsohon littafi ne na sabunta muku shi., shima so sanadi nayi shi da jimawa.

*Na sadaukar*
*_Da wanannan littafa ga group dina SIRRIN 'YA MACE_*

*_Gai suwa da ban girma ga masoya wannan littafin KAD'AICI, Allah ya saka da alkhairi yabar zumunci._*